Haka dai suka d’an tattauna, kafun daga bisani Abba da Baba Maud’o suka fice, haka shima Dr Sulaiman.

Acan b’angaren Jannart kuwa ahankali, ta murd’a handle din kofar ta shiga bakinta d’auke da sallama.

Kwance yake akan lallausan gadonsa, Yayinda yayi kwanciyarnan irin ta rub da ciki.

Jin sautin muryarta ne kuma yasa shi, lumshe idanunsa dake bud’e.

Ita kuwa Jannart k’arasa shigowa cikin d’akin tayi, tare da  ajiye tray din dake hannunta.

D’an Kallon yanda ya bawa kofar shigowa dakin baya tayi, cikin sanyi da kuma tausasa murya tace.

“Ga abincinka nan.”

“Nak’oshi.”
Ya fad’a atakaice saboda ayanzun Sam bayason takura.

“Katashi kaci abinci inji likita.”

Jannart din ta fad’a tana me bud’e food flask din, tare da d’aukan spoon ta zuba Coastarian breakfast dish din, gyara zaman plate din akan table tayi, tare da d’ago da Kanta ta kalleshi.

“Please ka tashi, Mamy ne tace kaci abinci sai kasha magani kaji ko.”

Tayi maganan cikin sanyin murya, da kuma zallan yanayin shagwab’an da ita kanta batasan tayi sa ba.

Idanunsa ya d’an rumtse ahankali, tare kuma da sa hannayensa duka biyu, ya sake matse pillow’n dake kirjinsa.

Kwata-kwata bayason yawan damuwa, bawai kuma dan bayajin yunwa ba, no kawai dai bayason yaga Jannart din akusa dashi har haka ne, musamman ayanzu daya fahimci wani abu, adangane da ita, shine tana da wani special Mood wanda yafahimci ita kanta batasan tana dashi ba tana kuwa yiwa zuciyarsa raraka.

Sake gyara kwanciyarsa yayi, cikin kuma nuna halin ko inkula yace.

“Kije zanci.”

Idanunta ta d’an zubawa faffadan bayansa, tare da kama waist dinta ta rik’e, dama tasan halinsa, ta kuma san cewar bazai tab’a daina wa ba.

“Nifa bawai na wani damu dakai bane, Dan kawai kaga Ina baka attention dina, saboda baka da lafiya ne kawai Malam, baya ga haka me mazaisa nazo wajenka.”

Ta fad’i hakan acikin zuciyarta, tare kuma da murgud’a bakinta gefe.

“Da kika tsuramin ido haka wani abu ne zaki bani? Ko cinyeni danye zakiyi!?”

Rayyern din ya fad’a, batare daya juyo ba.

Saurin kawar da kanta gefe tayi, tare da turo dan karamin bakinta gaba, cikin yanayin Mood din shagwab’a tace.

“Ni ai ba kallonka nake ba kuma ba kai nake kalloba”.

A hankali yace.
“Toh wa kike kallo”.

Baki ta ɗan turo.
“Ni babu”.

Dan gajeren tsaki yaja tare da cewa.
“Mayya”.
Yayi mgnar a hankali so batajiba.
Sai ta d’an kwab’e fuska tare da cewa.
“Kuma ni Mamy ce ta aikoni, Dan Allah katashi mana katashi ka tashhhhhi....”

Ta kare maganar tana slowdown da muryarta.

Hakan kuwa shiya sanya, Rayyern din d’an juyowa akaron farko ya kalleta.

Karab kuwa kyawawan idanunsu suka had’e acikin na juna, da sauri Jannart din ta kawar da kanta gefe.

Shidinma kuma janye kallonsa daga gareta yayi, inda ya sauke ganinsa akan Coastarian breakfast dish din.

Idanunsa ya d’an lumshe akasalance, kuma cikin muryarsa da tayi sanyi yace.

“Give me the water.”

Kallon d’an madaidacin bakinsa dake motsawa tayi, sai kuma Ta kau da kanta, tare da rusunawa ta zuba masa ruwan swan acikin cup.

Mik’a masa ruwan tayi.

Ganin hakanne kuma yasa shi d’an yunk’urowa ya zauna.

Karb’an cup din ruwan yayi, tare dayi masa kurb’i d’aya ya ajiye.

Kyawawan yatsun k’afarta ya zubawa ido, cikin sauk’e numfashi yace.

“Naji zanci amma ki tafi, nima zan iyaci da kaina, banason abunda za’amin wanda baikai zuci ba, dan ni bana son abun zuciya biyu da manufa.”

Ya k’are maganar still yana me Kallon yatsun k’afar nata.

Idanu Jannart din ta d’an tsura masa, saboda har yanzu tana mamakin wasu kalamai da yake yawan jifanta dasu, wanda batasan me hakan suke nufi ba ta dai fahimci tabbas bai yarda da ita bane zarginta yakeyi.

Pink lips dinta ta d'an turo, tare da soma motsasu tana mamul mamul dasu, tamkar dai Wacce takeson fad'an wani abu.

Lips din nata ya kalla, ganin yanda suke motsawa ne kuma yasa shi kauda kansa gefe.

"Da wani k'aramin bakinta kamar na tsuntsu."

Ya fad'i hakan acikin zuciyarsa, Yayinda afili kuwa idanunsa ya lumshe tare da cewa.
"Zagina kikeyi ko?".
Da sauri ta zaro ido tare da cewa.
"Ni dai a'a".
Kana ta juya, tana me wasa da y'an yatsun hannunta ta nufi hanyar fita daga cikin dakin.

Har takai bakin k'ofar d'akin nasa kuma saita tsaya tare da juyowa,  cikin sanyi da kuma muryar dake nuna lallashi tace.

"Kaci abincin dan Allah sai kasha magani."

Batare kuma da ta jira abunda zaice dinba ta fice daga cikin dakin tana mgnar zuci.
"Sherri kayan kolba, wannan ai yafi Yah Junaid neman sababi da hujja wai na zageshi".

Bayanta yabi da kallo harta fice din.
Idonsa ya lumshe tare da sauke wani irin sassayan numfashi,
Kana a hankali ya buɗe su,
Anutse ya jawo plate din abincin, cikin sanyi da kuma yanayi irin na marassa lafiya, ya soma dan tsakalan abincin.

Baiwani ci sosai ba kuma ya ture plate din gefe, tare da d'aukan tea yasha,  bayan yasha tea dinne kuma ya b'alli magungunansa yasha.

Yanasha kuwa ya koma ya kwanta.

Jannart kuwa Koda ta sauk'a k'asa, Bata samu Mamy ba, Riyyam nsra kawai ta samu, da shidinne kuma suka sha hira, kafun daga bisani kowannensu ya tashi ya tafi.

Alhamdulillah yau kwanan su Rayyern, uku da dawowa daga China, Masha Allah kuma ciwon cikin nasa yayi sauki sosai, saidai jikin nasa ne baigama samun karfi ba, har yanzu.

Kulawa kuwa yana samunshi sosai daga wajen ahalin nasa, Abba, Baba Maud'o, Mamy, Ramadan Riyyam, da kuma Dr. Sulaeman harma da Usman P.A duk suna iyaka kokarinsu wajen bashi kulawa, saidai kuma har yanzu bai iyacin abinci sosai.

Wanda kuma hakan al'adarsa ce ta tuntuni.

Yau ne kuma Barrister Kabir da kuma Dr Sajo suka shirya musamman dan zuwa duba Rayyern din.

Koda suka Iso gidan tarba na musamman, Abba da Mamy sukayi musu, bayan sun gaisa dasu Mamy da Jannart ne, Abba yayi musu jagora zuwa  part din Rayyern din.

Koda sukaje akwance suka iske shi, duk da cewar bayajin karfin jikinsa, amma daya gansu ya d'an sake sunyi hira.

Yanzun kuma saukowarsu k'asa kenan.

Dr Sajo ne ya kalli Abba, cikin kulawa yace.

"Amma Alhaji Bashir me zai hana baza'a sake maida Rayyern din, hospital ba tunda naga har yanzu jikin nasa bawani karfi sosai."

Mamy dake zaune acikin falonne, ta d'an gyara zamanta, tare da fuskantar Dr Sajon, cikin bayyana damuwarta tace.

"Ai bawai wani abune matsalar ba, bayason cin abinci ne kwata kwata, komai aka basa sai yace a'a, Koda an matsa masa kuwa, bai wuce yayi loma biyu ko uku ba, sai yace ya koshi, bashi da wani abinci sai tea, nan ma yanzu ne yake d'an shan tea din da madara, da bayason ko madaran saidai empty, shiyasa bayi da karfin jiki."

Kai Dr Sajo ya jinjina, cikin gamsuwa yace.

"Eh to kin san dama duk inda dan adam yayi ciwo abinci yake fara tsana.
Tabbas kuwa bazai samu wadataccen karfin jiki ba, harsai in ya dage da cin abinci, amma ana tambayansa ko yana da buk'atar wani abu, sai anayi masa."

"To."
Mamyn tace.

Yayinda Abba kuwa cewa yayi.

"Idan naga abun nasa yaki karewa ai, dolensa na daukesa na maidashi hospital, yasan duk wani illar rashin cin abinci, amatsayinsa na Dr amma baya kiyayewa."

"Hakane kam sai hakuri da majinyaci, Allah dai ya bashi lafiya."

Cewar Barrister Kabir.

Da “Ameen.” Duk suka amsa.

Basu wani jima ba kuma, Abba yayi musu rakiya suka tafi.

Bayan suntafi dinne kuma Mamy ta haura saman.

Azaune tasa meshi yasaka Laptop d’insa agaba, yana Dan lallatsata.

“Rayyern.”
Mamy takira sunansa da kulawa.

Jin sautin muryar Mamyn nasa ne kuma yasashi d’ago kansa Ahankali ya kalleta.

“Na’am Mamy.”
Ya amsa adan kasalance.

Karasa shigowa cikin dakin Mamyn tayi, tare da matsowa kusa dashi, cikin kulawa da kuma nuna tausayawa agareshi tace.

“Meyasa ne haka Babana? Meyasa kwata kwata bakason cin abinci? kasani fa bazaka samu isashshen karfi ba, har sai inkana cin abinci, yanzu fad’amin mekakeson ci, ko meye saina dafa maka.”

Fuskarsa yad’an kwabe tare da marairaicewa.

Cikin yanayin sakalci yace.

“Nifa Mamy bana sha’awan komai, kawai dai abincin yanzunne baya min, nafison abu me d’an melting da kuma tsami, like Chinese dishes dai, ko Mamy amin irin kunun ranan.”

Ya k’are maganan yana langwabar da kansa gefe.

Murmushi Mamy tayi tare da cewa.

“To za’ayi maka kunun kaji kada ka damu.”

Mamyn ta fad’a tare da juyawa ta fice daga cikin dakin.

Direct kasa Mamyn ta sauk’o, inda ta samu Jannart ta gaya mata, cewar Rayyern yana son ayi masa irin kunun ranar.

“To.” Jannart din tace, babu musu kuwa ta wuce kitchine, Anutse ta soma had’a kunun kamar yanda ya buk’ata.

Tsab ta gama had’a kunun, da yayi kyau sai tashin kamshi yake, juye kunun acikin flask tayi, tare da daura flask din akan tray ta daura cups agefe, sai kuma madara da zuma wanda suke cikin wani abu mai kaman glass.

Fitowa falo tayi rike da tray din ahannunta.

Mamy dake zaune afalon kuwa Ganin Jannart din harta kammala ne yasa, cikin jin dadi tace.

“Masha Allah Jannart har kin kammala, Allah Dai yayi miki albarka, ki kai masa nasan yana nan yana jira.”

Murmushi Jannart din tayi, tare kuma da dan sunkuyar da kanta, cikin nutsuwa ta nufi saman.

Tafiya take Ahankali, Yayinda tayi kyau cikin riga da wandon pallazon dake jikinta, wanda ta yafa mayafi. Dan babba akan shigar nata, saidai duk da hakan ga wanda yayi mata Kallon k’urulla, tsab zai iya hango tsararren cikakken hips dinta.

Ga kuma rigar shirt din da yayi mata cibcib ajikinta, cikin tan nan alafe yake, tamkar babu hanji acikinsa.

Karasowa bakin kofar falon nasa da tayi ne kuma yasa ta, tura kofar ahankali, bakinta dauke da sallama ta kutsa kanta ciki.

Babu kowa acikin falon hakane yasa ta nufi, Bedroom nashi,
a hankali ta tura ƙofar tare da sallama a bakinta.
Still nan ɗin ma babu shi,
Cikin mamaki ta ɗan ware idanunta tare da jujjuya kanta, tana mai kasa kunne wai ko zata jiyo mostinsa a Bathroom,
jin shirune ba motsin komai, harta nufi kofar dakin dan fitowa falon nasa ne kuma, saita hangosa zaune acikin wani balcony wanda labulayensa keta kaduwa saboda iska.

Kaitsaye wajen ta nufa tana isa wajen kuwa, idanunta suka sauka akansa.
Da sauri tayi kasa da kanta, saboda ganinsa ahaka da tayi, domin yau dinma ba wani kayan kirki bane ajikinsa, singlet ne da kuma gajeren wando.

Shikuwa Rayyern jin sallamanta ne yasashi dago kansa, ya sauke idanunsa akanta.

Tashin farko kuwa idanunsa suka sauka, akan lafaffen cikinta, wanda ta daure kasansa da adon igiyan wandon dake jikinta.

Janye idanunsa yayi daga Kallon nata, tare da maida kallonsa gefe.

Anutse ta karasa isowa inda yake, tare da Dan dukawa ta ajiye tray din dake hannunta.

Cup ta d’auka tare da zuba masa kunun, kana ta saka masa madara da zuma aciki.

D’an d’agowa da kanta tayi, hade da mik’a masa cup din.

Cikin sanyi tace.

“Gashi.”

Tayi maganan tana me sauke idanunta, akan lallausan beard d’insa. Wanda yake matukar yi mata kyau.

Ahankali ya juyo da kallonsa zuwa gareta,  lokaci daya kuma ya sauke idanunsa akan kyakkyawar fuskarta, da kuma dan karamin lips dinta, dake shining din lipgloss.

Hannunsa yasa ya karb’i cup din, Ahankali kuma ya dan motsa lips d’insa,  saidai kuma ita kanta bataji mai ya fad’a ba.

Kan Wani had’add’en rug dake gefensa ta zauna, tare kuma da rike flask din ahannunta.

Saurin kallonta yayi, saboda baiyi tunanin zama zatayi ba, kamar zaice wani abu kuma sai ya fasa,Ahankali kuma ya janye idanunsa da suka sauka akan waist dinta.

Cikin nutsuwa ya soma sipping kunun, yana me lumshe idanunsa saboda yanda yakejin dadin kunun.

Itakuwa Jannart gaba daya kallonta ta mayar k’asa, inda take hango Riyyam-nsra da Baba Maud’o wayanda suke zaune abakin gate.

Kallonsu takeyi sosai, musamman ayanzu da taga Riyyam din na waya,  ba tare da taga ya jima yana wayan ba kuma ya mikawa Baba Maud’o.

Hannayenta duka biyu ta had’e tana kallonsu.

Yayinda acan kasan kuwa.

Mammy ce takira tana tambayan Riyyam din jikin Rayyern .

Nan Riyyam din yake shaida mata cewar jikin da sauki,  Koda ta nemi ta gaisa da Rayyern

dinne kuma, Riyyam yake sanar mata cewa, baya kusa da Hamma Rayyern din,  ananne kuma Riyyam din yace.

“Mammy  Ina tare da Baba Maud’o bari na bashi ku gaisa.”

“To.” Mammyn tace.

Yayinda Riyyam-nsra kuwa ya mikawa Baba Maud’o wayar.

Karb’an wayan Baba Maud’o yayi tare kuma da karata akan kunnensa, Cikin nutsuwa yace.

“Assalamu Alaikum.”

Acan Ethiopian kuwa Mammy dake zaune akan kujera, Jin amo da kuma sautin muryar daya daki dodon kunnenta ne, yasa taji zuciyarta tayi wani irin bugawa, take kuma tsikar jikinta suka shiga wani irin mimmikewa, cikin wani irin yanayi ta mik’e tsaye, tare da sake sauraran muryar dake kan wayar.

“Assalamu Alaikum.”

Baba Maud’o ya sake maimaita sallaman nasan, saboda Jin shiru da yayi.

Komawa Mamyn tayi ta zauna, tare kuma da sanya hannu ta dafe kirjinta, cikin rawar murya tace.

“Wa’alaikassama.”

Zumbur haka Baba Maud’o ya mik’e tsaye daga zaunen da yake, tare kuma da d’an zazzaro idanunsa waje,  lokaci daya wani irin yanayi ya bayyana atattare da Baba Maud’on.

Wanda hakan yasa Riyyam dake zaune kallon Baba Maud’on, Cikin yanayin mamaki yace.

“Baba Maud’o lafiya?”

Kallonsa Baba Maud’on yayi, tare kuma da komawa Ahankali ya zauna, saidai kuma har yanzu jikinsa bai daina tsuma ba.

Daga can b’angaren kuwa cikin rawar murya Mammy tace.

“Ina wuni, ya maijiki?”

Hannu Baba Maud’on ya d’an dunkule cikin wani irin abu dake dukan zuciyarsa yace.

“Lafiya mai jiki kuma Alhamdulillah.”

“Masha Allah Allah ya kara sauki, mungode sosai Baba Maud’o nasan kuna nan kuna fama da rigiman Riyyam, Allah ya bada lada.”

Mammyn ta fad’a cikin sanyin murya.

Baba Maud’o kuwa murmushi ya aro ya sakawa muryarsa, kana shima cikin sanyi yace.

“Ameen summa Ameen, ai Riyyam kam babu wani rigiman da yake yi mana, harma mun saba dashi kwannan yana ta cewa kin matsa ya komo mu kuma bamu son rabuwa dashi.”

Murmushi Mammyn tayi, cikin kuma karfin hali da danne bugun zuciyar da takeji, tace.

“Shikenan to Baba Maud’o ahuta gajiya.”

“Yauwa.”
Baba Maud’on ya amsa, tare da zare wayar akan kunnensa, cikin sanyi da kuma wani irin tunani dake dukan, kwakwalwarsa ya mikawa Riyyam nsra wayan.

Karb’an wayan Riyyam-nsra yayi tare da Karawa akan kunnensa.

Jin muryar Riyyam dinne kuma yasa, Mammy sauke wani irin nannauyar Ajiyar zuciya.

Cikin sanyi tace.

“Riyyam ka had’ani video call da Rayyern, inason naga ya yanayin jikin nasa.”

“To Mammy zan hadaku amma maybe sai gobe, saboda nasan yanzu haka yana sama, kuma Idan magriba ta kusa bayason yawan magana.”
Riyyam din ya fada atausashe.

Daga can b’angaren kuwa Kai Mammy ta jinjina, tare da cewa.

“Shikenan to badamuwa Allah ya kaimu goben.”

“Ameen”
Riyyam din ya amsa kana sukayi sallama da Mamyn.

Duk abunnan da sukeyi kuwa Jannart na kallonsu, saboda gaba daya hankalinta ya tafi garesu ne ma, yasa har yanzun take nan bata tafi ba.

Shikuwa Rayyern tuni ya shanye kunun da ta zuba masa din tas.
Ganin bata da niyan kara masa ne kuma yasa shi, dagowa ya kalleta.

Akaron farko kenan daya tsaya ya k'are mata kallo, idanunsa ya dan tsayar akan fuskarta, saboda yanda yaga hankalinta ya tafi izuwa wani waje na daban.

Ajiye cup din dake hannun nasa yayi, Karan ajiye cup dinnasa ne kuma yasa hankalinta dawowa garesa.

Ahankali ta juyo da kanta zuwa garesa, karab kuwa idanunsu suka sarke acikin na juna.

Sunkuyar da kanta k'asa tayi, tare da sauke numfashi, cikin silent voice dinta tace.

"Nak'ara maka ne?"

Kansa ya d'an girgiza mata, tare da lumshe idanunsa, cikin wani irin yanayin daya saka zuciyarta harbawa yace.

"Um um nakoshi." yayi mgnar yana jin dadi bakinsa yayi masa wasai yawunsa ya sinke alamar dandanon bakinsa zai dawo.

Kallonsa tayi, haka kuma shid'inma.

Kasa tayi da Idanunta tare da matsowa ta durk'usa, tray din ta ke kokarin dauka.

Dan kusancin da sukayi ne kuma yasa, daddad'an kamshin turarenta ratsa cikin hancinsa.

Idanunsa ya dan lumshe, Yayinda itakuwa tray din ta dauka Anutse ta juya ta tafi.

Kaitsaye kasa ta sauka, bayan takai kayan kitchine ne kuma ta wuce dakinta.

Shikuwa Rayyern kiran Sallan magriba ne ya tadashi awajen.

Washegari.

Yau dinma kunun da Jannart din tayi masa jiya ya kuma sha, sai kuma abu mai romo da Mamy tasa ta dafa masa, babu laifi kuma yaci sosai.

After 3days.

Mamy ce tsaye agefensa, Yayinda shikuwa ke zaune akan daya daga cikin kujerun falon.

Murmushi Mamyn tayi tare da dubansa cikin danjin dadi.

Tace.

“Masha Allah Babana Lallai jiki yayi sauki, tunda har ka iya fitowa  falo.”

Murmushi ya d’anyi tare da Kallon Mamyn nasa, cikin sanyi yace.

“Mamy yunwa nakeji sosai, kuma nafison abu mai dan tsami, please Mamy roasted fish da ruwan lemon tsami nakeso, ko kuma miyan da akayi ranan nan pls Mamy.”

Murmushi Mamyn tayi tare da cewa.

“To Rayyern amma ni bansan yanda akeyin miyan ba, rannan ma bani nayi ba Jannart ce tayi, amma bari na turo maka ita saikayi mata bayani.”

Fuskarsa yadan kwabe cikin shagwaba yace.

“Eyyah Mamy kifada mata mana, dole sai ni?”

“Eh mana bakaine kakeso ba.”

Mamyn ta fad’a tana me nufar dakin Jannart.

Ramadan dake zaune agefe kuwa, Kallon Hamman nasa yayi, tare da mik’o masa magungunan daya b’are.

Cikin kulawa yace.

“Please Hamma Rayyern karb’a maganinka kasha.”

Fuskarsa yadan yamutsa, kamar zaice a’a sai kuma ya karba yasha.

Bayan yasha maganin ne kuma Ramadan ya Mike ya tafi, domin dama hospital zai tafi, ya tsaya bawa Hamman nasa maganine.

Already Abba kuma dama ya tafi company, Riyyam-nsra kuwa yana waje .

Jannart kuwa dake falon ta zaune take, inda tayi kyau cikin wani fitted gown na maroon lace dake jikinta, sosai rigar tabi jikinta ta zauna, saboda yanda dinkin ya fita sosai.

Bak'aramin kyau yau Jannart din tayi ba, musamman da ta watsa jelan  gashinta haka bata kitseshiba, tare dasa dan siririn mayafi daga kanta zuwa kirjinta.

Shigowar Mamy ne kuma yasa ta d'agowa, fuskarta dauke da murmushi.

Itama Mamyn murmushi tayi, tare kuma da Kallon Jannart din Cikin kulawa tace.

“Jannart kije mijinki yana kiranki.”

Kai Jannart din ta d'an sunkuyar kasa, cikin sanyi kuma tace.

“To.”

Juyawa Mamyn tayi ta tafi, Ganin hakanne kuma yasa Jannart din mikewa, Cikin yanayin nutsuwarta ta nufi part din nasa.

Ahankali ta murd'a handle din kofar ta shiga, bakinta dauke da sallama.

Saidai kuma dan ja baya tayi, ganinsa da tayi yana waya, hakan yasa ta matsawa jikin kujera ta d'an zauna, wanda hakan yasa suka zama suna fuskantar juna.

Ahankali ta dan saci kallonsa, musamman yanda taga yayi kyau cikin shigar riga da wandon DG dake jikinsa.

Ahankali ya ajiye wayar tare da d'ago kansa ya kalleta.

K'asa tayi da Idanunta, cikin sanyi tace.

“Ina kwana.”

Idanunsa ya sauke akan labbanta zuwa kan kirjinta, wanda dinkin jikin nata ya masifar fitar da shape din samansu.

Kauda kansa yayi batare da ya iya amsa mata ba

Itakuwa Jannart jin bai amsa mata dinbane yasa ta cewa.

“Ya jiki.”

“Da sauki.”

Ya amsa mata da wani irin murya, wanda yasa ta dago ta kalleshi.

Ahankali kuma tace.

“Gani Mamy tace kana kira na.”

Idanunsa ya dan marairaice cikin sanyin murya mai hade da zallan shagwab’a yace.

“Yunwa nakeji sosai, kibani abinci, but mai dan tsami kawai kinji....”

Yaja maganar tasa cikin wani irin yanayi, tare dasa hannunsa ya shafa cikinsa.

Hakan kuwa shiya sanya Jannart ta d’ago Kai ta kalleshi, lokaci daya kuma taji wani irin tausayinsa ya cika mata zuciya.

Ahankali Cikin yanayin ta itama dake kama da shagwab’a tace.

“To meye kakeso? Miya ko kuma abinci?.”

Idanunsa dake lumshewa ya rufe, tare da bud’e labb’an sa ahankali yace.

“I don’t know kimin komai kawai, ko miyan da kika tab’ayi ranan mai ɗan sami.”

“To.” Tace asanyaye tare da juyawa ta nufi hanyar fita.

Koda ta fito daga dakin nasa, Anutse ta soma sauka daga kan steps din.

Dai-dai lokacin kuma Riyyam-nsra yake haurowa saman, hannunsa rike da waya.

Ganin Jannart dinne kuma yasa shi sakin murmushi, Cikin kulawa yace.

“Good morning My Aunty ya jikin Hamma Rayyern.”

Murmushi tayi tare da dubansa, cikin sakin fuska tace.

“Jikinsa da sauki Riyyam, yanzu ma na sameshi afalo.”

Murmushi Riyyam din yayi tare da cewa.

“Masha Allah, bari naje na sameshi.”

Riyyam din ya fada, Yayinda ita kuwa Jannart kaitsaye kasa ta wuce, inda ta nufi kitchine Dan fara had’a masa abunda zaici.

Riyyam kuwa direct falon ya wuce, yana zuwa zuwa kuwa ya zauna akusa da Hamman nasa.

Tare da dan rankwafar dakai cikin sanyi, yace.

“Hamma Rayyern Mammy tanason yin magana dakai, tace kuyi video call saboda taga ya jikin naka, na kirata please?”

Idanunsa ya dan lumshe, akasalance kuma ya d’an gyad’awa Riyyam din Kai alaman “Eh.”

Murmushi Riyyam din yayi cikin, Jin dadi kuma ya zaro wayartasa tare da dannawa numbern Mammy kira video call.

Ring kadan kuwa wayar tayi Mammy ta d’aga.

Tana d’agawa kuwa Riyyam yayi murmushi, tare da Kallon Mammyn nasa Cikin kulawa yace.

“Mammyna Barka da safiya, ga Hamma Rayyern dinnan ku gaisa.”

Ya k’are maganan yana me mik’awa Rayyern din wayar.

Kasancewar kuma kan Rayyern din yana dan jingine ne yasa, Riyyam cewa.

“Hamma Rayyern ga wayan.”

Ahankali ya d’an juyo tare da kai dubansa ga fuskar wayar, wani irin bugawa yaji zuciyarsa tayi da karfi, wanda hakan ya sashi zabura tare da yunkurawa ya gyara zamansa, inda ya sauke ganinsa akan fuskar.........!

Littafin TUBALI dai na kuɗine ko kin gansa a wasu group ɗin na satane

By
*GARKUWAR FULANI*

22/12/2021, 19:45 - 🥰🥰: Tare da fuskantarsu dukansu, cikin dan nisawa yace.

“Gaba d’aya matsalarmu a kullum akan Dr Rayyern Bashir Muhammad Mai-nasara ne, wanda kuma ni kaina bani da iko, ko wani matsayi da zan iya dakatar dashi akan abunda ya saka agaba, saboda duk wani k’a’ida da dokokin da akebi ya bisu, Idan kuma har nace zan wargaza masa tsari.
To tabbas zai iya Kai k’arata wajen na sama dani, hakan kuma zai iya sawa na rasa aikina, yaron ya wuce duk yanda muke tunani, kowacce hanya da zamu b’ullo masa ya sani, kansa yana ja sosai, babban abunda na lura dashi kuma shine, kwata kwata baya tsoron magautansa yaron yana nan Tamkar a haifeshi ne domin daukan fansa!!!.”

Numfashi mai nauyi duk suka ja, musamman Alhaji Idi Sale Dakata wanda gaba daya abubuwa suka had’e masa.

Ga zafin b’atan Jannart ga kuma, na wannan shegen yaron Dr. Rayyern.
Barrister Kabir kuwa, kalaman Alhaji Bala Tambari na karshe yaketa nanatawa a zuciyarshi don son fahimtar wani abin.

Haka dai taron nasu ya watse gaba d’aya zuciyar Alhaji Idi, da kuma na Dr. Lukman Alhaji Abdu Tababa babu dadi, kowannensu kuma saboda Rayyern.

Dr. Lukman din, da kuma Alhaji Abdu Tababa ne suka had’a hanya wajen tafiya, haka ma Alhaji Bala Tambari shima tafiya yayi.

Hakan yasa falon ya rage daga, Daddy sai Barrister Kabir.

Juyowa Alhaji Idi Sale Dakata’n yayi? Ya fuskanci Barrister Kabir, cikin kuma nuna halin damuwa yace.

“Kabir ayanzu babu abunda yake damuna, kamar b’acewar Jannart, har yanzu babu wani labari, kwata kwata ayanzu ma ba batun companyn Rayyern Mai-nasara bane ke damuna, matsalar b’acewar Jannart itace ke damuna hukuma suna iya yinsu abin yaci tura.”

Afakaice kuma ta k’asan idanu, Barrister Kabir ya kalli Yayan nasa, tare da d’an ya mutsa fuskarsa.

Wanda kuma daga wajen Alhaji Idi Sale Dakata’n ma hakan yake, domin kuwa bayan yayi maganar shima, ta k’asan idanu, ya kalli K’anin nasa, tare da sakin wani Shu’umin murmushin,

da shi kad'ai yasan ma'anar yinsa.

Barrister Kabir kuwa, mur yasha tare da saka fuskar tsare gida, irin tasu ta lawyoyi, saboda shima akwai wani abu daya gano amatsayinsa na lawyer.

Shi yanayiwa Barrister Kabir kallon biri, shi kuwa Barrister Kabir yanayiwa yayan nasa kallon Ayaba.

Koda suka fito daga d'akin taron Alhaji Idi Sale Dakata'n, main falon gidan suka dawo, inda suka samu Momy ta gama had'a abinci.

Sama sama haka Barrister Kabir yaci abincin, bayan sun kammala ne kuma yayiwa Yayan nasa sallama, kaitsaye kuma daga gidan Alhaji Idi Sale Dakata'n, gidansa ya nufa.

Koda ya isa gidan afalo ya samu Dijat.

Hira kadan suka tab'a kana kaitsaye ya wuce bedroom d'insa.
Key ya sawa kofar bedroom din, tare da komawa ya zauna, bayan ya d'auko wasu takardu.

Anutse yake wargaza takardun, tare da Ware wasu daga ciki yana duddubawa.
D'ago wata takarda da yayi ne kuma, ya sashi tsurawa rubutu, da kuma hoton passport din dake jiki idanu.

*** ***

Almost 4weeks kenan yanzu da, dawowar Rayyern daga China, Alhamdulillah kuma jikinsa ya warware.

Bisa taimakon Ramadan da kuma Jannart, way'anda suke kula da shan maganinsa.

Hakan yasa ciwon cikin nasa yayi sauki, ya kuma gama samun karfin jikinsa, duk da cewar time to time ya kanji, ciwon cikin na tashi masa, amma da yasha magani yake jin sauki.

Ahankali yake sauk'owa daga kan matattakalan falon, inda yayi kyau cikin shigar Ash colour suit dake jikinsa.

Yayinda hannunsa ke rik'e da briefcase, da alama kuma aiki zaije.
Ya dawo asalin Rayyern d'insa, big man wanda bai wani cika son wasa ba, wani Rama da yawan kasalan da yakeji ada, duk sun kama gabansu.

Mamy dake tsaye akan dining table, jin alaman takun takalmansa ne yasa, ta d'ago kanta ta kalleshi.

Ganin yanda yayi kyau ne kuma, yasa Mamyn sakin murmushi, Cikin kulawa tace.

“Babana yadai, yau na ganka cikin shiri haka fita zakayi ne?”

Kansa ya jinjina, adaidai lokacin da yake gama sauk’owa daga kan steps din yace.

“Eh Mamy yau zanje company.”

Murmushin dake kan fuskar Mamy ne ya fad’ad’a, cikin jin dadi tace.

“Ah Lallai Masha Allah Babana ya samu sauk’i, amma Ina fatan kanajin karfin jikinka sosai.”

Idanunsa ya d’an lumshe tare da jinjina mata kai alaman. “Eh.”

“To kayi breakfast tukun kafun ka tafi.”

Mamyn ta fad’a tana me nuna masa kujera, tare dayi masa alama akan ya zauna.

Fuskarsa ya d’an shagwab’e, kamar zaice a’a kuma saiya zauna.

Dai-dai lokacin kuwa Jannart ta shigo cikin falon, sanye take da riga da wando ajikinta, saidai wandon irin mai fad’in nan ne, haka ma rigar Wacce take da igiyan d’aurewa, hakan ne kuma yasa lafaffen cikinta bayyana, saboda yanda ta d’aureshi da igiyan, haka ma shape din cikin nata ya bayyana sosai.

Kasancewar kuma kayan nada kalan baki, shiyasa ta yafa siririn mayafi daga kanta zuwa wuyanta.

Sassanyan kamshi take bazawa, shigowarta cikin falonne kuma yasa shi sauk’e idanunsa akanta.

Mamy kuwa Ganin Jannart dinne yasa Cikin kulawa tace.

“Yauwa Jannart yi saving din mijinki mana, yana sauri zai tafi wajen aiki ne.”

Kai Jannart din ta d’an sunkuyar k’asa, cikin yanayin nutsuwa tace.

“To Mamy.”

Kaitsaye dining table din da yake zaune ta nufa, saidai koda wasa bata bari sun had’a idanu ba.

Koda ta k’arasa inda yake, plate ta d’auka tare da bud’e food flask, cikin sanyin muryar dake bayyana nutsuwarta tace.

“Ina kwana.”

“Lafiya.”
Ya amsa mata atak’aice, tare da zubawa kyawawan fararen yatsunta idanu.

Abincin ta zuba masa, bayan ta kammala ne kuma ta turo masa plate din gabansa.

Tare da saka masa apple juice din da ta had’a, acikin wani d’an glass cup.

Ahankali ya soma cin abincin, tare kuma da dan lullumshe idanunsa, saboda yanda yake jin kamshinta na shiga hancinsa.

Jannart kuwa Ganin ya fara cin Abincin ne, yasa ta wucewa kaitsaye ta nufi sama, Dan d’auko maganinsa.

Ahankali ta tura kofar d’akin ta shiga.
Lumshe Idanunta tayi saboda, wani irin kamshi daya bugeta.
Ga kuma sanyin ac dake busa ko ina.

Dan bud’e Idanunta tayi, tare da soma bin ko ina dake cikin dakin da kallo, komai nasa need babu alaman datti, duk da cewar ya kwana acikin dakin, amma saida ya gyara komai kafun ya fita.

Hakanan kawai ta samu kanta da sakin murmushi, kaitsaye kuma cikin nutsuwa, ta wuce ta dauko magungunan nasa.

Koda ta sauk’o k’asa harya kammala cin abincin nasa, saidai juice dinne da bai gama shaba, wanda kuma yake sipping d’insa ahankali.

K’arasowa kan dining table din tayi, Anutse ta b’are magungunan tare kuma da zuba su acikin tafin hannunta.

Kallonsa ta d’anyi, tare da mik’a masa magungunan, alaman ya karb’a.

D’ago idanunsa yayi ya kalleta, cikin yanayinsa daya saba yi mata magana yace.

“Ni yaro ne, da har sai kin b’aremin magani, ni bazan iya dakai na bane akace miki? Sai kiyi ta wani ɗuɗɗuramin magunguna babu ko tausayi”

Idanunta ta d’an janye daga kallonsa, saboda ayanzu babu wani abu nasa da bata sani ba, saikayi masa abu sau goma, amma baya tab’a gani yanzu zai gwatsaleta ta fahimci zarginta yakeyi ma shi.

K’wayoyin idanunta tad’an juya ahankali, sau d’aya kuma cikin sigar lallashi tace.

“Okay I’m sorry take it.”

Hararanta ya d’anyi ta k’asan idanunsa,  sanin Mamy na cikin falonne kuma yasa shi, bud’e tafukan hannunsa, Anutse ta zuba masa maganin ahannunsa, gudun kada hannunta da nasa su had’e, tayi hakanne kuma saboda, ita kadai tasan me takeji, aduk sanda ta tuna lokacin da fatar hannunsa ya tab’a nata.

Rayyern kuwa bayan yasha Maganin ne ya mik’e tsaye, tare da d’aukan briefcase d’insa, cikin sauri yace.

“Mamy na tafi saina dawo.”

“A dawo lafiya Allah ya bada sa’a.”

Mamyn ta bashi amsa, Cikin kulawa.

Da  “Ameen.”
Ya amsa kana ya sakai ya fice daga cikin falon.

Ganin hakanne kuma yasa Jannart dawowa, kusa da Mamyn ta zauna.

Shikuwa Rayyern yana fita kaitsaye company ya wuce,
Koda yaje kuwa ya samu ma’aikatan nata aiki, kowa na aikinsa kamar yanda ya dace.

Gaba d’aya ma’aikatan sun bada himmansu wajen yin aikin  tsakani da Allah.

Domin har anfara har had’a cattoon's din abubuwa, wanda kowanne kwali d’auke yake da sunan tambarin.
MAI-NASARA.

Komai Yayi masa sosai, hakanne ma yasa shi jinjina kansa, kaitsaye kuma ya wuce office d’insa dake nan cikin companyn.

Wasu d’an aikace aikace yayi, bayan ya kammala ne kuma ya fito, kaitsaye hospital d’insa ya wuce.

Bashi ne ya dawo gidan ba kuwa sai k’arfe 10:00 pm dai dai.
Hakan ya faru ne kuma saboda tsayawa da yayi, yiwa wata operation, baya ga haka kuma, ya tarawa kansa aiki sosai, wannan dalilin yasa shi tsayawa, ya d’an rage ayyukan.

K’asa k’asa ya danna Horn din motar tasa, cikin abunda bai wuce mintuna 2 ba kuwa, aka wangale masa gate din gidan.

Anutse ya tura hancin motar ciki, bayan yayi parking motar ne kuma ya fito.

Tare da Kallon Baba Maud’o wanda shine ya bud’e masa gate din.

“Baba Maud’o da kanka, ai daka bari na fito na bud’e, sam banaso naga kana wahalar da kanka, saudayawa Idan naga kana wannan aikin sai naji duk babu dadi, please Baba Maud’o ka bari.”

Rayyern din ya fad’i haka ga Baba Maud’o cikin tausasa harshe.

Baba Maud’o kuwa Murmushi yayi tare da d’an gyara tsayuwarsa, kana Cikin kulawa yace.

“Haba Rayyern meye na damuwa kuma, bayan kasan hakan aikina ne, kuma gashi Ari yayi bacci shiyasa.”

Fuska Rayyern din ya d’an kwab’e, hade da karyar da wuyansa yace.

“Ni dai Baba Maud’o da gaske banason hakan, banajin dadi Idan naga kana bud’e gate inajin wani nauyi a zuciyata.”

Murmushi Baba Maud’o yayi, tare da komawa wajen zamansa ya zauna.

Ganin hakanne kuma yasa Rayyern d’in ma, matsawa ya zauna akusa da Baba Maud’on.

“D’azu Barrister Kabir yazo dubaka da jiki, amma baisame ka ba, saidai yace agaisheka.”

Baba Maud’o ya fad’a yana me Kallon Rayyern din.

Shikuwa Rayyern Ajiyar zuciya ya sauk’e, tare da d’an mammatsa hannunsa.
Cikin kuma taushin murya yace.

“Ina amsawa, bari na shiga ciki Baba Maud’o, yau duk na gaji aikin office ya gajiyar dani.”

“To Rayyern Mukwana lafiya.”

Da “Ameen.”
Rayyern din ya amsa, tare da wucewa ciki kaitsaye.

Koda ya shiga main falon nasu babu kowa, hatta su Ramadan da Riyyam nsra duk suna daki.

Kaitsaye kuma shima d’akin nasa ya nufa.
Yana shiga kuwa ya soma rage kayan jikinsa.

Bayan ya shiga toilet yayi wanka ne kuma, ya shirya kansa cikin lallausun kayan bacci.

Bayan yasha Nutri milk ne kuma ya koma kan gado ya kwanta.

Kasancewar agajiye yake ne kuma, yasa yana kwanciya bacci ya d’aukesa.

Washegari.

Arewa24 tv station.

Aunty Fauziya ce ke tafe cikin d’an sauri, saidai kallo d’aya zaka yiwa Fuskarta, ka fahimci cewa tana cikin yanayin damuwa.

Fitowarta  kenan kuma daga dakin yad’a labaransu, sukayi Karo da Salman.

Kallonta Salman din yayi, Ganin damuwa afuskarta ne kuma yasa shi d’an tsayawa, Cikin kulawa yace.

“Aunty yadai naganki haka, wani abu ya faru ne?”

Kai ta d’an girgiza, cike da damuwa tace.

“Salman b’acewar Jannart ke damuna, tayaya za ‘ace mace kamar Jannart ta b’ace b’at kamar kud’i? hankalina yana tashi sosai Salman, ka duba dai irin jami’an tsoron da Babanta ya bawa cikiyar nemo ta, ga kuma mu da kullum sai munsa cikiyarta, amma har yau babu wani wanda yace ya ganta, abun yana min ciwo Salman, ga mahaifinta asanadin haka ko lafiyar kirki bashi dashi, kwanan nan naji har India aka fita dashi,  duk kuma akan lamarin b’acewar Jannart, Ina cikin damuwa akan hakan.”

Ajiyar zuciya Salman ya sauk’e.

Dai-dai lokacin kuwa Asiya tazo ta wucesu, saiwani karairaya takeyi tamkar zata b’alle.

Ganin hakanne kuma yasa Aunty Fauziyan wucewa office dinta, take kuwa Salman ya rufa mata baya.

Koda suka isa cikin office din zama, duk sukayi, ananne kuma Salman ya d’ago ya kalli Aunty Fauziyar.

Cikin sanyi ya d’an gyara zamansa tare da cewa.

“Gaskiya da banyi niyan fad’awa kowa ba saboda sirrine, saidai ke naga gaba d’aya hankanlin atashe yake, akan b’atan Jannart, amma Dan Allah duk wata magana da zan fad’a miki inason ta zama sirri.”

Nisawa Aunty Fauziya’n ta d’anyi, tare kuma da fuskantar sa tace.

“Kafad’i duk abunda kakeson fad’a Salman, Insha Allah bazan gayawa kowa ba, kasanni kasan koni wacece zan rik’e duk wani sirri.”

Kai Salman din ya jinjina, tare da dan gyara zamansa kana yace.

“K’warai nasan hakan Aunty Fauziya, nasan ke ta musamman ce shiyasa ma na yanke shawarar sanar dake, danki cire wannan damuwar dake zuciyarki, agaskiya Jannart ba b’ata tayi ba.”

Idanu Aunty Fauziyan ta tsura masa cike da mamakin, Jin abunda ke fitowa daga bakinsa tace.

“Kamar yaya Salman ka warwaremin maganar ta yanda zan fahimta.”

“Jannart ba wai b’acewa tayi ba, K’anin Babanta Barrister Kabir shi yayi mata aure, batare da sanin kowa ba, yace kuma yayi hakanne saboda wani dalili nasa maik’arfi, wanda kuma acewarsa hakanne kad’ai zai tseratar da rayuwarta, daga fad’awa koman magauta masu farautar rayuwarta.”

Wani irin gauron Ajiyar zuciya Aunty Fauziyan ta sauke, duk da cewar taji mamakin maganan k’warai, amma kuma taji sanyi acikin zuciyarta.

Numfashi ta d’anja tare da Kallon Salman din, cikin sanyin yanayi tace.

“To wannan al’amarin da d’aure kai yake gaskiya,  amma kuma shi yaron da aka aura mata d’in tana sonshi ne, ko kuma shi yana sonta?”

Kai Salman din ya girgiza, kana asanyaye yace.

“Agaskiya kuma wannan ne bansani ba Aunty.”

D’anjim Aunty Fauziyan tayi, na y’an wasu dak’ik’u kuma tace.

“Kayi hakuri Salman, agaskiya ada nayi tunanin duk abunda zaka fadamin zan rufeshi, amma kuma sai gashi yanzu, naji ajikina tamkar akwai wata rawa da zan iya takawa, akan wannan al’amarin,  lalle dole zan san yadda  zanyi naga Jannart, muje wajen MD.”

Ta k’are maganan tana me mik’ewa tsaye.

Hakan yasa Salman rufa mata baya, kaitsaye suka nufi ofishin MD.

Koda sukaje Aunty Fauziyan ce ta kawo masa maganan Jannart, tare da nuna b’uk’atar ta nason Ganin Jannart din.

Jin buk’atar tasu ce kuma yasa MD jinjina kansa, cikin kokonton hakan yace.

“Agaskiya inajin kamar hakan bazaiyiwu ba Fauziya, saboda maganan nan sirrice da ba’aso kowa ya sani, nima kaina ba’a gayamin Dan matsayina ko wani abuba, a'a kawai dai angaya minne saboda, kada Jannart din ta rasa aikinta anan gaba,  haka ma Kai Salman kasan dalilin da yasa aka gaya maka,  saidai ba damuwa bari mu jarraba, zan k’ira Barrister Kabir din muji.”

Ya k’are maganan yana d’aukan wayarsa.

Aunty Fauziya kuwa murmushi tayi, tare dayi masa godiya.

Shikuwa MD’n kiran numbern Barrister Kabir yayi, cikin sa’a kuwa ya samu Barrister Kabir din ya d’aga wayan.

Bayan sun gaisa ne kuma yake shigar da buk’atar Aunty Fauziyan awajen Barrister’n.

D’an Jim Barrister Kabir yayi, cikin d’an nazari kuma yace.

“To shikenan MD, amma kana ga kayarda da matar kuwa, kana ga sirrinmu bazai fita awajenta ba.”
Yayi mgnar murya a sake dan yanzu ko mgnar ta fita yana da ɗan yaƙini fito na fito da magautanta sai dai baida cikekkun hujja.

“Sosai kuwa Barrister, saboda Fauziya D Sulaiman macece mai amana, karanci, tausayi, da saukin kai, kuma akwai rawar da zata iya takawa, musamman Kodan wajen bawa, Jannart din shawarwari ma.”

MD din ya fad’a.

Jin hakanne kuma yasa Barrister Kabir cewa.

“Badamuwa bari na turo muku numbern, amma ko Salman ban yarda a bashi numbern ba, ita matar kawai za’a bawa.”

“To Insha Allah.”
MD din ya fad’a.

Nan ya katse wayar, da kaman minti d’aya kuwa sai ga, text na numbern Jannart din ya shigo cikin wayar MD.

Take kuwa MD ya tura mata numbern.

Godiya Aunty Fauziyan tayi masa, cikin jin dadi kuma ta juya ta tafi.

Haka dai Rayuwa ta ci gaba, inda yau ansamu k’arin kwanaki, akan wata d’ayan daya shud’e.

Alhamdulillah kuma abubuwa duk, suna tafiya yanda ya kamata, musamman a b’angaren Rayyern, wanda ayanzu kusan kullum Idan ya fita, baya dawowa sai dare,  saboda yakanje asibiti da company, shiyasa gaba d’aya ma ko isashshen zama baya samu.

Ab’angaren Jannart kuwa rayuwarta take normal, saboda ayanzu ta gama sabo da duk y’an gidan, Masha Allah komai yana tafiya mata daidai sai dai time to time tana tuno gidansu har tayi kwalla.

Acan tashar tasu kuwa, yau din Aunty Fauziyan ce zaune, acikin office dinta, wayarta ce kuma ke rike ahannunta.

Gaba daya ta shiga cikin nazarin kiran wayan Jannart, saboda yanda take kokonto akan ta kira ne ko a’a.

Ayau dai kam ta yanke shawarar kiran wayan Jannart din.

Acan gidansu Rayyern kuwa, yau Nasir yazo, hakan yasa suka had’u shida Riyyam nsra da kuma Ramadan.

Gaba d’ayansu afalon saman suka zauna, haka duk suka cika musu gidan da sowa, saboda Kallon wasan k’wallo da sukeyi.

Wanda kuma sun samu freedom din nasu ne, saboda ganin Rayyern baya nan.

Ciye ciye kuwa ba kalan wanda ba suyi ba, bayan pizza da shawarman da sukaci, hatta sweet saida suka sha, anan kuma cikin falon suka zubar da ledodin musamman Nasir shima dan masifan son zaƙine,  haka kuma duk wasu pillows dake jikin kujerun falon, saida suka watsar dasu sukayi musu d’add’aya.

Bayan sun gama abunda za suyi ne kuma suka fice, batare da sun gyara falon ba.

Rayyern kuwa yaudin ad’an gajiye ya dawo gidan.

Wanda hakanne ma yasa bainemi su Mamy ba, kaitsaye ya wuce saman.

Saidai yana shiga, abunda ya gani ya sashi d'an zaro idanunsa.

"What is this?"

Ya fad'a yana me Kallon yanda falon nasu ya haukace.

Saurin Ajiye briefcase d'insa yayi, tare da juyawa cikin sauri ya koma, domin yasan hakan ba aikin kowa bane, saina su Ramadan da Riyyam-nsra.

"Mamy Mamy!!"

Da k'arfi yake d'an k'wala k'iran sunan Mamyn, yana me saukowa daga kan steps din.

Mamy kuwa jin kiran da Rayyern din keyi mata ne, yasa ta d'an lek'owa daga kitchine tare da cewa.

"Lafiya kuwa Rayyern?"

Fuskarsa ya d'an kwab'e tare dasa hannu, ya kama waist d'insa, cike kuma da takaici yace.

"Mamy Ina su Ramadan, kinga yanda suka yi min kaca kaca da falo kuwa? sunb'ata min komai, sunyi ciye ciye sunbar duk wani datti awajen, Mamy wallahi ki kirasu suzo su share."

Ajiyar zuciya Mamyn ta sauk'e, tare kuma da komawa ta zauna, tana me cewa.

"Nifa banmasan da yaushe suka fita ba, nasan dai d'azun sunanan harma da Nasir, amma yanzu kam da 'alama basa ma cikin gidannan."

Fuskarsa ya sake kwab'ewa, still cikin kame k'ugu yace.

"Gaskiya ni Mamy azo agyaramin, sun b'ata komai ko wajen da mutum zaibi mai tsabta babu."

Murmushi Mamy tayi saboda sanin halin rigima, irin nasa da tayi ne kuma yasa, ta kalli Jannart da yanzu fitowarta, cikin dan tausasawa tace.

"Dan Allah Jannart jeki gyara masa falon, nikam aiki nakeyi a kitchine, Idan ba haka ba wannan da kike gani bazai barmu ba, ya tamana kwarnafi kenan kaman mu muka b'ata."

"To."
Jannart din tace tare da sunkuyar da kanta k'asa, kana anutse ta haura saman.

Shikuwa Rayyern sauka falon kasan yayi ya zauna.

Koda ta haura kuwa Anutse ta soma tattare falon, cikin mintuna kad'an kuma ta kammala, air freshener ta fesa tare da jawo kofar ta rufe.

Kana anutse ta sauk'o k'asa.

Tun fara sauk'owanta daga kan steps kuwa ya tsurawa, kyawawan k'afafunta ido, musamman yanda ta d'an tattare sket dinta, hakan yasa yake iya hango kyawawan singalalinta.

Itakuwa Jannart Anutse ta k'arasa sauk'owa k'asan.

“Yunwa nakeji.”

Ya fad'a still bai d'auke idanunsa daga kan kafarta ba dan yana tsoron kallon samanta gani yake zata tsole mishi ido da waɗannan abubuwan nata saukinta  ɗaya bata rabuwa da mayafi.

Kai kawai ta jinjina masa, alaman to, kana cikin nutsuwa ta nufi kitchine.

 Fried rice and coleslaw da kuma tamarin juice ta kawo masa, Anutse ta ajiye abincin agabansa, daidai lokacin kuma wayarta dake aje gefensa, ya soma tsuwa alaman shigowar kira.

Saurin d'agowa tayi tare dakai dubanta, ga screen din wayar, Ganin new number'n dake kiranta ne kuma, yasa duk ta cika da mamaki, Ahankali kuma ta dawo da kallonta garesa,  wanda shidin ma kuma idanu ya zuba mata.

Sake Kallon wayartata tayi, cike da mamaki.

Shikuwa Rayyern fuska ya tab'e, cikin kuma halin ko inkula yace.

“Kima daina wani pretending ki daga, ki fada musu cewar na warke, domin basu samu yanda suke soba, ban mutu ba.”

Idanunta ta d'an zuba mishi, cike da mamakin kalaman nasa, da yakeyi wanda akullum bata fahimta, batasan me hakan yake nufi ba, shin wai baiyarda da ita bane ko kuwa, yana ga kamar cutar dashi zatayi.

Kanta kawai ta girgiza tare da d'aukan wayan nata, Ahankali ta sakala wayar akan kunnenta, saidai batayi gangancin fara magana ba.

Daga can b'angaren Aunty Fauziya kuwa, Jin an d'aga wayar ne yasa ta yin sallama.

Aikuwa take Jannart ta d'auko muryar, lokaci guda cikin mamaki da farinciki tace.

"Laa My Aunty  kece?"

"Eh nice Jannart, ya kike ya kwana biyu."
Aunty Fauziyan ta tambaya tana murmushi.

Cike dajin dadi Jannart din tace.

"Lafiya kalau my Aunty, wallahi nayi kewarki a ina kika samu number na."

"Nima haka Jannart, numbern ki kuma Abbanki ne ya bani."

Aunty Fauziyan ta fad'a cikin kulawa,  tare kuma da cewa.

"Fatan kuna lafiya ya maigidanki?"

D'an juyowa Jannart din tayi ta kalleshi, wanda kuma shidinma kuma ita yake kallo.

Saurin juyar da kanta tayi, kana cikin sanyi yace.

"Lafiyanshi k'alau."

"Masha Allah, Kodai yana kusa ne naji muryarki k'asa k'asa.

"Uhummm."
Jannart din ta amsa tana dan Murmushi.

Jin hakanne kuma yasa Aunty Fauziyan cewa.

"Shikenan Jannart muyi waya anjima, yanzu bari na barki kiji dashi."

Tana gama fadin hakan kuwa ta katse kiran.

Jannart kuwa batare da ta sake juyowa ta kalleshi ba kaitsaye ta wuce d'akinta.

Shikuwa Rayyern bayan ya gama cin abincin ne ya tashi ya haura sama.

To ahaka dai rayuwa taci gaba da tafiyar musu, bayan 5 weeks kuma abubuwa duk sun sanja, yanayin gari da kuma weather ya juya izuwa, yanayin zafi, domin zuwa yanzu har anfara iska da kuma hadari dake nuna shigar yanayin farko-forkon damuna.

Kamar yadda yayi kwanaki shida baya, yau din ma tun bayan sallan la'asar, misalin biyar saura.

Gaba ɗaya garin ya game da hadari, bak'ikk'irin daga gefen gabas kowa ya daga ido ya kalli hadarin sai ya razana, sabida yadda yayi gangami yayi duhu.  saidai kuma cikin dan wani lokaci hadarin ya fara komawa ja, da dukkan alamu kuma, iskane mai k'arfi yake kokarin tashi irin na forkon damuna.

A cikin compound din gidan nasu kuwa, Abba ne da Baba Mauɗo ke zaune, suna nan zaunen ne kuma suka hango Rayyern wanda ya fito, Cikin nutsuwa yake tafiya.
Yana mai daga kanshi yana kallon saman gidan nasu tare da zazzagaye kowani lungu da sak'o na gidan.

Baba Mauɗo kuwa binshi da ido yake yana wani irin murmushi mai cike da jin daɗin.

Idanu Abban ya dan lumshe tare da jingine kanshi da jikin bango.
Cikin yanayin nazarta yace.

"Hmmm  gado ba karambani ba, komai na daga cikin d'abi'ar mahaifinshi bai bari ba."

Shikuwa Rayyern dake ta faman zazzagaye gidan,  yanayin hakanne saboda sunnah ce da Manzon Allah (S.A.W) ya keyi, Idan yaga hadari Yakan zazzagaye gidansa, Dan dudduba abubuwa abinda ke bukatar gyara ya gyara na killacewa a killace.

Yana cikin zagayen ne kuma wayarsa dake cikin aljihunsa ta soma kara.

Koda ya duba, ganin sunan sunan Dr. Sulaiman ne ya sashi d'agawa.

Bayan sun gaisane kuma Dr. Sulaiman din yace.

"Dr batun tafiya Mascow fa, komai ya riga daya Kankama, Insha Allah nanda 2 to 3 weeks masu tafiya zasu tafi."

"Okay."
Kawai Rayyern din yace atakaice tare kuma da katse kiran.
Sabida iskar ta fara saukowa,
Ci gaba yayi da zagaye wajen, harta side din su Baba Maud'o kuwa saida yaje ya duba, Ganin komai normal ne yasashi dawowa cikin gida.

Wanda zuwa lokacin kuwa iskan ya taso gadan gadan.

Lokacinne kuma Abban shima ya shigo, tare da neman waje ya zauna.

Baba Mauɗo Kuma ya shiga side ɗinsu

Rayyern din kuwa windows din dake abude ya rurrufe.

Yayinda Abba kuwa ya zuba masa ido, adai-dai lokacin kuwa shi kadai yasan me yake rayawa acikin zuciyarsa da kuma abinda yake tinawa

Rayyern kuwa Bayan ya gama rurrufe ko inane, idanunsa suka sauk'a akan k'ofar falon Jannart, da iska ke bud'eshi yana rufewa shi gib da karfi.

Juyawa yayi kamar zai haura sama kuma sai ya fasa ganin Abba nata kallon shi sai kuma ya kalli wannan kofar.
Anutse ya nufi kofar tata, Koda ya isa hannunsa yasa ya tura k'ofar, tare kuma dasa kansa acikin falon, yayi hakanne kuma saboda nan ne kadai falon daya rage da bai duba ba.

Ahankali ya sauk'e idanunsa akan Jannart Wacce ke zaune akan kujera.

Sanye take cikin wata riga Marar nauyi, wanda tayi mata kyau sosai,  ga kuma gashin kanta dake watse dan ko d'ankwali bata dashi.

Idanunta da hankalinta kuwa, duk yana ga tv inda take Kallon wani cartoon mai abin dariya.

Idanunsa ya d'an janye daga kallonta, had'e dajan d'an guntun tsaki, kaitsaye kuma ya wuce dan rurrufe windunan falon.

Sautin tsakin nasa ne kuma yasa Hankalin Jannart dawowa kansa, da sauri ta juyo, ganinsa da tayi ne kuma yasa ta, saurin tashi ta gyara zamanta.

Saidai kuma gaba daya babu mayafi akusa da ita, hakan yasa ta d'an takure jikinta waje daya.

Shikuwa Rayyern ci gaba da rufe windows din yayi har ya juya ya fuskanci tsakiyar falon.
Sai kuma ya ɗan juyo kansa ya kalli bayanshi ganin yadda labuyen suka a harde alamun iskane ya hardesu, ba tare daya juya ba.
 Ahankali kuma ya dan Mika tsawonsa,  dan son gyara labulen daya hard'e asama sabida iskar sosai ya daga hannunsa sabida windows din sunada tsawo sosai.

Hakan kuwa shi yasa rigarsa ta d'age ta ɗanyi sama.
Daga cibiyarsa zuwa kasa suka bayyana,
Dai-dai lokacin kuwa Jannart ta sauk'e Idanunta akan shatin, saman mararsa kasan cibiyarsa da kuma black boxer  din dake jikinsa.

Wanda ya kara haska farar fatarsa.

Idanunta ta zubawa wajen, bata ko k'yaftawa, saboda yanda shatin marar tasa ya bayyana sosai, ga kuma hasken da wajen ke dashi kana ga wani tattausan gargasa dake kwance daga ƙasan cibiyar tasa har zuwa ƙasa sosai inda robar boxes dinsa ke manne da jikinsa har ana iya

ɗan hango saman mararsa kana asalin dogon wondon kuma yayi ƙasa sosai kan mazauna sa wanda haka yasa shatin surar jikinsa bayyana.

Wani irin rawa takejin jikinta da idanunta sunayi.
Yayinda gaba ɗaya tsikar jikinta ke mimmiƙewa tsaye.
Wani irin harbawa zuciyarta keyi mai tafe da tsoron abinda idonta bai taɓa katari dashiba.

Rayyern kuwa kanshi na sama, baima san tana kallonshi ba.
Saida ya gama warware labulen.
ahankali ya d'an sauk'e hannunsa sama, tare da juyowa ya sauk'e idanunsa akanta da sauri ya sunkuyo ya kalli setin inda take kallo a jikinsa.

Fuskarsa ya tsuke tare da tab'ewa kana ya watsa mata wata Zazzafar hararanta cikin takaici yace.

"Meye? Mayya kawai cinyeni zakiyi ne?"

Da sauri ta kauda idanunta tayi daga garesa, tare da mikewa tsaye ta d'auki wayarta yayinda wata azabebbiyar kunya ta rufeta.

Ahankali ta dan Raba zata wuce zuwa daki.

Shikuwa Rayyern cikin tsautsayi, labulen da yake gyarawan ya ture wani goran ruwa dake gefe, hakan kuwa shi yasa ruwan ya malale awajen.

Juyawa shidinma yayi da niyar fita, dai-dai lokacin kuma Jannart ta iso sukayi gab da gab, batare da sun Ankara ba kuwa, saiji yayi gaba daya tsantsi ya debe sa Suuuuuu haka ya tafi idanunsa ya zaro, tare kuma da fad'awa kan Jannart, wani irin masifeffen tsorone da fargaba ya rufeta wanda yasata rumtse idanunta jin sun tafi suuuu sun f...!!!

*GARKUWAR taku ce dai MA'AURATA, da masu shirin aure, da masu jego, da yan gayu masu son k'amshi kece raini, da gyaran da zaike maimaita muku dararen forkon kuruciya*

Ko kunsan Jikinmu na da sinadaran hormones da suke taimakawa dan'adam akan komai musamman lokacin da mace take mu'amalar aure da mijinta. Mafi akasari wannan hormones din ne ke samun matsala ko su yi sanyi koma su daina aiki kwata-kwata shi ne dalilin da zai sa mace tace bata jin sha'awa ko bata san dadin aure ba. Albishirinku ina da kayan da ke taimakawa wannan sinadaran du dawo aiki tukuru don karkato miki da kimarki wajan mai gida sannan su taimakawa wannan sinadaran hormones dinki su dinka secreting din ni'ima wadatacciya da zata taimaka miki ki gamsu mijinki ya gamsu fiye da tunaninki. Note: Kayana ba sa tsinka ruwan ni'ima suna dai taimakawa hormones dinki ne su tsattsafo da ni'imar

musamman wacca cutar sanyi ko dattin mahaifa ya dankarar da su ya hana su yin aikinsu yanda ya kamata. Haka zalika idan kina da kyau ki kara da wanka. Zaki iya amfani da magani na na gargajiya wanda zai gyara miki sex hormones din kullum ki kasance cikin humidify wato cikin damshi mai albarka kamar yanda ake son mace. Yana gyara miki mara.

Sai kamshi. Hajiyata daure ki fara amfani da turarena ki ji irin salon kamshin sa salo ne da zai daidaita ki da mijinki ya kankaro miki da kimarki a wajansa. Siyan na gari mayar da kudi gida.

Ga masu buƙata ga number' wayata wanda nake whatsApp dashi 09097853276 kimin mgn ta whatsApp in har kin tabbatar kin shirya saya mu dai-dai ta, kayana ba ƙanana bane, shiyasa bana harkan karanta, muddin kinsan baki shirya sayaba Please kada kiyi min mgn ki bari sai kin shirya kuɗinki a hannu,  ba ina nufin kayana bana talaka bane, no akwai ƙananan set na masu karamin karfi, banson aimin mgn a ɓatamin lokacin aiyukana a shirme baki shiryaba. Shine karantan da bana so.
0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU. In kin shirya ga number ta ga kuma account number ta wanda in mun gama mgn zaki turo kudin ki, kana insa miki kaya a mota, duk ƙasar da kike kayana zaije gareki, amman fa in kinada dalilin zuwan nasune🤝🏻sayan na gari meda kudi  gida.

Dan Allah masu son kaya in dai kin san baki shiryaba baki da kudi a ƙasa ki huyar dani da kanki kasa kimin mgn.

GARKUWAR MA'AURATA

By
*GARKUWAR FULANI.*
22/12/2021, 19:45 - 🥰🥰: Matar da hoton fuskarta ya cika fuskar wayar.

Wani irin harbawa yaji zuciyarsa tayi da karfi, wanda har saida hakan yasa shi zaro idanunsa waje.

Da matukar mamaki yake Kallon fuskar matar, Wacce bata da wata maraba da fuskar Ramadan, domin kuwa tsananin kaman Ramadan daya hango akan fuskarta ne ma, ya sanyashi jin wani irin bugun zuciya.

Lokaci daya kuma yaji wani irin nauyi, da kuma dattakun matar ya cika idanunsa, Yayinda daga cikin zuciyarsa kuwa, wani irin girma, kima, karamci, martaba da kuma haibar matar ne ke hauhawa cikin duk harbawar da zuciyarsa keyi.

Ganin fuskar matar ne kuma yasa, kowanne kofar gashi dake jikinsa budewa, take yaji wani irin sanyi na ratsa shi tako Ina, Yayinda kuma nutsuwa ke kara saukar masa.

“Mammy Ina kwana!!”

Ya fad’a cikin tausasa murya daga can cikin maƙoshinsa har zuwa kan labbansa.

Daga b’angaren Mammy kuwa da ta tsura masa ido bata ko k’yaftawa, wani irin abu itama takeji acikin zuciya da gangar jikinta, lokaci daya kuma taji zuciyarta tayi rauni sosai, tabbas Kallon fuskar Rayyern din da tayi ayanzu, yana tattare da wasu abubuwa da dama, ciki kuwa harda abunda ke kwance acikin zuciyarta, a mafi rinjayen tsawon shekarun rayuwarta.

“Lafiya Maud’ona ya jikin ka?”

Mammyn ta tambaya cikin boye rauni, da kuma damuwar dake kwance akan fuskarta yace.

“Alhamdulillah jiki na yayi sauki Mammy.”

Rayyern din ya bata amsa, cikin sanyi da kuma sigar tausasawa.

Riyyam-nsra kuwa dake zaune agefe idanu ya zubawa, Hamma Rayyern din nasa.

Mammy kuwa Daga can b’angaren ta, murmushi ne ya dan bayyana akan fuskarta, cikin tsananin kulawa da kuma muryar tausayawa tace.

“Allah Ubangiji ya karamaka lafiya, ya kareka aduk inda kake, ya tsare gabanka da bayanka, ya kuma nisanta ku da duk wani sharrin mutum da aljan, Allah ya baku zaman lafiya kaida iyalinka, ya albarkaci rayuwarku ya cika haske a rayuwarku Allah yayi maka al'barka!!!.”

“Ameen thumma Ameen Mammy nagode sosai.”

Rayyern din ya fada cikin nuna tsananin jin da d’insa, domin kowacce kalma da Mammyn zata fad’a, jinsa yake yana tasiri acikin zuciyarsa, Yayinda kuma yakejin wani irin farinciki na musamman yana lullub’eshi.

Mammyn ma Ganin farinciki kwance akan fuskarsa ne yasa ta jin dadi aranta, cikin kuma sakin fuska tace.

“Ya Ramadan da Mamyn ku?”

“Lafiyansu kalau Mammy, saidai Ramadan ya tafi wajen aiki, Mamy kuma tana k’asa.”

Ya bawa Mammyn amsa asake, yana mejin Karin nutsuwa na saukar masa sabida mgnar da yakeyi da itan.

“Masha Allah Allah ya taimaka, Ina Surukata Jannart, fatan itama tana lafiya.”

Mammyn ta tambaya da kulawa.

Idanunsa ya d’an lumshe tare kuma da bud’e su alokaci guda, cikin kwarin jikin daya samu yace.

“Lafiya yanzu ta sauk’a k’asa.”

Murmushi Mammy tayi, tare da jinjina kai, cikin farincikin dake da d’a mamaye zuciyarta duk bayan minti guda tace.

“To bari na bawa Zaytoon ku gaisa, gatanan duk ta tsareni da ido.”

Murmushi Rayyern din yayi dai-dai lokacin kuma, Mammyn ta mikawa Zaytoon dake gefen ta wayar.

Karb’an wayar Zayton tayi, tare da fadada fari’ar dake kan fuskarta, cikin muryarta mai dan sanyi tace.

“Hamma Rayyern.”

Saurin d’ago idanunsa yayi, ya kalli kyakkyawar yarinyar da ke magana acikin wayar, wanda muryarta tayi masa sak da wata muryar da yaji kwanannan , idanunsa ya Dan bud’e da kyau, tare kuma  da zaro su waje, badon komai ba kuwa saidan Ganin still kamanin yarinyar sak na Ramadan ga kuma kamannin muryarta da waccar tsohuwar kamar dai yadda kamannin Muryar Ramadan Riyyam-nsra da ita Zayton ɗin a can wani sashin na zuciyarshi kuwa kamarsa da Riyyam-nsra ne ya fado masa “Yah salam”.
Yace a ransa a zahiri kuwa,
Idanu ya dan zubawa yarinyar, har na tsawon minti daya, kafun daga bisani ya fadada fara’ar dake kan fuskarsa, cikin sakewa yace.

“Na’am Zayton.”

Murmushi Zayton din tayi, kana cikin jin dadi tace.

“Sannu Hamma Rayyern ya jikinka, Ina fatan dai kayi sauki sosai, kuma kana cin abinci sosai ko?.”

Wani irin Murmushi Rayyern din yayi, wanda har saida kyawawan hakoransa  suka bayyana, tashin farko yaji matashiyar budurwar tashiga ransa sosai.

“Jikina da sauki sosai Zaytoon, amma banason Ina yawan cin abinci saboda kada na zama ɗan lukuti kamarki.”

Dariya sosai Zaytoon ta kwashe dashi, saboda daga jin yanda yayi maganar ma kasan akwai

tsokana aciki.

“Haba Hamma Rayyern ni har wani jiki ne dani, kanaga saboda banida jiki ne ma ai, Riyyam  ya rainani, Hamma Rayyern Ina Auntyna Jannart take?”

Zaytoon din ta tambaya, cike da kulawa.

Murmushi yayi tare da d’an shafa lallausan sumar kansa, cikin muryar tausasawa yace.

“Tana k’asa.”

Kai Zaytoon din ta jinjina, tare kuma da dan rausayar dakai, cikin nuna kulawarta agaresa tace.

“To ka gaishemin da ita kaji, sannan please Hamma Rayyern kana kulawa da kanka kaji, Allah Ya baka lafiya mai amfani.”

Idanunsa ya d’an lumshe tare kuma da sauke Ajiyar zuciya, saboda sosai yaji dadin addu’ar da yarinyar ta masa kana har cikin ransa yake jin sonta a ransa.

Wanda har hakan yasa shi cewa.

“Ameen nagode Zaytoon.”

Kai Zaytoon din ta jinjina, Yayinda shikuwa Rayyern ya mikawa Riyyam nsra dake zaune agefe wayan.

Da sauri Riyyam da zuciyarsa ke cike da farinciki ya karb’i wayan tare da fuskantar screen din wayar, cikin kula dajin dadi  yace.

“Mammyna yau kam kinga Hamma Rayyern dinmu ko.”

Kai Mammyn ta jinjina, cike da jin dadi tace.

“Kwarai kuwa Riyyam yau kam naga Rayyern.”

Tayi maganan cikin kasa da murya, ta yanda Riyyam dinne kadai zai iya Jiyota.

Jin abunda ta fada dinne kuma yasa Riyyam nsra tashi, rike da wayan a hannunsa kaitsaye ya nufi dakin Ramadan.

Shikuwa Rayyern maida kansa jikin kujera yayi, tare da lumshe idanunsa, ahankali yake lumshe idanunsa, yana mejin wani irin nutsuwa na saukar masa.

Mammy da Riyyam kuwa basu wani jima suna magana ba, Mammy ta katse kiran.

Acan Ethiopia kuwa bayan Mammy ta ajiye wayanne, Ta zame daga zaunen da take tare da durk'usawa k'asa tayi sujjada.
Na nunawa Allah tsananin jin dadinta, da kuma godiya agaresa, domin komai da yake faruwa shine ya tsarashi, shine kuma yake bawa ahalinta dama ita kanta kariya akoda yaushe.

Acan b'angaren Jannart kuwa  Anutse ta kammala gasa masa roasted fish, tare da matsa masa ruwan lemon tsami aciki, kamar yanda ya gaya mata yana buk'atar abu mai d'an tsami tsami, bayan ta kammala had'a masa roasted fish dinne kuma, ta soma kokarin yi masa miyan kase kamar yanda ya  buk'ata, saidai kuma kasancewar miyar tana daukan lokaci sosai, shiyasa gama ta ba yanzu yanzu ba.

Rayyern dake zaune afalo kuwa, Ganin almost 1hour ya kare ba akowa masa abincin nasa bane, yasa shi haurawa saman sofa ya kwanta.

Ahankali yake lullumshe idanuwansa, wanda da'alama kuma bacci yakeji, duk da cewar kuma yana jin yunwa, amma hakan baisa baccin yaki daukarsa ba.

Domin yana nan akwance cikin abunda bai wuce 20mn ba, bacci ya d'aukesa, kasancewar acikin magungunan da yake sha akwai mai dan saka yawan bacci.

2hours later.

Ahankali yake bude idanunsa, wanda suka shafe sama da awa biyu a kulle.

Mik'a ya d'anyi ahankali tare da ambaton sunan Allah acikin zuciyarsa.

Ahankali ya dan tashi zaune, tare dasa hannu ya shafa kan lafaffen cikinsa, da keyi masa kukan yunwa.

Numfashi ya d'an fesar akasalance kuma, yakai dubansa izuwa babban agogon dake cikin falon.

1:25 pm dai-dai agogon ya nuna masa, wanda hakan ya sashi d'an yunk'urawa ya mike. Musamman saboda ganin da yayi lokacin sallah yayi.

Hannayensa ya zura acikin aljihun wandon dake jikinsa, kaitsaye kuma cikin tafiyar, dake nuna ya Dan samu karfin jikinsa ya nufi bedroom d'insa.

Koda ya shiga cikin bedroom din Anutse, ya soma kokarin rage kayan dake jikinsa.

Bayan ya cire trouser'n dake jikinsa ne kuma, ya d'auko wani towel ya d'aura akan waist d'insa.

Direct toilet ya wuce, inda ya had'ewa kansa ruwan wanka mai d'an d'umi.

Anutse yayi wankan nasa tare da d'auro alwala ya fito.

Koda ya fito daga toilet din kuwa wani irin kamshin shower jel ne ke tashi ajikinsa, Yayinda kuma tausassun gashin jikinsa suka kwanta lub.

K'awataccen sajen dake kwance akan fuskarsa kuwa, shek'i take tayi saboda danshin ruwa dake jikinta.

K'arasawa gaban mirror yayi, tare da d'aukan mini towel ya shiga goge ruwan dake jikinsa.
Komai nasa da nutsuwa yakeyinsa.
Hakan yasa duk wanda zai kallesa sai yaji ya burgesa.

Had'add'en body lotion d'insa ya shafa, sai kuma turaren companyn Gucci daya shafa ajikinsa.

K'arasawa gaban drawern d'insa yayi, inda ya ciro wani riga da wandon companyn Ouchpan masu kyau da taushi.

Rigar irin long sleeve d'innan ne, sai kuma wandon daya kasance tight, Wato mai dan kama jiki, amma kuma irin jeans dinnan ne, masu yanayi da crazy.

Anutse ya zura kayan ajikinsa, tare da d'aukan wasu simple shoe ya zura akafafunsa.

Masha Allah! Ba k'aramin kyau kayan sukayi masa ba, kasancewar su black colour kuma shiyasa suka k'ara bayyana, hasken da fatarsa ta k'ara.

Ahankali ya d'an ciji jajayen labb'ansa, tare kuma dasa hannunsa ya shafa cikinsa dake kukan yunwa.

Fuskarsa ya d'an kwab'e tare da karyar da wuyansa gefe, Allah ya sani yunwa yakeji sosai. Domin har wani jiri jiri yakeji.

Wayarsa dake kan gado ya d'auka, tare kuma da nufan falon nashi kaitsaye.

Koda ya fito idanunsa ya sauk'e akan dining table din dake cikin falon, saidai kuma rashin ganin an ajiye masa abunda zaici ne yasa shi b'ata fuska, tare da d'an rausayar da idanunsa, cike da kasala da kuma yunwa ya nufo main falon nasu kaitsaye.

Acan b'angaren Jannart kuwa bata jima da kammala had'a abincin ba, kasancewar kuma garin

ana d’an yanayin zafi shiyasa, Koda ta kammala had’a abincin a tray, kaitsaye part dinta ta koma.

Wanka tayi da sabulun beauty touch, wanda yasa gaba daya jikinta ya d’au sassanyan k’amshin sabulun.

Bayan ta fito daga wankanne kuma ta shirya kanta, cikin wani had’add’en English wear gown, wanda kwata kwata bashi da nauyi, kasancewar kuma rigar tight gown ne shiyasa ya bayyana duk wani shape din jikinta.
Harta kan nipples dinta kuwa saida ya bayyana, sosai rigar tayi mata kyau, tare da k’ara bayyana tsararren surar jikinta.

Turaren oud mai kamshin gaske ta shafa ajikinta, bayan ta tubke dogon gashin kanta, wanda yasha kitson da Mamy tayi mata ne kuma, ta yafa wani mayafi mai kauri ajikinta, daya rufe duk wani shape dinta, tayi hakanne kuma saboda sanin da tayi cewa, akwai maza agidan.

Juyawa tayi Ahankali kuma Cikin nutsuwa ta fice daga cikin dakin.
Kaitsaye kitchine ta nufa, dan daukan abincin da ta dafa din.

Rayyern kuwa Ahankali yake saukowa daga matattakalan steps din.

Cikin nutsuwa da kuma d’aukar hankali yakeyin kowanne takunsa.

Ahaka yake saukowa daga kan steps din.
Hannunsa daure akan cikinsa, yana shafawa tare da d’an lumshe  idanunsa.

“Mamy Mamy!!”
Sunan Mamy yake kira ahankali, cikin kuma muryarsa da tayi sanyi sosai, saboda rashin k’arfi da kuma yunwan da yake fama dashi.

Adai-dai lokacin kuwa Jannart ta k’araso tsakiyan falon, Jin kamar muryar mutum ne kuma yasa ta d’aga kanta, karab kuwa Idanunta suka sauk’a akansa.

Kyawawan Idanunta ta d’an zuba masa, tare da soma Kallon shigar dake jikinsa, Wacce tayi masa kyau sosai.

Dai-dai lokacin kuma shima ya sauk’e idanunsa akanta.

Ahankali ya zame tare da zama akan steps din karshe dake kan matattakalan, idanunsa ya d’an lumshe tare dasa hannu ya dafe cikinsa,  wani irin numfashi yake sauk’ewa mai d’auke da gajiya, cikin sanyin muryar dake nuna gajiyawarsa ya k’wala kiran sunan Mamy.

“Mamy tana d’akinta.”
Jannart din ta bashi amsa, tare kuma da d’auke Idanunta daga kallonsa.

Idanunsa dake alumshe ya d’an bud’e, tare da k’ara d’aura hannunsa akan cikinsa.
Wanda yayi Dan ƙugin yunwa, har saida Jannart din ta jiyo sautin.

D’an kallonsa tayi, gaba daya duk ya marairaice, ya wani zama abun tausayi, da dukkan alama Yunwa ce ke wahalar dashi.

“Meye kike wani kallona haka kamar zaki cinyeni, ni yunwa nakeji.”
Rayyern din ya fad’a yana me sauke mayun idanunsa akanta.

Wanda kuma hakanne yasa tayi saurin dauke Idanunta daga kallonsa.

Batare kuma da tace masa komai ba ta juya, Cikin nutsuwa ta wuce kitchine.

Da idanu yabi bayanta, har saida yaga wucewarta cikin kitchine din kafun ya tashi ya dawo cikin falon.

Jannart kuwa tray da plates ta d’auko, tare da dawowa falon.

Ahankali ta sunkuya dai-dai zata ajiye tray din agabansa ne kuma, mayafin dake jikinta ya zame ya fad’i.

Saurin ajiye tray din tayi tare da juyawa da sauri dan daukar gyalen nata.

Juyawan da zatayi dinne kuma yasa, Rayyern din sauke Idanunsa akanta.

Ganin inda idanun nasa suka sauk’ane kuma, ya sashi saurin rumtse su, tare kuma da kawar da kansa gefe sabida gani yayi tamkar nimples ɗin ta zasu tsole mishi ido, kasan cewar batasa bra ba yasa breast ɗinta ke tsaye kam nimples ɗin sunyi tsaye cur motsin da take yasa duk ƙirjinta rausayawa kara rumtse idanunshi yayi sabida ganin abin da yakeyi duk da ya rufe idon.

Itakuwa Jannart cikin sauri ta d’auki mayafin nata ta yafa.
Saboda kunyan da taji ya lullub’eta ne kuma yasa ta kasa d’ago kanta ta kalleshi.

Ahankali ta bud’e food flasks din, roasted fish din ta zuba masa, sai kuma miyar kasen shima da ta zuba masa shi, awani plate na daban dasa mishi tuwo kwaya ɗaya.

“Gashi.”
Ta fad’a cikin wata irin sassanyar murya, still batare kuma da ta d’ago ta kalleshi ba.

Akasalance ya d’ago kansa, tare da mik’a hannayensa alaman ta basa plate din.

Sai Alokacinne kuma ta d'ago Kai ta kalleshi, kasancewar kuma tana d'an nesa dashi ne, yasa dole saida ta matsa gab dashi.

Ahankali ta d'an ajiye guiwowinta akan tattausan carpet din dake malale atsakiyar falon.

Hannayenta duka biyu ta sanya wajen Ganin ta mik'a masa plate din.

Ak'ok'arinta nayin hakanne kuma, batare da duk sun Ankara ba, Rayyern din yasanya hannunsa ta k'asa zai karb'i plate din, hakanne kuwa yasa shi sauk'e tafukan hannayensa, akan lallausan fatar hannayenta, masu tsananin taushi tamkar auduga.

Wani irin abu Jannart taji acikin jikinta, wanda har hakan yasa tsikar jikinta mimmik'ewa, lokaci daya kuma gyalen ta ya zame zuwa kan kafad'unta, hakan yasa lallausar sumar kanta ya bayyana.

Idanunsa ya d'an zubawa gashin kan nata, Yayinda ita kuwa ahankali ta zame hannunta daga cikin nasa tare da sanya hannu ta jawo gyalen zuwa kanta.

Dai-dai lokacin ne kuma Mamy ta fito daga d'akinta.

Ganin Rayyern da Jannart din atare ne kuma, ya sakata sakin murmushi Cikin kulawa tace.

"Babana lafiya kuwa Ina sallah naji kana ta rabka min kira."

D'agowa yayi ya d'an kalli Mamyn, cikin yanayin sigar shagwab'a yace.

"Mamy To ba yunwa nakeji ba."

Murmushi Mamyn tayi, tare kuma da neman waje ta zauna.
Cikin sakin fuska tace.

"To Rayyern Idan kanajin yunwa, baga matarka ba, komai ita zaka tambaya ba niba, kuma ga abincin ma, Ina naga ankawo ma,  Jannart sannu da aiki."

Mamyn ta fad'a tana Kallon Jannart, da ta janye jikinta daga kusa da Rayyern din.

D'an murmushi tayi, batare kuma da tace komai ba, ta dawo kusa da Mamyn nan k'asan sofa ta zauna.

Shikuwa Rayyern d'an k'aramin bakinsa ya taɓe, kana ashagwab'e cikin kuma yanayinsa na marar lafiya, ya soma cin abincin da Jannart din ta kawo masa.

Tun aloman farko da yayi kuwa, ya lumshe idanunsa, saboda dadi da kuma gardin kifin daya ratsa shi, bugu da kari ga kuma ruwan lemon tsamin da taste d'insa, ya hadu dana kifin sai ya bada wani dandano na daban.

Ci gaba dacin abincin nasa yayi, duk da cewar bata wani sa masa da yawa ba, saboda sanin halinsa da tayi na rashin son cin abinci.

Mamy da Jannart kuwa hira suke d'an tab'awa kad'an kad'an.

Wanda hakan yasa sam basu ma lura da cewar Rayyern din ya cinye abincin ba.

"Bank'oshi ba fa."

Maganar Rayyern din ya katse su daga hirar da sukeyi.

D'agowa Jannart tayi, karab kuwa idanunsu suka sark'e acikin na juna.

Saurin janye Idanunta daga kallonsa tayi, tare kuma da mikewa ahankali, ta k'arasa inda yake zaune.

Mamy kuwa Murmushin jin dadi tayi, tare kuma dajin wani sanyi aranta, saboda dama burinsu ne Ganin Rayyern din yaci abinci ya kuma fara sakewa da matarsa.

Jannart kuwa durk'usawa tayi agabansa, tare da daukan plate din, ta soma kokarin kara masa gasashshen kifin.

"Idan ba rowa bama tayaya za'a bawa mutum abunda ansan bazai ishesa ba."

Rayyern din ya fad'a k'asa k'asa ta yanda, yasan Jannart dince kawai zata iya jiyosa.

Aikuwa karab maganganun nasa, suka sauk'a acikin kunnuwanta kasan cewar tana kusa dashi ainun kuma hankalinta na kanshi.

Hakan yasa Ahankali ta d'ago Idanunta ta kalleshi.

"Malama meye?"

Ya tambaya yana me tsareta da idanu da tsuke fuska.

Fararen hakwaranta ta sanya, Ahankali ta ciji labb'anta, Cikin yanayin sanyi da kuma, yanayinta mai kama da shagwab'a, ta d'an maida bakinta gefe, alaman murgud'a baki.

Idanunsa ya d’an zaro, saboda ganin abunda tayi masa din,  duk da cewar kuwa hakan da tayi din, ba k’aramin k’ara mata kyau yayi ba, musamman saboda yanda lips dinnata suka sha, oil lipgloss.

“Me bakin rashin kunya.”

Yayi maganan k’asa k’asa, tare da motsa k’afarsa Ahankali,  wanda kuma niyarsa shine ya take mata yan yatsun k’afarta.

Dai-dai nan kuma Abba da Baba Maud’o suka shigo cikin falon.

Hakanne kuwa yasa shi maida k’afartasa.

Jannart kuwa plate din ta tura masa gabansa, tare da komawa baya ta zauna.

“Sannu da shigowa Abba, Baba Maud’o sannu.”

Jannart din ta fad’a cikin girmamawa.

Murmushi dukansu sukayi, kana cikin jin dadin girmamasu da Jannart din keyi, Baba Maud’o yace.

“Yauwa Jannart sannu, ya gidan?”

“Alhamdulillah.”
Ta amsa tana me dukar da kanta k’asa.

Abba ma fuska asake, yana me zama akusa da Rayyern din kuma yace.

“Yauwa Jannart, sannunki .”

Baba Maud’o ne ya kalli Rayyern din cikin kulawa yace.

“Maud’ona ya jikin naka.”

Murmushi Rayyern din ya d’anyi, kana cikin sakin fuska da nuna Jin dadin kulawar Baba Maud’on yace.

“Alhamdulillah Baba Maud’o yanzu kam jikin da sauki.”

“Masha Allah Allah ya kara sauki, dama nace bari nazo na duba ka.”

Baba Maud’on ya fad’a yana me mik’ewa tsaye.

“Ameen Nagode Baba Maud’o.”
Rayyern din ya amsa.

Shikuwa Baba Maud’o juyawa yayi ya fice daga cikin falon.

Hakanne kuma yasa Abba ma tashi yabi bayan Baba Maud’on.

Dai-dai lokacin kuma Riyyam nsra ya fito falon, hannunsa rike da wayarsa.

Anan kusa da Rayyern ya zauna, Ganin kuma irin delicious din da Rayyern din keci ne, yasa shi dan tand’e baki.

Cikin dan yanayin zak’uwa yace.

“Gaskiya Hamma Rayyern kana cin dadi, tun Ina sama nake jiyo kamshin abincin kan nan gsky My Aunty kina mana ƴan ubanci.”

Hararan wasa Rayyern din ya d’an watsa masa,  shikuwa Riyyam din wayarsa ya ciro, tare da dannawa numbern Ramadan kira.

Mamy da Jannart kuwa murmushi sukayi.

Bugu biyu kuwa Ramadan din ya dauka.

Cikin zak’uwa Riyyam din yace.

“Albishirinka Hamma Ramadan, yau kada Kaci komai awaje, ka dawo gida Aunty Jannart irin miyar ranan tayi.”

Daga can b’angaren Ramadan yace.

“Ai ganinan ma Ina dawowa, kace Aunty Jannart ta ajiyemin nawa.”

“To.”
Riyyam nsra din yace, daga haka ya katse kiran.

Rayyern kuwa d’ago kansa yayi ahankali, tare da Kallon Mamynsa cikin sanyi yace.

“Mamy d’azu munyi waya da Mammyn Riyyam tace tana gaidaki.”

Murmushi ne ya bayyana akan fuskar Mamy, cikin jin dadi tace.

“Masha Allah Ina amsawa.”

Juyo da kallonta ta kumayi inda ta sauke idanunta akan Riyyam nsra.
Cikin nuna kulawa tace.

“Ni kam Riyyam baka tab’a had’ani da Mammynka ba ko awaya, bani hotonta na gani mana Idan kana dashi.”

Murmushi Riyyam nsra din yayi, cikin tausasawa da jin daɗin satan amsar da Mamy ta bashi mgnar ta yace.

“Ayyah Mamy yi hakuri, amma babu hoton Mammy  awayana sabida randa zanzo na sai sabuwar waya kuma na bar waccar a gida.”

Ya kare maganar yana dan karyar da wuyansa gefe.

“To had’ani da ita mana muyi video call.”

Mamyn ta fad’a tana me kallonsa.

Wani irin bugawa yaji kirjinsa nayi, wanda hakan yasa shi sadda kansa k’asa.

“Tayaya zai had’a Mamy da Mammynsa video call?”

Yayiwa kansa tambayar.

Mamy kuwa Ganin yayi shiru ne yasa ta cewa.

“Lafiya kuwa Riyyam inayi maka magana kayi shiru, had’ani da ita muyi magana.”

Kansa ya d’an langwab’ar gefe, cikin kuma yarda da k’aryar da zuciyarsa ta tsara masa yace.

“Ayya Mamy d’azu muna waya dasu, naga kiran ya katse, ashe wai Zaytoon ce ta raɗa mata wayar a ƙasa, dana sake kira kuma baya shiga, saida ga baya Mammy kecemin wai, cameran wayan nasu ya samu matsala, saidai ko voice call.”

D’an Jim Mamyn tayi, kamar me nazartar wani abu kuma saitace.

“To Wayar Zaytoon fa?”

“Ai Zaytoon bata da waya, Mamy ta hana ta rik’e waya, tace wai bayanzu ba.”

Ya k’are maganan yana me waskewa, gudun kada kowannensu ya fahimci cewar bashi da gaskiya.

Kai Mamyn ta jinjina, kana cikin gamsuwa da bayanan nasa tace.

“Ai hakan da Mammyn naka tayi shine daidai, barin waya ahannun y’a Mace budurwa adai-dai wannan lokacin hatsari ne, kodan wannan babbar masifa ta Tiktok dinma, saidai Wacce Allah Ya kare kawai.”

Murmushi Riyyam din yayi, cike dajin dadin yanda karyar tasa ta samu karb’uwa kuma ya samu sun kauda mgnar ma.

Rayyern kuwa mik’ewa yayi, saboda dama ya kammala cin Abincin.
Anutse ya nufi sama, saboda surutun nasu na damunsa.
Har ya fara haurawa yace.
“Uhum Mamy ai su kansu yara masa basu waya da barinsu yin shuhura a social media babbar masiface, yanzu kigafa yadda Riyyam-nsra yake kamar mazari, wanda  a baɗini kuma Allah ne kaɗai yasan me yake shukawa”.
Ya ida mgnar ya juyowa ya tsurawa Riyyam-nsra ido.
Wanda shi kuwa yayi wani irin firgita dan sai yake ga Hmma nasu ya gane komai da yakeyi ne.

Mamy kuwa cikin yarda da yaron tace.
“A babu ma abinda yakeyi”.
Uhum kawai yace yaci gaba da tafiyarsa.

Tashinsa awajenne kuma yasa ita kuwa Jannart sakewa,  bayan ta gyara wajen da yaci abincin ne kuma ta dawo, suka zauna ita da Riyyam hira suka sha sosai, suna nan zaune dai har Ramadan ya dawo.

Bayan sunyi sallan magriba ne kuma, Jannar din ta zuba musu sauran ragowar abincin Rayyern din sukaci.

After 3day.

Alhamdulillah acikin kwanaki ukun nan, jikin Rayyern ya k’ara sauki sosai, domin babu laifi yanzu ya samu karfin jikinsa.
Domin yana iya fitowa har can compound din gidan, wajensu Baba Maud’o, sannan har motsa jikinsa yana iyayi yanzun.

Ab’angaren Jannart kuwa tun ranan bata sake sakashi a ldanunta ba.
Sosai kuma takejin dadin zaman gidan, musamman ayanzu da duk sanda Ramadan  ya dawo, sukan zauna suyi hira sosai, harma game sukeyi.

Ga kuma wayarta dake d’ebe mata kewa, kasancewar ta bud’e Twitter, Instagram, da kuma Tiktok, da wani suna na daban, bawai original account dinta da kowa ya sani ba, sunan da ta bud’e dashi kuwa, ba wai normal sunane da kowa zai gane ba.
Akomai nata da Unique kawai take using.

Acan b’angaren gidan su kuwa.

Har dai zuwa yanzu babu wani mai gamsashshiyar nutsuwa acikinsu, more especially Alhaji Idi Sale dakata.
Momy da kuma Abdull, wanda abun ya had’e musu biyu, rashin lafiyar Dadyn da kuma b’acewar Jannart.

Yanzu ma zaune su Alhaji Idi Sale Dakata, Alhaji Abdu Tababa, Dr. Lukaman, da kuma Barrister Kabir, Alhaji Bala Tamnari suke acikin katafaren dakin ganawa'n Alhaji Idi Saleh Dakata.

D’ago da kansa yayi ya kalli Alhaji Bala Tambarin, cikin dan yanayin damuwa yace.

“Wato Alhaji Bala, har yau ina mamaki kan al’amarin daya shafi yaron nan Rayyern, musamman akan company’s d’insa, akullum hab’aka abubuwan nasa sukeyi, na kuma rasa gano tushe da madafan arzikinsa, saboda ayanzu haka nasa ayimin bincike akan sabon companynsa, ankuma tabbatarmin da cewa, zuwa yanzu ankawo komai da komai na amfani acikin companyn, kama daga kan engines dama dai sauran abubuwa, saboda har anfara sarrafa kayayyakin abinci, amma naji ance bazasu fara fitar da kayayyakin nasu ba, sai farkon shekara mai kamawa ina mamakin dukiyar yaron dan a iya wannan Company nasa zaikai biliyoyin kuɗi da sunfi shekarunsa yaushe aka haifesa har ya yarasu.”

Kai Alhaji Bala Tambari’n ya jinjina, cikin gamsuwa kuma yace.

“K’warai kuwa nima nasan da haka Alhaji Idi Saleh Dakata.”

Gyara zama Alhaji Abdu Tababa yayi, kana cikin takaici yace.

“Wannan abu ni Ina mamakinsa, amma Meyasa ba zaka dakatar dasu ba Alhaji Bala? Naga Kaike kula da duk wasu harkan filayen da ake gine gine masana'antu, ni har yauma ina mamakin tun farko ma meyasa ka basu takardar izinin fara ginin companyn?”

Murmushi Alhaji Bala Tambarin yayi, saboda shi yasan meya sani, kamar yanda suka kasa gane waye, Dr. Rayyern Bashir Muhammad Mai-nasara din, to shima hakane.

Dr. Lukman ne ya cab’i zancen da cewa.

“Gaskiya dai kam, amma ni yanzu sauki na daya, abubuwanshi na harkar asibiti gaba daya sun dakata, yafi maida hankalinsa, akan abubuwan da suka shafi companyn.”

Barrister Kabir dake zaune agefe ne ya saki wani  murmushin jin daɗi.

Tare da gyara zamansa, Cikin nutsuwa yace.

“Anaka tunanin kenan Dr. Lukman, domin da alama baka da labarin cewa, acikin kwanan nan akwai likitotinsa da ya ware kusan guda biyar dashi na shida, way’anda zasu tafi Russia Mascow yin wani course, baya ga haka kuma Idan sunyi wannan course din sun dawo, akwai ci gaba na musamman wanda za’a samu, a hospital din nasa, domin zasuje suyi course dinne, akan abunda ya shafi dashan k’oda, dana zuciya aikin ƙwaƙwalwa da juyen jini ga masu cutar sikila uwa uba da safarar tunanin kwakwalwar ɗan Adam, dama dai sauransu, kuma Insha Allah zasu kawowa K’asa cigaba.”

Idanu Dr. Lukman ya d’an zazzaro, cikin bakinciki takaici da kuma kunci yace.

“Wallahi kwata-kwata Barrister bani da wannan labarin, kuma ai wannan plant din nima, najima da tsarashi azuciyata, wanda kuma nakeso na aiwatar acikin hospital dina, amma kuma sai next year nakeson haka, why? Why? Wannan yaron ya shigemin hanci, komai zanyi saiya rigani kafin ma in tuna abu shi yayi, na shiga uku Anya zai barni na ci gaba arayuwata kuwa?”

Dr. Lukman din ya fad’i  haka cikin tashin hankali, saboda ya fahimci cewa, duk saurinsa Dr. Rayyern din yana gaba dashi akan komai.

Boyayyen Murmushi Barrister Kabir yayi, tare da maida kansa ya ajiye ajikin kujera, yayi hakanne kuma saboda yanda yaga, hankalin Dr. Lukman din ya tashi sosai.

Alhaji Bala Tambari kuwa, gyara zamansa yayi...!

*Albishirinku! Ma'aurata, GA GARKUWAR KU nan tafe muku da tsarabobi na musamman gareku ma'aurata daga cibiyar mgnin mata mai taken  GARKUWAR MA'AURATA*

NI DAI AYSHA ALIYU GARKUWA.
Ina matukar mamakin wani irin lokaci da ya riske mu mai wahalallan fassara. Kullum dai magana daya ce, akan ma’aurata, fada, rashin jituwa, mutuwar aure, akan kuskure kalilan, rashin kula, rashin yi wa juna uziri. Toh wai duk me ya janyo hakan? Na zurfafa a tsananin tunani hakan ya tilasta min bincike mai tarin yawa wanda ya kai ni ga gano inda matsalar take? Shin yar’uwa ke macece amma kin san wacece mace ku? Kin san me ake kira mace kuwa? Mace ita ce matar da take zama iyali a wajan namiji ta zame masa bango, sanyin idaniyarsa, ta zame masa gata da farin cikin rayuwarsa ta zame masa ruwa abar kore ƙishinsa ta zame masa

mayafi mai karesa daga gigitar kadaice, ta kuma dorar da mijinta kan turbar gaskiya, ta kashe masa jiki da salonta ta rikita shi da baiwa da ni'imar da Allah ya bata idan har ta san hanyar mayar da kanta sabuwa dal awajanta, wato kullun takasance masa tamkar amarya har ya kasa tantance daren amarcinsu da sauran dararen rakun rayuwar su.

Wannan ita ce mace. Ina da wata saukakkar hanyar da zaki zama abar so da kulawa da soyayya a wajan mijinki ta hanya mafi sauki, 09097853276 hanyar ita ce ki gwada amfani da kayana na gyara ki gani, ina mai tabbatar miki da in sha Allahu sai kin dara da murna sai kuma kin gode min. Kayana kaya ne da aka yi shi da zallan itacanmu na gado marasa illa a cikin jikin dan adam musamman mace, kaya ne da suke taimakawa (sex hormones 😍) dinki.
Misali kina kallon India😘, hollywood, Asian film🥰 kina ganin yanda mazansu ke nunawa matansu tsananin soyayya kamar su ba su kyautar ransu!?
Saboda me hakan? Saboda suna sadaukar da lokacinsu wajan gyara jikinsu da kayan da ke tsattsafo da ni'ima cike da tsukewa, kayan nan kuma ana yinsu ne zallar magungunan gargajiya wanda ba su da illa domin haɗine na ingantattun itatuwa da yayansu.
Ina baiwar Allahn da miji ke daure mata fuska babu hirar arziki?
Zo ki ji yar'uwa zan baki gumbata da zallar gari wanda aka yi su da nagartattun itacen da ke da matukar amfani a jikin mace. Gubar ciko, gumbar tsalle dole, gubar da ba'a baiwa mai kishiya, garin maɗi, garin mallaka, tsumin goron tula, tsumin tsartai, tsumin maratsi, pala-pala butar sirri, kwanon k'asaitacciyar mace, furar mata madadararta gareki Hajia takenta sha yanzu mgni yanzu, Ina mata masu fama da sanyi? Sanyin mara ki zo na hadaki da magani na na sanyi wanda yake wanke mara ya fitar da duk wata cuta da ke samun mazauni a wajan.
Ina da ciccibi mai kyau. Ina da hadin amare mai kyau wanda zai gyara yarinya ya kankaro mata kimarta akwai hadin mai jego wanda muke yinsa na asali inada kekkyawan Hadi maida tsohuwa yarinya.

Akwai daya bangaren wato *KAMSHI*
Kimarki gyaranki da kamshinki. Matan da suka gane suka san yanda za su kankaro da mutunci su ne masu amfani da kayan gyara da kuma sanyaya jikinsu da kamshi, ina da turaren wanka da na bandaki na daki na jiki da na kaya dana tsuguno kamshin turarena na dabam ne mai sanyaya zuciyar wanda ya shaka ina da kayan kamshi na amarya da na maijego da na uwargida da dukkan macen da take kokarin mayar da kanta mai daraja a idon kowa ta zamo sarauni a idon mijinta, akwai shu'umar humra, sayan na gari maida kuɗi gida, banda karanta yayin gyara Hajia.

Zaku iya samun kayyakina a duk garin da kike, zakiyi min mgn ta whatsApp number na 09097853276 domin yin zaɓinki, ko karin bayani, zaki tura kuɗin ta account na 0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU in mun gama mgna zan sa miki kaya a mota yazo duk garin da kike, in baki shirya saya yanzuba Please kada mu wahal da juna ki bari sai kin shirya kafin kiyi min mgn.

🤝🏻🥰😘 Daga taku AYSHA ALIYU GARKUWA

*(GARKUWAR MA'AURATA)*

By
*GARKUWAR FULANI*

22/12/2021, 19:45 - 🥰🥰: Jannart suuu suka tafi, cikin tsoron kaiwa k'asa Jannart ta sanya hannayenta akan damatsan sa, tare da rikesa k'am, kana ta rumtse Idanunta da masifan karfi.

Aikuwa duk da yin hakan da tayi bai hanasu kaiwa k'asa ba, cikin abunda bai wuce 1second ba gaba d'aya duk suka zube awajen saidai shi ya koma kasa ita a sama.

"Auchhhhh!!"
Rayyern ya fad'a da k'arfi tare da rumtse idanunsa.

Wanda ya fadi hakanne kuma saboda buguwan da yayi, ga kuma Jannart da ta fad'o saman k'irjinsa wacce tsoro yasa ta maƙalƙale masa.

Jannart din ma wani siririyar k'ara ta saka, musamman da kirjinta ya bugu ajikin nasa kirjin sosai taji tsayayyun breast ɗinta sun bugi kirjinsa.

Atare duk suka rumtse idanunsu, saboda zafin fad'uwar da sukayi ne kuma, yasa duk kowannensu ya kasa yin k'wakk'waran motsi.

Still Har yanzu kuwa hannayen Jannart nakan dantsen hannunsa, tayi masa wani irin rik'o dake bayyana tsoronta.

Yanayin yanda suka kasance ahaka dinne kuma yasa, d'an kunnen Jannart din mak'alewa da gaban rigarsa, Ahankali ta d'an d'aga kanta, saidai jin rigar tasa ya kama d'an kunnenta ne yasa ta kasa d'agowan, saboda wani zafi da taji.

Dai-dai lokacin kuwa gaba d'aya duk wani haske dake cikin d'akin ya d'auke, saboda d'auke wuta da akayi sabida iskar data turbude garin Kano baki ɗaya, ga kuma yanayin garin kwata kwata babu wadataccen haske yayi duhu.

Shi kuwa Rayyern al'amarin ya magaga ya zarta zatonsa ya kama hanyar wata fitinenneyar duniyar da bai san sa ita,
Sabida yadda yake jin wasu irin masifaffun abubuwa suna tsikarinsa sabida yadda yaji sauƙan Cabɓullenta bisa nasa ƙirjin.
Wani irin maraitaccen numfashin yaja can ƙasan maƙoshinsa tare cusa kanshi tsakanin wuyanta da kafaɗarta wani numfashin ya kuma sha sabida sassayan ƙamshinta da ya zuƙa.

Idanu Jannart ta d'an rumtse, cikin gajiya da kuma zafin da take d'anji ajikinta, ta d'an sake matsar da kanta saman kirjinsa, wanda kuma burinta shine ta samu ta zare d'an kunnenta daga

jikin rigarsa.

Hakan da tayi d'inne kuma ya bata daman jiyo bugun zuciyarsa, wanda take tafiya da sauri sauri dib-dab-dib-dab.

Idanunta ta d'an lumshe tare da soma d'an jujjuya kannata, dake kwance saman kirjinsa, saboda ta kosa dan kunnen nata ya fita.

Shikuwa Rayyern dake kwance ak'asanta, hannunsa d'aya yasa ya kama gefen ba yansa, tare kuma da lumshe idanunsa, Ahankali k'amshin dake fita ajikinta, da kuma wanda ke fita acikin gashinta ke ratsa cikin hancinsa.

Sosai yake iya jiyo bugun zuciyarta daga cikin kirjinsa.

Idanunsa ya kuma rumtsewa adai-dai lokacin da yaji tana murza kanta akan chest d'insa.
Lokaci d'aya kuma yaji wani irin abu nabin kowani sashi na jikinsa.
Yaarrr yarrrrr haka tsikar jikinsa ke zubawa, Yayinda duk wani kofan gashi na jikinsa, ke bubbud'ewa.

Tun da yake aduniyarsa bai tab'ajin hakan ba, bai kuma san menene hakan ba, sai ayanzu da yaji yanda d'umin numfashin Jannart d'in, ke dukan wuyansa, ga kuma yanayin yanda yaji tana juya kanta akan kirjinsa, da wani irin salo.
Bugu da k'ari for the first time daya tab'a kasancewa da Mace haka, tunda yake aduniya hakan bai tab'a faruwa dashi ba sai yau, bai tab'ayin kusanci da Mace sosai haka ba bai tab’a sanin ya ake fuskanta ba in anyi kusanci da juna.

Idanunsa ya d'an sake rumtsewa, tare kuma dasa hakorinsa ya ciji jajayen labb'ansa.
Kwata kwata bazai iya jurewa kasantuwarsu ahaka ba, domin shi kam awajensa hakan bak'on lamari ne, da bayajin k'wak'walwarsa zata iya d'auka saboda abubuwan masu yawa ke ɗaurewa da kwancewa a sasan jikinsa.

D'an yun k'urawa yayi da niyar tashi, amma sai yaji ya kasa, saboda Jannart din dake kansa, da kuma bayansa wanda ya d'an rik'e.

"Wayyo Allah, ke ki tashi akaina mana, ko doki kika samu ne?"

Ya k'are maganan da wata irin fitinenniyar murya yana me taune lips d'insa.

Jannart dake kwance akansa kuwa, Jin abunda ya fad'a d'inne kuma yasa ta turo d'an k'aramin bakinta, gaba Cikin yanayin shagwab'a tace.

“Ni bazan iya tashi ba, d'an kunnena ya mak'ale ajikin shirt dinka, Idan na tashi da k'arfi kuma kunnena zai yage."

"To ya yage din mana sai meye, nidai da halla malama tashi akaina, da nauyinki zanji Koda zafin fad'uwan da nayi, Dan mugunta ma ai ke ya kamata ki fad'a k'asa ba niba."

Ya fad'a yana me yunk'urin tashi zaune.
Hakanne kuma yasa Jannart din sakin wani k'ara tare da manna kanta da ƙirjinsa da kyau kana ta kara rumtse damatsan hannunsa, saboda d'agowan da yaso yi ya sa tajin kunnenta zafi sosai.

"Auchhh kunnena."
Ta fad'a cikin wata irin shagwab'abbiya kuma kasalalliyar muryar, daya sashi komawa ya kwanta lib.

Hakan ko yasa ta ɗan ɗago, sai kuma tayi maza ta sake fad'awa jikinsa, saidai awannan karon atausashe kirjinta ya fad'a kan nasa.

Wani irin shocking yaji  tun daga k'asan k'afarsa, har zuwa tsakiyar madigan kansa wanda hakan yasa Rayyarn nasa wani irin masifeffen harbawar daya sashi furta.
“Aushhhhhyyyyyohhhhh”.
Yaja sautin da karfi dan abin yazo masa a bazata.

Taushi da kuma tudun tagwayen abu biyu masu kamar audugan da yaji
Akan kirjinsa ne,  yasa shi rumtse idanunsa da sauri, tare kuma da dunk'ule hannayensa.

Lokaci d'aya kuma numfashinsa ya soma wani irin fusga,  Yayinda zuciyarsa kuwa ta shiga bugawa a millions.

"Yah Salam  wayyoooooooo Allah na ni mema ya shigo dani wannan jarabebben d'akinne? Why Rayyern Why?"

Ya fad'i hakan azuciyarsa, yana mejin tamkar yasanya hannayensa ya tureta, ko hakan zai sa ya daina jin abubuwanda yakeji na game dukkan sasan jikinsa gaba ɗaya, wanda kwata kwata arayuwarsa baima sansa ba to amman kuma haka nan sai yaji ya kasa baya son tureta, sai yakeji tamkar su tabbata a haka.

Jin sautin  bugun zuciyartasa ne kuma, yasa Jannart d'an d'agowa, saidai bata wani Kallon fuskarsa da kyau saboda duhu.

"Meyasa zuciyarsa ke bugawa fast fast haka?"

Tayiwa kanta tambayar, dai-dai lokacin kuma Cikin ikon Allah ta samu ta zare d'an kunnenta daga jikin rigar tasa.

Hakanne kuma ya bata daman d'ago Kanta, tare da mirginawa cikin sauri ta sauk'a ajikinsa.

Jin ta sauk'a daga jikinsa ne kuma, yasa shi sauk'e wani irin ajiyar zuciya tare da mikewa tsaye cikin sauri wani irin haushin saukan nata daga jikinsa ne ya rufesa har kamar ya saki kuka.

"Mcheeeww mutun sai nauyi kamar dutse."

Ya fad'a abayyane yana me shafa bayan rigarsa, dake Jik'e da ruwan.

Jannart kuwa duk da cewar baya ganinta, sosai baki ta murgud'a masa, tare da d'aukan wayarta tamik'e tsaye.

Kaitsaye d'akinta ta wuce, domin shima Rayyern din yana tashi, baijirayi komai ba ya nufi hanyar fita daga cikin dakin.

Ahankali yake tafiya yana d'an ciccije bakinsa, har ya gama fitowa daga part din Jannart din.

Dai-dai ya fito falonne kuma idanunsa, suka sauk'a akan Abba dake zaune bisa kujera.

Hakanan yaji kirjinsa ya buga, lokaci d'aya kuma yaji wani irin masifeffen kunya Abban nashi ya kamashi, akaro na farko kuma kenan yanzun, agaba d'aya rayuwarsa da yaji kunyan Abban nasa ta kamasa.

Tamkar wani marar gaskiya haka yayi k'asa da kansa, kana cikin sanyi ya taho sad'ab sad'ab ya haura sama sam ya kasa ya mishi mgn, sai yakeji tamkar Abba yaga abinda ya faru.

Da kallon mamaki Abba yabi bayan Rayyern din, musamman da yaga yanda bayan rigar Rayyern din, ke jik'e da ruwa, wanda kuma shi a iya saninsa, ko digon yayyafi ba'ayiba balle ko yace shiya jik'a Rayyern din.

Ajiyar zuciya kawai Abban ya sauk'e, tare da mik'ewa shima yayi b'angaren sa.

Rayyern kuwa yana haurawa sama, rigar dake jikin nasa ya cire.

Tare da sanjata izuwa wata, Ahankali ya d'an zauna abakin gadonsa tare da jawo Laptop d'insa ya soma hidimar tafiyarsu Mascow.

Saidai gaba daya ya kasa daina jin k'amshin Jannart din acikin hancinsa.

D'an rumtse idanunsa yayi, tare kuma da bud'esu alokaci guda, cikin d'an yanayin k'osawa yace.

"Fitinanniya."

Acan b'angaren Jannart kuwa Koda ta shiga d'akinta, kwanciya tayi lub akan gado, tare da d'aukan wayarta ta soma buga game.
Duk yanda taso maida hankalinta akan game din kuwa abun yaki, domin hakanan takejin k'amshin jikin Rayyern din, ya kasa barinta tayi sukuni, duk da cewar baya wajen amma mayen kamshinsa yana wajen.

Fuskarta ta d'an ya mutse, tare da shagwab'e murya, cikin kasa da murya tace.

"Ai duk shiya jawo muka fad'i, da wani k'amshinsa awajen."

Yanayin yanda tak'are maganan tana murgud'a baki, Idan ka gani zakayi tunanin agabansa take.

Almost 40minute kuwa ana tsula iska kana hadarin gaba d'aya ya washe, dai-dai lokacin kuma aka soma kiraye kirayen sallan magriba.

Atare duk mazan gidan suka wuce masallaci, Abba, Rayyern Ramadan da kuma Riyyam-nsra.

Acan suka iske Baba Maud'o ma, wanda shi yakan riga ma kowa dake gidan tafiya masallaci.

Koda sukayi sallan magriban kuwa, basu fito daga masallacin ba har saida suka sallame sallan Isha.

Koda suka dawo gida, anan kan dining table suka zauna, Yayinda Abba kuwa ya wuce sashinsa kaitsaye.

Mamy ne takai masa abincinsa, Ramadan da Riyyam-nsra kuwa Jannart ce tayi saving d'insu.

Ubangayyan kuwa bai hawo kan dining table d'in ba, anan cikin falon ya zauna, batare kuma daya ce akawo masa nasa abincin ba.

Itakuwa Jannart tana sane dashi, amma saita share batare da ta tambayesa ko yana buk'atar abinci ba, ta nemi waje ta zauna, tare da soma tsakalan abincin da ta zubawa kanta.

Rayyern dake zaune kuwa Ganin Mamy ta fito daga b'angaren Abba ne, yasa shi mik'ewa tsaye.

"Babana kai bazakaci abincin bane?"
Mamy ta tambaya da kulawa.

Fuskarsa ya d'an yamutsa, cikin kuma halinsa na rashin son yawan mgn daya tashi masa yau din yace.

“Ba'a bani ba”.
Yanayin yadda yayi mgnar yana kuma kallon Jannart ƙasa-ƙasa ne yasa, Mamy yin murmushi tare da cewa.
“To bari a kawo maka”.
Cikin kauda kai yace.
"No Mamy ni nakoshi."

"Amma Babana kafasan baka jima da tashi daga ciwo ba, Meyasa bazaka maida hankalinka wajen cin abinci akan lokaci ba?"

Mamyn ta fad'i haka cike da nuna masa, tsananin soyayyar da takeyi masa.

D'an marairaice fuskarsa yayi,  hakan yasa yayi tamkar k'aramin yaro.

"Seriously Mamy nak'oshi ne, kuma anjima zansha tea, yanzu bari naje wajen Abba."

Ya k'are maganar yana me nufan sashin, Abban kaitsaye.

Mamy kuwa da Idanu ta bishi har saida ya shige part din Abban, kafun ta janye idanunta tare da dawowa kan dining table din ta zauna.

Ahankali Rayyern ya tura k'ofar d'akin Abban ya shiga bakinsa d'auke da sallama.

Abba dake zaune akan carpet, yana cin abinci ne ya d'ago kansa, tare da amsawa Rayyern din sallaman, fuska asake yace.

"Rayyern shigo mana."
Abban ya fad'a cikin kulawa.

K'arasowa cikin falon Rayyern din yayi, tare da matsowa ya rusuna agaban Abban nasa, cikin girmamawa had'i da ladabi yace.

"Abba barka da warhaka."

Kai Abban ya jinjina, tare da d'aukan d'aya daga cikin spoons d'in dake, kan tray din abincinsa ya mik'awa Rayyern din.

"Muci abinci."
Abban ya fad'a cike da kulawa.

Kansa ya d'an rausayar gefe, tare dasa hannu ya shafa cikinsa, cikin sanyi yace.

"Abba nak'oshi."

Kallonsa Abban yayi kamar zaice wani abu kuma saiya fasa, saboda dama yasan halin Rayyern cin abinci akai-akai bawai ya wani damesa bane sai daifa idan ya ritsa abinda yakeso ba sauki.

Rayyern kuwa d'an gyara zamansa yayi, tare da fuskantar Abban nasa, cikin muryar dake nuna girmamawa yace.

"Abba dama akan maganan tafiyarmu Mascow ne”.

D’an zuba mishi ido Abba yayi kana ya dauki cup ruwa ya dan sha kana ya aje tare da cewa.
“Uhum ina jinka".
Gyara zamansa ya danyi tare da ci gaba da cewa.
“Yanzu mun kammala komai ranar tafiyan nata matsowa, kuma Ina d'aya daga cikin way'anda zasu tafi, saboda ni nema zanyiwa sauran Doctor's din jagora,  da nayi tunanin bazanje ba, amma kuma sai naga zuwan yana da muhimmanci, saboda akwai babban likita daya daga cikin malamaina nacan, daya nunamin dacewar zuwan nawa, tunda duk way'anda zasuje din ak'ark'ashin kulawana suke, To ya kamata na kasance tare dasu."

D'an dakatawa da cin abincin Abba yayi, tare kuma da d'ago kansa ya kalli Rayyern din, cikin gamsuwa yace.

"Masha Allah, ashe har tafiyar tayi kusa, zuwa nanda yaushe ne zaku tafi?"

"Nan da sati biyu Insha Allah."

Kai Abba ya jinjina tare da cewa.
"Allah ya kaimu, amma naji ku biyar zaku tafi, saidai ka manta masauk'inmu da yake can, wajen zaman mutum biyu ne kawai sai inga kamar zaku takuru a ɗan gidan tunda ba wani babba bane."

Kai Rayyern din ya jinjina tare kuma da gyara zamansa, cikin kwantar da murya yace.

"Eh Abba, su sauran staffs din namu, hotel zamu kama musu, nida Usman P.A ne kawai zamu zauna, anan gidan."

Kallonsa Abba yayi cikin dan yanayin mamaki yace.

"Kaida Usman P.A kuma?"

"Eh Abba, dashi zamu tafi saboda nasan zai d'an ragemin wasu ayyukan."

Rayyern din ya fad'a atausashe, daga cikin zuciyarsa kuwa yana tsoron kada Abban, nasa ya

shigo da wata buk'atar.

Abba kuwa kansa ya girgiza, tare da cewa.
"A'a kam bada Usman P.A zaka tafi ba, da matarka zaka tafi."

Azabure Rayyern din ya d'ago kai, tare da zaro idanunsa ya kalli Abban, cikin yanayin kad'uwa yace.
"What Abba...."

D'aga masa hannu Abban yayi alaman dakatarwa, cikin nuna masa gaskiya da kuma hakikanin tabbacin magananansa yace.

"Na maimaita da matarka zaka tafi Rayyern, ba kuma zan sanja magana ba, saboda banason irin abunda ya faru dakai a China ya sake faruwa,   Ina da tabbacin cewa matarka zatafi kula dakai, fiye da Usman P.A, domin shi ba ad'aki d'aya zaku dinga kwana ba, kaga bai zama lallai yasan awani hali kake ciki ba a cikin dararen zamanku a can,  amma matarka fa tana tare dakai akoda yaushe, Dan haka za tafi kowa, sanin wanne hali kake ciki."

D'an numfasawa Abban yayi, kana cikin kulawa yaci gaba da cewa.

"Lafiyarka tafi mana komai Rayyern, akoda yaushe bama son duk wani abu na cutarwa dazai sameka, saboda haka bazamu tab'a barinka ka kasance awata duniya, Kai kad'ai babu wani mai baka kulawa ba."

Fuska Rayyern din ya kwab'e, lokaci d'aya kuma yaji komai duk ya daina yi masa dad'i, bakinsa ya bud'e ahankali da niyar yin magana.

Saurin dakatar dashi Abban yayi,  cikin tsare gida yace.

"Kada kace komai Rayyern domin wannan Umarni nane, bawai shawara ba."

Abban ya fad'i haka cikin tsare gida, tare kuma da jajjadada umarninsa.

K'asa Rayyern din yayi da kansa, tare kuma da d'an marairaice fuska cikin sanyi yace.

"Kayi hakuri Abba bawai Ina ja da umarninka bane, amma Barrister Kabir yace baya son kowa yasan cewar tana nan gidan, Koda kuwa zuwa nan da compound d'in gidan ne."

"Nasan da hakan, shiyasa ma tafiyar da zakuyin babu wanda zaisan kun tafi tare, tunda bawai da kowa da kowa muke mu'amala ba sannan kuma tafiyarku tare kamar wani matakin tsaretane."

Abban ya fad'a yana me gyara zama danci gaba dacin abincinsa.

Rayyern kuwa badon yaso ba, haka ya mik'e tare da yiwa Abban sallama, kaitsaye ya fice daga cikin falon.

Direct main falo d'insu ya nufo.
Dai-dai lokacin kuwa Mamy da Jannart d'in ke zaune,  inda Mamyn ke kan sofa, sai Jannart dake zaune ak'asa tana latsa wayarta.

K'arasowarsa cikin falonne kuma, ya sanyashi kama k'ugu, tare da Kallon gefen da Jannart d'in take, k'asa k'asa ya watsa mata wani kalon da bai san manufarsa ba.

Cikin kuma yanayin shagwab'a ya kalli Mamynsa, tare da karyar da wuya, asanyaye yace.

"Mamy inason muyi magana."

Jin abunda ya fad'a d'inne kuma yasa, Mamy d'agowa ta kalleshi.

"Magana kuma Rayyern, to inajinka."
Mamyn ta fad'a tana me maida hankalinta garesa.

"No Mamy dake kawai nakeson magana."

Ya fad'i hakan cikin gatse da kuma gayya, tare kuma da sake hararan Jannart k'asa k'asa, wanda ita batama san yanayi ba.

Mamy kuwa jin abunda ya fad'a d'inne yasa ta, Kallon Jannart dake zaune, ganin kuma gaba d'aya hankalin Jannart din ba akansu yake bane, yasa Mamyn mik'ewa, cikin nutsuwa tace.

"To mu haura sama."

Ai kuwa kaman jira dama yake tuni ya shige gaba, Mamyn na biye dashi a baya.

Suna shiga cikin falon nasu kuwa ya juyo, tare da Kallon Mamyn nasa, cikin son isar mata da k'orafi yace.

"Eyyah Mamy kiji Abba fa, wai  da wancan yarinyar yakeson naje Mascow, Mamy takurani zatayi Allah, ni kuma Mamy banason takura, yanzu meye laifi Idan na tafi da Usman P.A?."

Murmushi Mamy tayi, tare da kallonsa Cikin kulawa tace.

"To meye abun damuwa acikin wannan Rayyern, ka tafi da ita mana, kuma kasan baka isa tsallake umarnin mahaifinku ba, Lallai dole abunda yace shi za'ayi, kuma nima bani da wani ja akan hakan."

Fuskarsa ya shagwab'e tare da karyar da wuyansa gefe,  cikin sanyi da rashin samun k'arfin guiwa yace.

"To yanzu Mamy Dan Allah kiyi wani abu mana."

"Ni babu abunda zan iya Rayyern, kasan waye Abban ku Idan yayi magana baya tab'a sanjawa, nima kuma Ina goyan bayan hakan, saboda hujjar daya kawo hujja ce mai kyau."

Mamyn ta fad'i hakan cike da son jaddada masa yiwuwar hakan.

Shikuwa Rayyern gane akan maganar tasu babu wani sauyi ne, ya sashi juyawa tare da neman waje ya zauna.

Mamy kuwa kanta kawai ta girgiza, tare da juyawa ta fice daga falon.

Kaitsaye falon k'asa ta nufa, anan. Ta iske Ramadan da kuma Riyyam-nsra wanda yanzu shigowansu, kasancewar bayan sunci abincin daren sunfita wajen su Baba Maud'o.

Ganin sunata hira ne kuma yasa Mamyn wucesu,  kaitsaye ta nufi b'angaren Abba.

Su kuwa su Ramadan sun jima suna hira, kafun daga bisani Jannart ta wuce d'akinta, Ganin hakanne kuma yasa suma duk suka watse.

D'aki suka koma inda kowannensu ya rungumi wayarsa,   Musamman Riyyam-nsra da ya sakeyin wata sabuwar budurwa, y'ar k'asar Nigeria kuma y'ar nan cikin garin kano, wanda ta nace masa akan cewar tana son su had'u.

Shikuwa Ganin yanda take tura masa wasu part, daga cikin body dinta ne yasa shi, bata duk wani attension d'insa.

Saidai kuma gaba d'aya ya kasa, sanin wani karya zaiyi, Dan samu ya fita ko zuwa hotel ne su had'u da yarinyar dan sam Rayyern ya saka masa takunkumi.

Acan b'angaren Jannart kuwa, tana shiga d'akinta kwanciya tayi,  kasancewar ta gaji ne kuma yasa cikin mintuna kad'an bacci ya d'auketa.

Washegari

kamar kullum ita ta taya Mamy duk wasu aikace akace, bayan sun kammala breakfast bayan taci nata ne, kuma ta koma daki ta kwanta.

Ab'angaren Rayyern kuwa tun  6 ya wuce hospital, saboda akwai wasu patient da yake son dubawa.

Bayan kuma Rayyern din ya tafi ne kuma, Ramadan shima ya mara masa baya, saidai yau harda Riyyam-nsra suka tafi hospital din, saboda shi yace bayason zaman gida.

Ganin duk gidan yayi shiru ne kuma, yasa Mamy da Jannart watsewa afalon suma.

Rayyern kuwa bashi ya dawo gidan ba, sai bayan oppsallan magriba.

Bayan sunyi sallan Isha ne kuma duk suka shigo gida.

Bayan sun kammala Diner ne kuma, suka dawo cikin falon suka zauna.

Jannart ce ta fito daga cikin d'akinta, inda take cikin wani had'add'en doguwar riga navy blue, wanda yayi mata matukar kyau.
Musamman da ta yafa d'an siririn farin mayafi akanta.

Fitowan nata kuwa, yayi daidai da shigowar Rayyern cikin falon, karab kuwa ya sauk'e idanunsa akanta.

Duk da cewar ba akusa suke ba, amma hakan bai hanasa.
Ganin k'yallin da fuskarta keyi ba, still ga kuma bakinta, da yake fitar da shining na pink lipstick din da ta saka.

Janye idanunsa yayi daga kallonta, tare da k'arasowa cikin falon ya zauna.

Ita kuwa Jannart batare ma da ta lura dashi ba, kaitsaye kitchine ta wuce.

Koda taje ta samu sandwich d'in da take gasawa ya gasu.

Kashe oven din tayi, tare da d'aukan wani bowl, bayan ta saka poil paper aciki ne kuma, ta juye duka sandwich din.

D'aukan bowl d'in tayi ahannunta, tare da nufowa falon cikin takun ta na nutsuwa.

D'an tsayawa tayi ta d'auki tissue paper, kana ta k'arasa isowa cikin falon.

Da Murmushi Mamy ta kalleta, kana fuska asake tace.

"Jannart sarkin aiki, sannu duk kin cika mana gidan namu da k'amshin sandwich din naki."

Murmushi Jannart din tayi, tare kuma da matsowa ta ajiye bowl d'in sandwich din agaban Mamy.
Cikin kuma d'an yanayin alk'unya tace.

“Bismillah Mamy kici sandwich din.”

“Haba My Aunty Mamy kawai, tun d’azu fa muke zaman jiran sandwich din, da k’amshinsa ya cika ko ina dake cikin falon nan, Allah tun kafun ki kammala yawuna yake ta tsinkewa.”

Ramadan ya fad’a yana me matsowa, kusa da bowl din, tare da yagan tissue ya d’auko sandwich din guda d’aya.

Janart kuwa Murmushi tayi, tare da neman waje ta zauna akan sofa.

Ramadan kuwa Koda yakai sandwich din bakinsa idanu, ya lumshe, tare da jinjina kai, bakinsa cike da sandwich din wanda yaji rid’i yace.

“Gaskiya Aunty Jannart you’re the best, komai kin iya domin ban tab’a cin sandwich mai dadin wannan ba da  Allah waya koya miki girki haka?.”

Murmushi Jannart tayi tare da cewa.
“Malamai na nada yawa, Mom Aunty Dijat da kuma AYSHA ALIYU GARKUWA marubuciyar littafin GARKUWA dan na koyi abubuwa da yawa a ciki littafin sai kuma shirin Akoshi da rufi na tasharmu”.
Yana mai haɗiye na bakinsa yace.
“Kai Allah yayi musu al'barka ya jikansu suda iyayensu al'farma Annabi da al'ƙur'ani, ai mu sun mana gata Allah kawo Raihana ki koya mata komai”.
Dariya sosai Riyyam-nsra, Jannart, Mamy sukayi suna masu cewa Amin.

Riyyam nsra dake zaune ne ya taso cikin dariya da sauri, tare da cewa.

“Nima ai baza’ayi banda niba wanga santi.”

Ya kare maganan yana me daukan sandwich din yakai bakinsa.

Idanu ya lumshe tare da jinjina kansa, saboda yanda yaji dadin sandwich dinma harya zarce yanda Ramadan ke fadi.

Rayyern kuwa tab’e bakinsa yayi, tare da kawar da kansa gefe.

Riyyam-nsra kuwa sake gyara zama yayi, tare da ninke k’afafunsa, d’ago da kansa yayi ya kalli Mamy da kuma Rayyern, lokaci d’aya kuma sai yaji duk jikinsa yayi sanyi, wanda hakan yasa asanyaye yace.

“Mamy, Hamma Rayyern this week dinnan fa zan koma Ethiopia”.
Cikin abinda ba gaza one second ba duk suka katse dariyarsu tare da zuba mishi ido cikin

tsareshi da ido Rayyern yace.
“Meyasa? Yaushe ka tsara tafiyar?”.
Kanshi ya jingina jikin kujera cikin sanyi yace.
“Saboda Mammy ta matsa akan na dawo, tun last week take min maganan dawowa na to daga nan na fara shirin tafiyar, kuma nima nayi kewarsu sosai, sannan kuma na gama aikin da nazoyi ak’asar nan, yanzu babu wani abu daya ragemin sai komawa”.

Cike da tsananin mamaki Ramadan, ya d’ago da kansa ya kalli Riyyam-nsra din.

Murya araunace yace.

“Koma wa Ethiopia kuma Riyyam? sannan kuma this week why ka bari sai end of the month mana.”

Murmushi Riyyam-nsra din yayi, tare da kwantar da kanshi, cikin sanyi yace.

“Dole zan koma Hamma Ramadan ko shekarane ai zaizo dole in koma, saboda yanzu bani da wani reason na zaman k’asar nan, dama daliline ya kawoni.”

Idanu Rayyern dake zaune ya zubawa Riyyam din, Cikin yanayin nazarta yace.

“Wani aiki ne ya kawo ka, then wani reason?”

Murmushi mai kama dana waskewa Riyyam-nsra din yayi, kana cikin samun madafa yace.

“No Hamma Rayyern ba wani babban aiki bane fa, d’an k’aramin aiki ne kuma ma harna gamashi, dama kawai inada passion nazu wa Nigeria ne kan TIKTOK nema fa.”

Idanu Rayyern ya zuba masa batare daya sake cewa komai ba.

Mamy kuwa cikin dan yanayin damuwa tace.

“Haba Riyyam tafiya hakanan lokaci d’aya, ba zato ba tsammani ka bari mana kad’an k’ara kwanaki.”

Murmushi Riyyam din yayi, tare kuma dasa hannu ya shafa sumar kansa, cikin dan sakewa yace.

“Mamy Mammy ta matsa akan saina dawo, baya ga haka ma najima a k’asarnan almost 4to5 month fa.”

Shiru duk sukayi cike da jimamin tafiyar Riyyam din.

Musamman Ramadan da yakejin zaiyi kewar Riyyam din sosai, haka ma Jannart Domin ba kad'anba Riyyam-nsra din ke d'ebe mata kewa, domin akullum tana ganinsa kaman Abdull d'insu ne, baya ga haka kuma Riyyam din yana da shiga zuciya.

Rayyern kuwa mik'ewa yayi tsam ya nufi sama, saboda yagaji sosai a hospital baya ga haka, kuma yau dinma yaje company saidai ba new company dinsu yaje ba, yaje company dinsu wanda ake sarrafa auduga ne.

Koda ya haura saman kwanciyarsa yayi.

Acan falo kuwa basu yi wani hira sosai ba, duk suka watse kowa ya koma d'akinsa.

Almost 3days.
Kenan yau wanda acikin kwanaki ukun kuma, komai yana tafiya dai-dai musamman ab'angaren new Company, din da su Rayyern din suke son budewa.

Dan zuwa yanzu ankammala komai da komai, har an fara sarrafa kayan provision.

Kowanne store dake cikin company din kuwa, an cika sa da sarafeffen kayan provisions kala daban daban.
Komai na dafawa sun sarrafa shi.

Alhamdulillahi kuma ranar Friday aka tsaida amatsayin, ranar da za'a bud'e companyn.

Kasancewar kuma yau alhamis, shiyasa ake ta shirin bude companyn gobe, wannan yasa gaba d'aya Rayyern bai samu ya zauna ba.
Hasalima Koda ya fita bashi ya dawo gida ba, sai k'arfe 10 dai-dai.
Wannan yasa agajiye yayi bacci.

Washegari ranar jumma'a.

Kusan gaba d'ayansu Atare suka tafi masallacin jumma'a, bayan sun Idar da sallah ne kuma, Abba ke sake shaidawa Baba Maud'o cewar yaune, zasu bud'e sabon kamfanin nasu.

Sosai Baba Maud'o yayi farinciki, tare kuma da fatan Allah ya sanya al'khairi, ya kad'e duk wata fitina, ya kuma sanya musu riba mai albarka.

Da. "Ameen Ameen."
Abba ya amsa.

Bayan sun dawo daga masallacin ne kuma, suka soma shiri dan zuwa bud'e companyn.

Ganin yanda suke ta hada
hada ne kuma yasa, Jannart dake gefen Mamy matsowa kusa da Mamy cikin sigar rok'o tace.

“Ayyah Mamy dan Allah nima zanje in ba matsala.”

Murmushi Mamy tayi tare da juyowa ta kalleta cikin sakin fuska tace.

“To Jannart ai zaki iya zuwa, amma bari na tambayi Abbanku naji me zaice tunda kin san a tsare kike.”

Kai Jannart din ta jinjina, cike kuma dajin dadi ta cigaba, da juya pepper chicken din da takeyi tare da cewa.
“Toh Mamy a gaya mishi Allah yasa a barni”.
Amin
Mamy tace tana fita Kitchen din.
direct sashin Abba ta wuce, Koda taje ta sameshi yana shiryawa.

Zama tayi abakin gadonsa, cikin tausasa murya da kuma bashi girma amatsayinsa na Mijinta tace.

“Dama magana nazo muyi.”

Aje hular hannunsa yayi tare da cewa.
“Ina jinki”.
Cikin zuba mishi ido tace.
“Jannart ce ta sameni wai tanason zuwa bikin bud'e companyn, shine nace bari nazo naji ta bakin ka.”

Kai Abban ya dan jinjina cikin gamsuwa yace.

“To ai ba abundamuwa bane, zata iya binmu saimu tafi tare ko, kice mata ta shirya.”

Dan Murmushi Mamyn tayi, saidai kuma cikin jimami tace.

“Amma Alhaji kamanta cewar zamanta awajenmu sirrine.”

D'an Jim Abban yayi na wasu mintuna kana yace.

“Babu damuwa, zata iyayin shigar da babu wanda zai ganeta, misali ko irin shigar larabawa haka da suke rufe fuska, kinga Idan tayi haka babu wanda zai shaida ta ko!?.”

“Hakane To bari naje na sanar mata.”
Mamyn ta fad’a tana me mik’ewa tsaye.

A kitchen din ta samu Jannart, Cikin kulawa kuma tace mata taje ta shirya, saidai amma tayi shigar da bakowane zai ganeta ba.

Cikin jindadi Jannart din tace.
“To.”
Kasancewar ta kammala aikin da takeyi dinne kuma, yasa kaitsaye ta wuce d’akinta Dan shiryawa.

Acan b’angaren su Ramadan kuwa tsab suka shirya, cikin shigar manyan kaya, shida Riyyam-nsra kayansu iri d’aya Getzner ce orange color mai masifar maiƙo da kyau kalar kayan ya ƙara haska fatarsu saida sukayi wani yellow-yellow.

Bayan sun gama shiryawanne kuma duk suka fito falo.

Dai-dai lokacin kuma Rayyern ya fito daga cikin dakinsa, yayi kyau sosai cikin shigar suit din dake jikinsa Pink guava mai dan ɗigon maroon.
Wanirin sheƙi yakeyi suit din rigar cikin itama maroon hakama net din sa.
Kana ga takalmam toms maroon suma masu masifar kyau da sheki.
Ga kuma wani had’add’en  agogon daya saka.
Sosai yayi kyau masifar kyau sajen shin nan ya kwanta lib-lib sai sheƙi sukeyi yan siraran lips ɗinsa jajaye suma suna sheki,
Tattausan sumar kanshi tana kwance lib sai ƙamshi da sheƙi sukeyi.
Wayarsa ce riƙe a hannunsa.
Yana takowa da dan sassarfa,
cikar haiba da kuma kwarjininsa duk sun bayyana.
“Wow Masha  Hamma Rayyern kayi masifar kyau”.
Cewar Ramadan yayinda tuni Riyyam-nsra kuma yaketa daukansu hoto.

Haka suka rankayo zuwa falo, yana gaba Suna biye dashi abaya.

Koda suka sauk’o k’asa afalo suka samu Mamy.
Sai kuma Abba, Dr. Sulaiman, da kuma Usman P.A, duk sun shirya sauk’owan su Rayyern din kawai suke jira.

“Abba mutafi time yana kurewa.”
Rayyern din ya fad’a yana me duba agogon hannunsa.

Kai Abba Ya jinjina, tare da Kallon Mamy Cikin kulawa yace.

“Kira Jannart.”

“To” Mamyn tace, saidai batakai ga mikewa ba, Jannart din ta bud’e kofar falon ta ta fito.

Sanye take da doguwar riga maroon colour, Wacce aka k’awata jikinta da adon fararen duwatsu shuwariski.

Rigar irin abaya masu fad’innan ne, da tayiwa jikinta matukar kyau,  sai kuma babban mayafin da ta saka akanta, wanda kuma ta nad’ashi har akan fuskarta, kamar dai yanda larabawa keyi, hakan kuwa shiyasa idanunta kawai ake iya gani.

Bak’aramin kyau tayi ba, domin tafito ne a balarabiya sak, tayi kyau ainun.

Wanda har hakan yasa akaron farko, Rayyern ya kasa d’auke idanunsa daga kanta.
Duk da yaji bakincikin cewar da ita zasu tafi, amma ya yaba da shigar jikin nata ainun.

“Masha Allah Jannart kinyi kyau.”

Mamy ta fad’a cikin yabawa shigar dake jikin Jannart din, saboda shigane na musulunci, da kuma shigane daya boye asalin kamanninta.

Atare duk suka rankaya suka fita, zuwa compound din gidan, inda tsala tsalan motoci suke jiransu.

Wata black Range Rover Rayyern ya shiga, haka ma Abba da Baba Maud’o.

Su Ramadan da Riyyam-nsra kuwa motocinsu daban, Yayinda Mamy da Jannart ma suka shiga nasu motar.
Haka Usman P.A da Dr Sulaiman.
Convoy motocin nasu sukayi, ahaka har suka isa cikin babban kamfanin. Daya amsa sunansa kamfani.

Jama’a da kuma yan jaridune cike awajen, bayan su Rayyern din sun isone kuma, wajen ya dinke da sowa.

Haka dai suka karasa wajen zama na musamman suka zauna, sosai Jannart ta yaba da tsarin kamfanin. Domin tayi imani ko kamfanin Dadynta bai kai wannan ba.

Taro akayi mai tsabta bayan kowa yaci yasha ne kuma, aka bude companyn.

Yan Jarida kam sun samu abunda sukeso, musamman da suka ga yanda Rayyern yasa, wasu daga cikin ma’aikatan kamfanin, suka cika motoci da kayan provision, inda ya bada umarnin, akai kowacce mota ta abinci, gidan yari, da gidan Marayu, sauran motocin kuma yace rabawa gajiyayyu.

Ai kuwa hakan da yayi ya daki zuciyar mutane da yawa, hakan yasa yan jarida suka kara kaimi wajen shooting.

Alhamdulillah anyi taro lafiya, inda taron ya samu halartar manyan baki, yan kasuwa shareholders mata da maza suke ta zuwa, kowa yanaso ya zuba hannun jarinsa a kamfanin.
Bayan duk Jama'an dake wajen sun watse ne kuma, suka tattara duk suka koma gida.
Zuwa lokacin kuwa har dare ya soma yi, wannan yasa agajiye dukansu suka koma gida.

Washegari Saturday still a busy suka tashi, musamman Rayyern.

Yayinda Riyyam-nsra kuwa keta shirye shiryen, komawarsa Ethiopia.
Saboda ranan Monday Insha Allah zai tafi.

Acikin yan kwanakin kuma duk cikin hidima suke, saboda mutane daban daban da suke zuwa gidan su Rayyern din Taya murna yayinda shi kuwa Rayyern yanzu bai samun zuwa asibiti ma, a Company yake wuni kullum sabida yana son dai-dai ta komai ta yadda in ya tafi ta online zaci gaba da aiyukansa wasu kuwa ya mikasu ga MD.

Kasancewar yau Lahadi ne kuma yasa, Riyyam-nsra shiryawa yaje gidansu Naseer.

Hira sukayi sosai da Naseer din kafun daga bisani yayiwa, Umman Naseer din sallama, daga nan kuma gidan Malam Mai-nasara suka wuce.

Bayan sunyi masa sallama ne kuma, suka dawo nan gidan su Rayyern din.

Hira suka sha sosai, duk da cewar zuciyarsu babu dadi, saboda sunsan zasu yi kewar Riyyam din sosai.

Washegari Monday kuwa, k'arfe 8 dai-dai jirgin su Riyyam din zai tashi.

Duk yau din haka suka tashi babu dadi, saboda shakuwar dake tsakaninsu more Especially Ramadan da yayi zugum,
dan har wani ciwon kai yakeji, saboda tafiyar Riyyam-nsra din.

Haka ma Jannart.

K'arfe 7:50 am dai-dai kuwa Abba, Baba Maud'o, Rayyern da kuma Ramadan suka rakashi airport, cike da kewarsa, kyautttuka kuwa babu irin wanda basu bashi ba, domin Rayyern ma ba k'aramin kud'i yayiwa Riyyam-nsra din transfer ba.

Jannart kuwa har snacks tayi masa, tare da basa kyautan wani Apple Watch dinta mai kyau.

Sosai yayi musu godiya da irin karamcin da suka nuna masa, Koda yazo shiga jirgi,

Ruggume Ramadan yayi sai ga hawaye shar-shar a idanunsa
Cikin rawar murya yace.
“Hamma Ramadan azanzo aurenka”.
Cikin rawan murya Ramadan yace.
“Zanyi kewarka Riyyam-nsra inaji ba dadi tamkar zan rabu da rabin jikina nakeji”.
Da sauri Baba Mauɗo ya juya musu baya yana maijin wasu irin zafafan hawaye na tsastsafo mishi.
A hakan yaji Riyyam-nsra ya ruggumeshi ta baya kawai sai yaji hawayen sun silalo mishi.
“Allah sarki Baba Mauɗona zanyi kewarka”.
Ina ya kasa mgn domin in yayi mgn zasu gane yana kuka.
Cikin rauni Rayyern ya ɗan kamo hannunsa tare da cewa.
“Toh Riyyam-nsra mu zauna kawai mana”.
Da sauri ya sharce hawayen sa tare da juyawa gaban Abba ya ruggumeshi yana cewa.
“Mammay na nake son gani da kai mata sakonta amman in sha Allah nan kusa zan dawo”.
Daga nan ya juya ya nufi wurin shiga jirgin
Yana  zubda k’walla tare da daga musu hannu, aransa  yakejin zaiyi kewarsu sosai.
Saidai kuma yasani cewa.
Lallai watarana zai dawo, zai dawo ya zauna acikinsu, zama kuma na musamman bawai irin wanda sukayi ayanzun ba.

K’’arfe 8 dai-dai jirgin su Riyyam-nsra din ya d’aga, zuwa k’asar Ethiopia.

Haka su Rayyern din suka dawo gida, jikinsu  asanyaye.

Ramadan ne ya zauna akusa da Jannart, cikin sanyi yace.

“Wallahi duk gidannan babu dadi, Riyyam shi ke samu duk wani farinciki, gashi yanzu ya tafi, again kuma Hamma Rayyern ma nanda one week zai tafi, gaskiya nima tafiya zanyi.”

Cikin.sanyi Jannar tace.

“Gsky dole muji gidan ba daɗi,
To ba gani ba ga Mamy, ka daina fushi.”

Longoɓar da kai Ramadan din yayi, tare da mikewa tsaye, Cikin yanayin jin yuwa  yace.

“Muje ki bani abinci My Aunty.”

Mamy dake kallonsu ne tayi murmushi, cike da k’aunar y’ay’annata tace.

“To Ramadan kamanta da cewar, Rayyern da Jannart zai tafi? ai zama mu kad’ai kam ya kama mu.”

Jin abunda Mamyn ta fad'ane kuma, yasa Jannart saurin juyowa ta kalli Mamyn,  domin kwata kwata ita bata masan da zancen ba.

Ramadan kuwa fuska ya sake kwab'ewa Cikin yanayin damuwa yace.

"Gaskiya Mamy nima zan tafi London shak'atawa, ko ki gayawa Abba Dan Allah yaje, gidansu Rayhanna mana, atambayamin aure, gidan ya rame da yawa, please Mamy."

Ya k'are maganan yana me had'e hannayensa, alaman rok'o.

Murmushi Mamy tayi, kana cikin kulawa tace.

"To me kakeci na baka na zuba Ramadan, ai komai ya kusa, tunda har ankai kudin, nagani inaso, kuma iyayen Rayhannan sunce zasu tuntub'i Abbanku."

Idanu Ramadan din ya dan zazzaro cikin, mamaki hadi da tsananin jin dadi yace.

"Wow Mamy yaushe akayi haka bansani ba, Dan Allah su Abba sunje."

Murmushi Mamyn tayi tare da jinjina masa Kai tace.

"Eh su Abbanku sunje shekaran jiya, shine kuma yace kada na fad'a maka, da alama surprising dinka yakeson yi yanzuma subutar bakine."

"Masha Allah Alhamdulillah, thank you Mamayna, soon nima zanyi aure wow."

Ramadan din ya fadi haka cikin tsananin jin dadin daya rage masa kewar Riyyam-nsra.

Mamy da Jannart kuwa murmushi sukayi.

Haka dai suka d'an tab'a hira, kafun daga bisani suka watse.

Jannart kam gaba daya jin cewa da ita, za'a tafi Mascow yasa jikinta yin sanyi.

Wanda hakanne ma yasa ta d'aukar waya, ta kira Abba Kabir.

Bugu biyu kuwa ya d'auka bayan sun gaisa ne, kuma ta gyara zama kaman Abban yana gabanta tace.

"Abba kaji wai  dani zai tafi Mascow, d'azu Mamy take fad'a."

Daga can b'angaren Abba Kabir yayi murmushi, Cikin kuma jin dadi yace.
"Waye ɗin".

Cike da kunya tace.
“Shi Doctor din”.
Murmushi mai sauti Barrister Kabir yayi tare da cewa.
“Masha Allah Jannart, ai babu damuwa zaku iya zuwa, Allah Ubangiji ya tsare ya kuma kareku aduk inda kuke, yaushe ne zaku tafin?”

Fuskarta ta d’an shagwabe Cikin yanayin sanyi, tace.

“Abba basu fadamin ranar ba, amma nasan zasu fada ma Idan lokaci yayi.”

“To shikenan Jannart.”

Abba Kabir din ya fad’a, daga haka kuma hira kadan sukayi sannan sukayi sallama.

Washegari kuwa Abba da kasan ya kira Barrister Kabir ya sanar masa batun tafiyar.

Wanda kuma yau ya kama saura kwana biyu tafiyar tasu, sosai kuma suke ta shirye shirye tuni Rayyern ya tsara ayukan campany'nsa yadda ya dace.

Ana Gobe zasu tafi dinne kuma, Abba Kabir yazo sukayi sallama da Jannart din.

Washegari.

1:pm dai-dai jirginsu zai t
Yashi zuwa Mascow, hakan yasa tunda safe suka kammala shirinsu.

Cike da yakinin kewarsu, Mamy Abba da kuma Ramadan suka rakasu airport.

Karfe takwas jirginsu ya tashi zuwa, Abuja.

Bayan sun isa Abujan ne kuma, da kammanin awanni biyu jirginsu na zuwa Mascow ya d’aga zuwa sararin samaniya.

Ko acikin jirgin kuwa kujeransu na hade dana juna, tunda suka kama hanya kuwa, Jannart ta kwantar da kanta akan kujera tare da lumshe idonta dan bacci dake fuzgarta,
haka ma Rayyern shidinma lub yayi, Ahankali yake sauke ajiyar zuciya, tare kuma da ajiye idanunsa akan, yatsun hannunta wanda suke shinning.

Tafiya sukayi mai Nisan zango k’arfe.
8: 30 na daren garin, jirginsu ya sauk’e ababban airport din dake cikin garin na Mascow...!

*Albishirinku! Ma'aurata, GA GARKUWAR KU nan tafe muku da tsarabobi na musamman gareku ma'aurata daga cibiyar mgnin mata mai taken  GARKUWAR MA'AURATA*

NI DAI AYSHA ALIYU GARKUWA.
Ina matukar mamakin wani irin lokaci da ya riske mu mai wahalallan fassara. Kullum dai magana daya ce, akan ma'aurata, fada, rashin jituwa, mutuwar aure, akan kuskure kalilan, rashin kula, rashin yi wa juna uziri. Toh wai duk me ya janyo hakan? Na zurfafa a tsananin tunani hakan ya tilasta min bincike mai tarin yawa wanda ya kai ni ga gano inda matsalar take? Shin yar'uwa ke macece amma kin san wacece mace ku? Kin san me ake kira mace kuwa? Mace ita ce matar da take zama iyali a wajan namiji ta zame masa bango, sanyin idaniyarsa, ta zame masa gata da farin cikin rayuwarsa ta zame masa ruwa abar kore ƙishinsa ta zame masa mayafi mai karesa daga gigitar kadaice, ta kuma dorar da mijinta kan turbar gaskiya, ta kashe masa jiki da salonta ta rikita shi da baiwa da ni'imar da Allah ya bata idan har ta san hanyar mayar da kanta sabuwa dal awajanta, wato kullun takasance masa tamkar amarya har ya kasa tantance daren amarcinsu da sauran dararen rakun rayuwar su.

Wannan ita ce mace. Ina da wata saukakkar hanyar da zaki zama abar so da kulawa da soyayya a wajan mijinki ta hanya mafi sauki, 09097853276 hanyar ita ce ki gwada amfani da kayana na gyara ki gani, ina mai tabbatar miki da in sha Allahu sai kin dara da murna sai kuma kin gode min. Kayana kaya ne da aka yi shi da zallan itacanmu na gado marasa illa a cikin jikin dan adam musamman mace, kaya ne da suke taimakawa (sex hormones 😍) dinki.
Misali kina kallon India😘, hollywood, Asian film🥰 kina ganin yanda mazansu ke nunawa matansu tsananin soyayya kamar su ba su kyautar ransu!?
Saboda me hakan? Saboda suna sadaukar da lokacinsu wajan gyara jikinsu da kayan da ke tsattsafo da ni'ima cike da tsukewa, kayan nan kuma ana yinsu ne zallar magungunan gargajiya wanda ba su da illa domin haɗine na ingantattun itatuwa da yayansu.
Ina baiwar Allahn da miji ke daure mata fuska babu hirar arziki?
Zo ki ji yar'uwa zan baki gumbata da zallar gari wanda aka yi su da nagartattun itacen da ke da matukar amfani a jikin mace. Gubar ciko, gumbar tsalle dole, gubar da ba'a baiwa mai kishiya, garin maɗi, garin mallaka, tsumin goron tula, tsumin tsartai, tsumin maratsi, pala-pala butar sirri, kwanon k'asaitacciyar mace, furar mata madararta gareki Hajia takenta sha yanzu mgni yanzu, Ina mata masu fama da sanyi? Sanyin mara ki zo na hadaki da magani na na sanyi wanda yake wanke mara ya fitar da duk wata cuta da ke samun mazauni a wajan.
Ina da ciccibi mai kyau. Ina da hadin amare mai kyau wanda zai gyara yarinya ya kankaro mata kimarta akwai hadin mai jego wanda muke yinsa na asali inada kekkyawan Hadi maida tsohuwa yarinya.

Akwai daya bangaren wato *KAMSHI*
Kimarki gyaranki da kamshinki. Matan da suka gane suka san yanda za su kankaro da mutunci su ne masu amfani da kayan gyara da kuma sanyaya jikinsu da kamshi, ina da turaren wanka

da na bandaki na daki na jiki da na kaya dana tsuguno kamshin turarena na dabam ne mai sanyaya zuciyar wanda ya shaka ina da kayan kamshi na amarya da na maijego da na uwargida da dukkan macen da take kokarin mayar da kanta mai daraja a idon kowa ta zamo sarauni a idon mijinta, akwai shu'umar humra, sayan na gari maida kuɗi gida, banda karanta yayin gyara Hajia.

Zaku iya samun kayyakina a duk garin da kike, zakiyi min mgn ta whatsApp number na 09097853276 domin yin zaɓinki, ko karin bayani, zaki tura kuɗin ta account na 0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU in mun gama mgna zan sa miki kaya a mota yazo duk garin da kike, in baki shirya saya yanzuba Please kada mu wahal da juna ki bari sai kin shirya kafin kiyi min mgn.

🤝🥰😘 Daga taku AYSHA ALIYU GARKUWA
*(GARKUWAR MA'AURATA)*

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:45 - 🥰🥰: *Mascow International Airport.*

Ahankali Jannart ta bud'e Idanunta dake lumshe, tare da d'an muskutawa ta gyara zamanta, wanda kuma tayi hakanne saboda ganin, an bud'e k'ofar jirgin, har ma wasu daga cikin mutanen dake cikin  jirgin, sun fara fita.

Kasancewar a (VIP) very important people SECTION sukene shiyasa kuma ba suyi fitan farko ba.

Ahankali ta zare belt d'in dake d'aure agefen cikinta, tare kuma da mik'ewa tsaye, y'ar k'aramar hand bag d'inta ta d'auka, dai-dai lokacin kuma shima Rayyern d'in ya mik'e tsaye.

Hakan yasa ya zamana tana gaba shi yana biye da ita abaya.

Tafiya suke Cikin nutsuwa, wanda kuma hakanne ya bashi daman k'arewa shape din bayanta kallo, kasancewar doguwar rigan English wears ne ajikinta, mai d'an santsi da kuma sharara, bak'aramin kyau kuwa rigar tayi mata ba.

Ahankali ya janye idanunsa daga kallonta, tare da gyara zaman face mask din dake fuskarsa.

Dai-dai lokacin kuma suka kawo bakin, k'ofar fita daga cikin jirgin.

Ahankali Jannart ta sak'o jiki da kuma k'afarta ta dama waje.
Wani irin masifaffen sanyi ne taji ya shigeta, wanda har saida yasa ta manne hannayenta duka akan kirjinta, cikin kuma yanayin mamakin kyaun da garin ke dashi, ta soma jujjuya Idanunta

tako ta ina.

“Yah Allah.”
Ta fad’a adai-dai lokacin da ta sauk’e idanunta, akan tsarin burgewa da akayiwa, babban filin airport din, wanda ayanzun yake tamkar rana, saboda tsananin hasken wuta, daya cika ko’ina nawajen, domin matuk’ar ba sama ka kalla ba, ba zama ka tab’a cewa dare yayi ba.

Idanunta ta d’an lumshe Ahankali, tare da k’ara sanya hannayenta ta matse jikinta.

Acikin yanayin nata na hakane kuma, ta k’arasa sauk’owa daga Kan steps din.

Rayyern dake bayanta kuwa, idanunsa ya zuba mata, lokaci d’aya kuma ganin yanda take ta matse jikinta, yasa shi fahimtar cewa sanyi takeji.

Wanda azahirin gaskiya shi sanyin ma, dad’i yayi masa domin haka yakejin kowani kofar gashin jikinsa na bud’ewa.

Ahankali ya k’arasa sauk’owa daga kan steps din jirgin, dai-dai lokacin kuma sauran Doctors d’insa, way’anda already sun riga da sun sauk’o bisa jagorancin Dr Sulaiman, suka k’araso inda yake.

Hannayensa ya zuba acikin aljihun wandon jeans din dake jikinsa.

Tare da d’an soma takawa ahankali ya matsa, kusa da inda Jannart d’in ke tsaye.

“Muje.”
Ya fad’a cikin yin k’asa da murya, batare kuma da ya jirata ba ya soma tafiya.

Ganin hakanne kuma yasa ta rufa masa baya, kaitsaye suka nufi Cikin airport din, inda ananne zasu d’auki akwatunansu, suna gaba sauran Doctors din na biye dasu abaya.

Sudai mamaki da kuma tarin tambayoyi ne, kwance acikin zuciyarsu, saboda wannan ne karo na farko da suka ga, Ogan nasu da wata Mace agaba d’aya tsawon rayuwarsu, macen ma kuma da basusan wacece ba, kasancewar akwai face mask akan fuskarta, shiyasa har yanzu babu wanda yaga fuskarta, hasali kuma duk acikinsu basu da labarin auren Rayyern din sai Dr Sulaiman kadai ne ya sani, sun kuma san cewar kwata-kwata Dr Rayyern ba ma'abocin ta'ammali da mata bane, baya neman mata, to wacece ita awajensa?

Tambayar dake cin zuciyarsu kenan, wanda kuma basu da amsarta.

Ab’angaren Jannart kuwa sake matse jikinta takeyi sosai, domin duk yanda tayi tunanin sanyin garin ya wuce nan, wani irin masifaffen sanyi ne, dake ratsa cikin k’ashi da bargo, musamman ga ita da take da asma, gaba d’aya bata son sanyi, saboda had’ari ne ga rayuwarta.

Koda suka k’arasa cikin wajen kuwa, duk suna tsaye lambobin trolleys dinsu ke fitowa.

Saida kowa ya gama d’aukan nasa ne kuma, Rayyern din ya juyo ya kalli Jannart wanda Idanunta suka sanja launi, ga kuma wani irin sautin numfashi da yaji tana fitarwa.

Hannunsa ya mik’a Ahankali ya k’arbi trolley nata, juyowa yayi ya kalli d’aya daga cikin Doctors din.

“Sadiq kira mana taxi.”

“To.”
Sadiq din yace, kana cikin girmamawa ya fita zuwa babban compound din, Airport din.

Sud’inma kuma fita sukayi, dai-dai lokacin kuma Sadiq din ya nuna musu wasu taxi guda biyu. Wanda ya taro musu, kasancewar acikin airport dinma, masu taxi ne kaca-kaca.

K’arasawa jikin taxi din sukayi.
Rayyern ne ya bud’e k’ofar d’aya daga cikin taxi din ya shiga, Ganin hakane kuma yasa Jannart ma bud’ewa ta shiga da sauri, Dan acewarta ayanzu bata buk’atar wani jira har sai anbata izinin shiga,  saboda uban sanyin da takeji, tana k’ara wasu y’an mintuna awaje zai illatata.

Ganin su Rayyern din sun shiga cikin mota ne kuma, yasa sauran Doctors dinma duk suka shiga ragowar taxi din.

Kaitsaye hanyar wani  babban hotel din dake cikin garin suka nufa, bisa umarnin Rayyern.

Mik’awa kan titi da sukayi ne kuma yasa Jannart, kwantar da kanta ajikin kujerar motar, tare kuma da Ware dan siririn mayafin Kanta ta rufa ajikinta.

Atunaninta zama a cikin motar zai rage mata sanyi, saidai kuma taji sab’anin haka,  saboda acikin motar harda AC.

Idanunta ta d’an rumtse tare kuma da sake matse jikinta, cikin zuciyarta tace.

“Kai amma way’annan mutane akwai mayu, duk wannan uban sanyin bai ishesu ba, har sai sun had’a da AC.”

Rayyern dake zaune agefenta kuwa, gaba d’aya duk yana lura da yanayinta, saidai yi yayi kamar ma baisan cewa tana jin sanyin ba.

Tafiyar mintuna kad’an sukayi kuwa, sai gasu agaban wani had’add’en hotel mai tsananin kyau da tsari  *Brosko hotel Arbat Mascow.*

Idanu Jannart ta d’an zaro ta cikin glass din window’n motar, tare da Kallon dogon ginin beneyan hotel din, da bazata tab’a iya misalta kyawunsa ba.

“Kijira ni anan.”

Rayyern din ya fad’a adai-dai lokacin daya bud’e murfin motar ya fice.

Haka ma sauran Doctors din duk sun fito, kaitsaye cikin babban hotel din suka nufa, bayan Rayyern ya sallami sauran masu taxi din.

Kaitsaye cikin katafaren hotel
Din da kaitsaye za’a iya kiransa da Aljnnar duniya suka nufa.

Komai dake cikin hotel din mai kyau ne, kuma abun burgewa, duk da cewar dare ne amma kuma saboda yawan jama’ar dake ta zirga zirga awajen, da kuma wadataccen hasken da ke wajen, yasa wajen ya zamo tamkar rana.

Kaitsaye reception suka nufa, wanda kuma Rayyern dinne keyi musu jagora, kasancewar garin shi ba bak’onsa bane, sab’anin sauran Doctors din nasa, da babu wanda ya tab’a zuwa acikinsu.
Ayau kuma suka sake tabbatar da cewa, kyawun Mascow din ya wuce tunaninsu.

Koda suka k’arasa reception din Rayyern ne yayi musu duk wani abu daya dace, d’akuna 5 ya kama musu, kowannensu da d’akinsa, kud’i ya kashe sosai, domin duk wani abu daya san zasu buk’ata, saida ya umarta da a basu.

Bayan ya sallamesu ne kuma ya juyo, tare da nufo inda Taxi din nasu take.

Dai-dai lokacin kuwa Jannart take k’ara maida hankalinta, akan had’add’en ginin hotel din Brosko Arbat Mascow din, wanda aka k’awata ko ina d’insa da farin haske, ga kuma wasu irin followers wanda ita arayuwarta, bata tab’a ma ganin irinsu ba, domin furannine masu kyau da walwali.

Tsirarun mutanen dake wucewa akan titin ta kalla, kowannensu sanye yake da manya manyan kayan sanyi, daga sama kuwa dusan k’ank’ara ne ke d’an sauk’owa.

Duk da hakan kuwa mutanen wajen rayuwarsu suke normal, da dukkan alama sun saba da yanayin nasu.

Ahankali ya bud’e murfin motar ya shigo.

“Go.”

Ya fad’a yana me gyara zamansa akan kujeran, hakanne kuma yasa Jannart din d’ago Kanta ta kalleshi.

Karab kuwa suka had’a idanu dashi, janye Idanunta tayi daga kallonsa, tare da sunkuyar da kanta k’asa.

Shikuwa Rayyern y’atsun hannunta ya kalla, dai-dai lokacin kuwa driver’n taxi din yaja suka tafi.

Tafiya sosai sukayi  kafun suka iso gaban wani dan madaidacin gida, adai-dai wani babban k’ofa wanda gabansa ke cike da shuke shuken furanni mai taxi din ya tsaya.

Wanda hakanne kuma yasa Jannart d’ago kanta, Ahankali ta soma k’arewa wajen da ta gansu din kallo.

Wajene maitsananin kyaun gaske, wanda yake dauke da had’add’un gidajen, da kusan tsarinsu da yanayinsu ya kasance iri d’aya.

Bud’e murfin motar da taga Rayyern yayi ne kuma yasa ta fitowa itama.

Idanunta ta lumshe ahankali, saboda sanyin da taji ya sake shiga jikinta, saurin d’an takure jikinta waje d’aya tayi, saboda zama ta iya cewa, sanyin wajen ya banbanta dana wasu wajaje dake cikin garin, kasancewar arean kowani gida kewaye yake da wasu irin shuke shuke masu Bala’in kyau.

Rayyern kuwa sallaman mai taxi din yayi, bayan ya d’auki trolley d’insa ne kuma, kaitsaye ya nufi jikin wannan  gidan, da Jannart ta kasa d’auke idanunta akansa, domin hakanan take ganin ginin tamkar zane.

Ganin kuma Rayyern din na kokarin wucewa, ya barta ne yasa cikin sauri, ta d’auki nata jakar itama, tare da nufan inda taga yabi.

Ahankali take bin bayansa, Yayinda shi kuwa yake k’ara kutsa kansa cikin gidan.

Dai-dai sun iso tsakiyar gidanne kuma, idanunta suka sauk’a akan wani, makeken swimming pool, wanda aka k’awatasa da wani irin ruwa, gefe da gefensa kuwa wani wuta ne me fidda kala kalan haske, sosai swimming pool din yayi mata kyau.

Daga can gefen swimming pool din kuwa, wasu jajayen furannine masu kyaun gaske.

Itakam batasan  dame zata tsara had’uwa da kuma kyaun gidan ba.
Atakaice ma ganinta take acikin wata duniya sabuwa.

Isarsu jikin wata k’ofa ne kuma yasa, Rayyern d’an tsayawa, tare da d’aura Hannunsa na dama

akan k’ofar.

Wasu na’urori dake jikin k’ofar ne suka d’auki hoton y’an yatsun hannunsa,  bayan da kamar second 5 kuwa sai ga k’ofar glass din ta kawo haske.
“Wellcome back Dr. Rayyern Bashir Muhammad Mai-nasara.”

Wata y’ar siririyar murya ta fad’a, Wacce  ta fito daga cikin d’an wani na’ura mai kaman camera dake jikin k’ofar.

Na’urar na gama fad’in haka kuwa, lokaci d’aya k’ofar ta bud’e.

Idanu Jannart dake tsaye abayansa, ta d’an zazzaro saboda itakam bata tab’a ganin, security door irin haka ba.

Rayyern kuwa tura kansa ciki yayi, batare kuma da ya juyo ya cewa, Jannart din k’ala ba..

Jannart dake tsaye kuwa Ganin kofar na kokarin rufewa ne, yasa ta jan trolleynta cikin sauri ta shige.

Ahankali ta jefa k’afarta na dama akan wani masifaffen carpet me shegen laushi.

Da sauri ta kalli k’asanta, saboda yanda taji k’afafunta na kokarin nutsewa acikin carpet din.

Ajiyar zuciya ta sauk’e tare kuma da d’agowa, ta sauk’e idanunta, acikin babban falon da ta samu kanta.

Falone daya amsa sunansa falo, haka kuma falo ne da aka zubawa dukiya mai tarin yawa acikinsa.

For the first time da ta somayin k’auyanci arayuwarta, domin zata iya cewa bata tab’a Ganin falo mai kyaun wannan ba.

Komai dake cikin falon na yellow and milk colour ne, more especially cushions din falon, way’anda suke da matuk’ar kyau.
Kasancewar kuma ginin falon nada tsawo ne, yasa aka k’awata jikinsa da wallpaper, brown, milk and golding colour, sai kuma wasu had’add’un cottons masu masifar kyau, kasancewar cottons din farare, shiyasa aka d’an tsara baki bakinsu da brown style.

Atsakiyar falon kuwa, wani d’an madaidaicin carpet ne brown and milk colour, sai kuma brown table da aka d’aura akansa.

Daga can sama kuwa wani abune mai kaman glass babba, wanda ya d’an sako kansa cikin tsakiyar falon.

Sai kuma babban tv plasma dake aje akan wani glass mai kyaun gaske.

Daga can gefe kuwa wani d'an abune mai sheki wanda aka killacesa acikin rose,  sai kuma na'urar sanyaya d'aki, da kuma wanda yake saka d'aki d'umi.

Daga can gefe kuwa two bedrooms ne, sai kuma kitchine and dining table.

Jannart dake tsaye kuwa Idanunta ta zubawa cikin falon bata ko k'yaftawa, Yayinda acikin ranta take mamakin irin tarin dukiyan, da aka kashe wajen k'awata falon.

Rayyern kuwa kaitsaye d'aya daga cikin bedrooms din ya nufa.

Ganin hakanne kuma yasa Jannart, ajiye trolleyn ta cikin d'an yanayin matse jikinta, ta zauna akan d'aya daga cikin kujerun falon, tayi hakanne kuma saboda batasan inane zata sauk'a amatsayin masauki ba.

Shiko Rayyern koda ya shiga kayan dake jikinsa ya rage, cikin gajiyawa kuma kaitsaye ya nufi wani waje, wanda nake da yakinin cewa toilet ne, duk da kuwa yanda aka k'awata wajen da gilasai kala-kala.

Ahankali ya murd'a kofar ya shiga, kamar yanda nayi hasashen kuwa hakanne ya kasance, domin nanne toilet din dake cikin d'akin, saidai kuma ganin yanda aka k'awata toilet din, yasa ni tafiya duniyar mamaki, saboda yanda akayi wajen tamkar wajen shak'atawa.
Tabbas wajen ya had'u sosai, ga wanda bai tab'a zuwa ba kuwa dole ne yayi kauyanci.

Anutse ya sakarwa kansa shower, bayan yayi wankanne kuma ya d'aura da alwala, domin zuwa yanzu kusan k'arfe shabiyun dare ake nema, anan wajen nasu.

Ahankali ya bud'e murfin bathroom din ya fito, rike da towel ahannunsa yana me tsare ruwan jikinsa.

Bayan ya kammala goge duk jikin nasa ne kuma, ya k'arasa tare da bud'e trolleynsa, lotion mai dadin k'amshi ya ciro, tare da shafawa ajikinsa.
Bayan ya gama shafa mai dinne kuma, ya saka wani riga da wandon payjamas ajikinsa,  mik'a ya d'anyi kana Ahankali ya k'arasa, gaban fridge ya d'auki goran ruwa yasha.

Saida yaji ya koshi da ruwan kafun ya rage hasken wutan dake cikin dakin.

Kaitsaye kan had'add'en gadon dake cikin dakin ya nufa.
Da addu'a abakinsa ya kwanta, tare kuma da lumshe idanunsa, saboda wani irin gajiya da yakeji, Sam kwata kwata shiya ma manta da wata Jannart.

Acan falon kuwa Jannart ne ta sake matse jikinta waje d’aya, akaro na barkatai kuma kenan yanzun, da ta d’aga Idanunta ta kalli agogon dake kafe ajikin bango.

Idanunta ne suka d’anyi narai narai, saboda wani irin fitinannen sanyin dake ratsa ta takota Ina, har wani huci numfashinta ke fitarwa,  duk da cewar ta duk’unk’une jikinta waje d’aya, amma hakan baisa ta daina jin sanyin ba.

Ganin Idan ta tsaya ahakan zata cutune yasa ta bud’e Jakanta, wani babban abayanta mai kauri ta zaro, tare da zurawa ajikinta, sake komawa saman kujeran tayi ta mak’ale.

Idanunta ta d’an lumshe Ahankali, saboda Jin sanyin ya d’an ragu mata.
Akan trow pillows din dake manne ajikin cushion din ta d’aura kanta.

Ahankali ta soma sauk’e Ajiyar zuciya, tare da had’e Idanunta ta lumshe.

Duk da cewar tana jin gajiya sosai ajikinta, tana kuma buk’atar son tayi wanka da ruwan dumi, amma babu yanda zatayi.

Sam batasan haka sanyin Mascow’n yake ba, domin taso ace wani yanki na daban dake, cikin Russia din suka zo, bawai  Mascow nan ba.

Da wannan tunanin azuciyarta bacci ya d’auketa.
Still kuma ko acikin baccin nata batayi sake, abun rufawar nata ya fad’i ba.

Rayyern dake kwance akan lallausan gadonsa kuwa, sake gyara kwanciyarsa yayi, tare da lullub’e jikinsa da tattausan bargo.
Idanunsa ya d’an lumshe tare da sauke nunfashi cike da nutsuwa, kwata Kwata zuciyarsa ta kasa tuna masa Jannart daya bari a falo, yana nan ahaka har bacci ya d’aukesa.

5:00 am
Dai-dai alarm din dake gefen gadon nasa, ya soma fitar da sautin kara.

Wanda hakan yasa ahankali ya bud’e idanunsa tare dayin mik’a, sunan Allah ya fara ambata, kafun daga bisani ya tashi ya zauna.

Agogo ya kalla, tare da zuro
k’afafunsa k’asa.

Cikin d’an yanayin dake nuna har yanzu yana tare da, gajiya ya d’an lumshe idanunsa, acikin zuciyarsa kuwa tunanin yanda zai fara zuwa masallaci yake.

Saboda yasan tsakaninsu da masallacin akwai nisa, domin ko amota zaije saiyayi 15mn zai isa, Idan da k'afane kuma mutum sai ya share 30mn ma bai isa ba.

D'an ya mutse fuskarsa yayi, saboda gajiyan da yakeji ajikinsa.

Anutse ya tashi daga kan gadon, direct toilet ya nufa, da ruwan d'umi yayi wanka had'e da d'auro alwala, bayan ya fito Daga toilet dinne kuma, ya sanja kayansa  zuwa riga da wandon SP,  lallausan darduma ya shumfud'a tare da tada sallah.

Adai-dai lokacin ta soma bud'e Idanunta Ahankali, harta gama waresu.

D'an yunkurawa tayi ta tashi, ahankali ta mik'a hannu ta d'auki wayarta dake gefe,  Ganin lokacin sallan asuba yayi ne kuma yasa ta, tashi ta zauna.

Ahankali ta soma k'arewa falon kallo, saidai kuma sam bata ga alaman akwai toilet acikin falon ba, gashi duk jikinta wani iri yakeyi mata, ga masifaffen sanyin dake busawa gashi kuma dole zatayi wonkan taci gaba da salla domin tasan zuwa yanzu ta samu tsarki zataci gaba da ibadunta daga sallan asuban.

Ahankali ta ajiye k'afafunta ak'asa tare da mik'ewa tsaye, kallonsa ta mayar ga kofofin d'akuna guda biyun dake cikin falon.

Idanunta ta d'an tsayar akan k'ofar da taga Rayyern din ya shiga jiya.

Ahankali ta sake gyara zaman babban abayan dake jikinta, Cikin yanayin takunta mai d'auke da nutsuwa ta soma takawa, kaitsaye ta nufi d'ayar k'ofar dake hannun hagu.

Koda ta k'arasa bakin k'ofar ahankali, ta d'aura hannunta akan handle din k'ofar, tare da d'an murd'awa, cikin sa'a kuwa taji k'ofar ta bud'e.

Ajiyar zuciya mai k'arfi ta sauk'e, tare da d'an tura kanta cikin d'akin.

Extra room ne mai kyau, wanda gaba d'aya aka malale k'asansa da wani lallausan carpet, Daga can gefe guda kuwa gado ne d'an madaidaici, sai kuma wani long mirror dake can gefe da gadon.
Bayan bedside carbinet kuwa, babu komai acikin d'akin.

Ajiyar zuciya ta kuma sauk'ewa, Ganin kuma akwai na urar dumama daki acikin dakinne, yasa ta juyawa ta koma falo, akwatinta ta d'auko tare da dawowa cikin d'akin.

Bayan ta ajiye akwatin nata ne kuma, tanu fi wani k'ofa dake cikin d'akin hannunta riƙe da miskil dahar ta nufi kofar, wanda take da yakinin cewa toilet ne.

Kamar yanda tayi zato kuwa hakanne, toilet ne me kyau sannan kuma akwai komai na amfani aciki.

Ganin da tayi kuma akwai shower mai bada ruwan dumi ne, yasa ta kwab'e kayan jikinta, Anutse ta sakarwa kanta ruwan d'umin bayan ta tabbatar da tsarkinta.

Wani irin dadi da nutsuwa taji alokacin da ruwan ya sauk'a akan fatar jikinta.
Sosai sanyin da takeji din ya ragu, bayan tayi wankan ne kuma tayi amfani da turaren miskin kamar yadda ta saba kana ta had'a da alwala.

Wani babban bathrobe ta saka, tare da bud'e kofar bathroom din ta fito.

Cikin d'an hanzari gudun kada sanyi ya dake shiga jikinta, ta jawo akwatinta tare da bud'ewa, ta zaro wata had'add'iyar riga mai kaman na sanyi, duk da kasancewar rigar english wears ce amma tana da kauri sosai, saidai bata da yawan tsawo domin da kad'an ta wuce mata guiwa, domin rigane irin fashion dinnan.

Koda tasaka rigar cas tayi mata, musamman da rigar ta kasance irin mai kwala dinnan ne.
Tubke dogon gashinta tayi, tare kuma da d'aukan safa mai kauri da tsawo ta sanya ak'afafunta.

D'aya daga cikin sallayun da tazo dashi ta shumfud'a, tare da zura wani dogon hijabin daya rufe mata duk jikinta, bayan ta kunna na'urar dake d'uma d'aki ne kuma, ta koma kan sallaya tare datada sallah.

Bayan ta idar da sallan tayi azkhar ne kuma ta koma ta kwanta akan lallausan gadon, tare da jan blanket ta rufe jikinta.
Wani irin ajiyar zuciya mai karfi ta sauk'e, badon komai ba kuwa, saidan nutsuwar da taji ta samu.

Acan b'angaren Rayyern kuwa Koda ya idar da sallah, karatun Alqur'ani yayi, bayan ya idar da karatunne kuma ya soma shirya kansa.

Saboda zuwa lokacin har k'arfe 7 tayi, hasken sararin samaniya ya bayyana ko ina.

Tsab ya shirya cikin wani had'add'en suit da yayi matuk'ar amsar jikinsa, takalmin Gucci da kuma Gucci parfume ya fesa ajikinsa.
Sosai yayi kyau yau din, Yayinda suit din ta k'ara fito dashi, amatsayin babban likita, yayi kyau ainun, briefcase da kuma wayoyinsa ya dauka.

Ahankali ya murd'a handle din kofar d'akin ya fito, yana me gyara agogon dake daure atsintsiyar hannunsa.

Wayarsa dake rik'e ahannunsa ne ta soma k'ara, alaman shigowar kira, picking call din yayi tare

da kara wayar akan kunnensa, batare kuma da ya gama sauraran, abunda ake fad'a masa acikin wayan ba, cikin d'an yanayin gaggawa yace.

"I'm on my way."

Yana gama fadin hakan ya zare, wayar daga kan kunnensa,  cikin sauri kuma ya fice daga cikin falon.

Kaitsaye babban titin dake k'ofar gidan ya nufa, tsayawa yayi abakin titin tare da d'an soma lallatsa wayarsa, da alama sak'o yake turawa.

Bayan ya gama tura sak'onne kuma, ya maida wayar tasa cikin aljihun sa.

Almost 10mn kacal wata had'add'iyar mota ta k'araso inda yake, parking motar akayi, cikin sauri kuma baturen dake cikin motar ya fito, aladabce ya mik'awa Rayyern din key din motar.

Cikin muryar turanci baturen yace.

"We'll come back Sir."

"Thank you Jonas."

Rayyern din ya fad'a atak'aice tare kuma da bud'e murfin motar ya shiga,  wanda da dukkan alama dama,  yana da motar Wacce Idan yazo k'asar yake amfani da ita, kasancewar ak'asar yayi karatun Degree d'insa na biyu, wannan dalilin yasa yake zaune a gidan da yake mmkin yadda akayi Abbansu  ya mallakeshi anan k'asar ta Russia.

Jonas  shine Wanda yake kula da komai na gidan dama duk wani abu nasu, duk da ya manyata.
Koda zuwa ya kamashi, shi yake gayawa ya gyara musu komai.
Jonas din ne ya  rufe masa murfin motar, shi kuwa Rayyern cikin k'warewa yaja  motar yayi gaba.

Ganin Dr. Rayyern din ya tafi ne kuma yasa, Jonas tare taxi ya koma inda ya fito.

Rayyern kuwa kaitsaye babban hospital din, dake cikin garin Mascow ya nufa, kasancewar tuntuni ya bawa sauran Doctors din, umarni akan su had'u acan hospital din, so already ma sunje shi kawai suke jira.

A hankali ya kusa hancin motarsa cikin farfajiyar.
*HSCT centre Mascow*
Cikin parking  space na hospital din yayi parking, Cikin nutsuwa ya fito, tare da nufan cikin

hospital din da tafiyarsa ta k’asaita...!

By

*GARKUWAR FULANI*

22/12/2021, 19:47 - 🥰🥰: Yana isa farfajiyar asibitin su Dr. Sulaiman dake jiransa, suka k’araso garesa da sauri, hannu ya basu suka gaisa, bisa jagorancinsa kuma kaitsaye suka wuce, wani babban sashi na musamman dake Cikin hospital din.

HSCT centre Hospital ne me kyaun gaske wanda aka yi masa tsari mai kyau, komai dake cikinsa na musamman ne sabida shine babban asibitin horaswa da sukeji dashi a kasar.

Basu k’ara jaddada kyawun asibitin ba kuwa, saida suka shigo babban dakin ganawan manyan likitoti, wanda aka yi masa tsari na daban kuma na musamman.

D’akin taron da komansa ya kasance na glass, cike yake da manyan likitoti way’anda suka zo daga k’asashe sassan daban daban na duniya, kowanne likita kuwa ya amsa sunansa likita, wanda kuma sunzo ne dan k’arawa junansu sani.

Koda suka shiga cikin d’akin taron amutumce suka gaisa da junansu, anutse kuma kowanne ya zauna akan kujerar dake lik’e da sunansa.

Cikin girmama junansu, batare da wani babban cin k’asa ko addini ba suka soma gudanar da abunda ya kawosu.

Sosai suka b’ata lokaci wajen meeting, wanda ya d’aukesu sama da 6hours, domin tun 8:00 am suka shiga, basu fito ba kuma sai 2:00 pm dai-dai.

Nan ma bawai sun kammala bane, breaktime ne suka samu, wanda kuma hakanne ya baya musulman cikinsu daman yin sallah’n azahar.

Bayan sunyi sallan azahar dinne kuma, suka wuce wani cafe dake cikin hospital din, abinci mai kyau akayi saving nasu.
Saidai shi Rayyern bai wani ci sosai ba, duk da cewar baiyi breakfast ba yau din, amma hakan baisa yaci abincin sosai ba.

Bayan sun kammala cin abincinne kuma, suka sake komawa meeting din.

Basu suka fito ba sai sallan la'asar.
Koda sukayi salla kuwa, sashin da sabbin na'urorin aikin su suka nufa nan akai ta gwada musu ko wanne da kuma aikinsa
Basu fito ba har sai 5:30 pm, gaba d'ayansu agajiye suke, duk da cewar dukansu sun samu k'arin haske akan abubuwa da yawa, amma gaba d'aya sun jigata, saboda zaman waje daya babu dadi.

Fitowarsu din kenan kuma, Rayyern ya kalli su Dr. Sulaiman way'anda duk gajiya ya bayyana atattare dasu.

“I hope all yours. understanding the meeting?”

Yayi maganan yana me gyara zaman suit din dake jikinsa da rike jakar laptop nashi wanda shiyasa baya son Usman P.A yayi nesa dashi.

“Yeah we understanding.”

Gaba d'aya suka had'a baki wajen amsa masa.

Kai ya jinjina cike da gamsuwa, dai-dai lokacin kuma taxi din da suka tara suka k'araso.

Rayyern kuwa juyawa yayi ya nufi motarsa, shi kansa agajiye yake ga kuma wani irin kasala dake saukar masa.

Kusan Atare suka fita daga harabar asibitin, shida su Dr. Sulaiman way'anda suka shiga cikin taxi.

Suna hawa titi kuwa suka raba hanya, inda su masaukinsu Brosko hotel Arbat I, direct hotel dinsu suka nufa, shikuwa Rayyern hanyar gidansa ya nufa.

Cikin nutsuwa yake driving dinnasa, Dai-dai yazo wajen HALAL Sapiens RESTAURANT ne kuma ya tsaida motar, tare da fitowa ya nufi ciki.

Takeaway na african dishes yayi, sai kuma na salad and Chinese dishes.
Yayi hakanne kuma saboda sometimes yafiso yana mixing food.

Gaba d'aya acikin tsarinsa ma babu Jannart, domin kuwa kwata-kwata ma ya manta da cewar yazo da MACE.

Bayan ya karb'i takeaway dinnasa ne kuma, kaitsaye ya koma mota tare da nufar gidan nasa.

Koda ya iso gidan acikin compound yayi parking motar,  Ahankali yake tafiya yana me zare suit

din dake jikinsa.

Hannunsa ya d'aura ajikin kofar, tana bud'ewa ya tura kansa ciki.

Ahankali ya sauk'e Ajiyar zuciya, tare kuma da ajiye ledan Halal Restaurant din dake hannunsa akan kujera.

Direct bedroom d'insa ya wuce, yana shiga kuwa ya rage kayan dake jikinsa, tare da wuce bedroom in 20mn yayi wanka.

Bayan ya fito ne kuma ya shirya kansa, cikin wasu Sabin kaya.
Wayarsa ya d'auka kana ya kuma dawowa cikin falon.

Zama yayi akan sofa tare da tank'washe k'afafunsa, Ahankali ya bud'e ledar Halal restaurant din.

Chinese dishes din ya soma ci, Yayinda ya maida hankalinsa gaba d'aya kan laptop din dake gabansa.

Daga can cikin left side bedroom din kuwa, Jannart ce kwance tayi lub akan gado.

Wanda zuwa yanzu kuma tayi matuk'ar jigata, saboda wani irin yunwa dake damunta, kasancewar rabonta da abinci tun jiya da safe, Domin ko acikin jirgi wani dan cake kawai taci.

Tun tashinta yau din kuwa babu abunda takeci sai ruwa.
Wanda zuwa yanzu har ruwan ya soma murd'arta.
Ga kuma wani shegen sanyi dake damunta.

Hannu tasa ahakali ta dafe Kanta dake d'anyi mata ciwo, her know tasan babu kowa acikin gidan, kasancewar d'azu ta fito, ta kuma gama dube dubenta amma sam bataga alaman bayan ita akwai wani rai agidan ba,  har kitchine din dake cikin falon ta shiga wai ko, zata samu abunda zataci amma babu komai.
Hakan kuwa shi yasa koda tayi sallan la'asar ta dawo daki ta kwanta.

Duk yanda taso bacci ya dauketa kuwa abun ya kasa, saboda yunwa ya hanata sukuni.

Shikuwa Rayyern baiwani ci abincin sosai ba, ya mik'e tsaye, saboda yaga lokacin sallan magriba tayi.
Direct dakinsa ya koma ya d'auro alwala.

Koda ya fito car key d'insa ya dauka, tare kuma da ficewa daga Cikin gidan gaba d'aya.

Kasancewar yana dan gudu ne kuma yasa, tafiyar 13mn ne ya kaisa babban masallacin.

Yana zuwa kuwa ko mintuna 3 baiyi ba aka shiga sallan magriba.
Bayan sun idar ma haka ya zauna acikin masallacin, har saida akayi sallan Isha.

Acan gidan kuwa Jannart adaddafe tayi sallan Isha, saboda yunwan da take cinta aciki, bayan ta idar da sallan ne kuma ta sake dawowa falon.

Aikuwa cikin sa'a ta samu sauran abincin da yaci ya rage, zama tayi awajen cikin yunwa, batare kuma da tunanin komai ba ta jawo takeaway d'aya ta soma ci,  sosai taci abincin har saida taji cikinta ya kama, kana ta bi da ruwa.

Tana gama cin abincin kuwa lokaci d'aya, taji wani irin kasala ya sauk'ar mata azabebben sanyin da takeji ya ɗan ragu kaɗan.

Ahankali ta mik'e tsaye tare da wucewa d'akinta, tana shiga kuwa ta fad'a kan gado, tare da jawo blanket ta rufawa jikinta, lokaci daya kuma taji wani irin bacci na fusgarta.

Shikuwa Rayyern bayan an idar da Sallan isha'n, kaitsaye hanyan gida ya nufo.

A hankali yayi paking kana ya fito tare da rufe motar, cikin yanayin gajiya, Bacci da kasala ya nufi cikin gidan,
hannunsa ya ɗaura tsakiyar kofar lokacin ɗaya ta buɗe, cikin lumshe ido ya kutsa kansa cikin falon.
Yana taku cikin alamun bacci, gaban santer table ɗin ya nufa dan ɗaukar System ɗin sa daya bari a wurin.

Da sauri ya ɗan zubawa ledodin kan table ɗin idanu,
"Yah salam".
Ya faɗi tare dasa hannunsa ya dafe kansa.
Allah ya sani shi ya ma mance da ita gaba ɗaya sai yanzu da yaga ledodin da ya bari an sauya musu tsarin zama ta fado mishi a rai, a fili yace.
"Astagfirrullah ba ga irinta nanba na gayawa Abba yaki fahimtata, ni yaushema na kula da kainama bare wata da aka lika min gashi nan wlh na mance da ita".
Ya ƙarashe mgnar yana  k'arasa isowa gaban table din.

Yana isa kuwa idanunsa suka sauk'a akan ledan abincin daya bari, ga kuma wani takeaway dake gefe wanda aka bud'e.
Da dukkan alama kuma yasan itace taci abincin.

Kansa ya d'an girgiza tare da lumshe idanunsa, cikin d'an yanayin gajiya yace.

"Sune suka ja miki Allah ya gani ba laifina bane, na fad'awa Abba cewar ni bazan iya kula da wata mace ba, amma yasaka dole saida nazo da ita, zata takurani nasani, then ba Lallai na iya

kulawa da cinta ba, cause nima ban kula da nawa cin ba."
Ya ƙare mgnar yana mai
D'aga kafad'unsa yayi tare kuma da bud'e hannayensa alaman ko oho, bai sake bi takan takeaway dinba kuma ya wuce zuwa bedroom d'insa.

Yana shiga ya kwanta tare da buɗe laptop d'insa yana dan latsawa, ahaka har bacci ya d'aukesa.

Yayinda ab'angaren Jannart kuwa tuntuni ma, ita baccin ya d'auketa.

Washegari.

The same 7:00 am dai-dai ya gama shirya kansa, still cikin wasu tsadaddun suit, saidai colourn ya banbanta dana jiya, Domin yau din ash colour suit ya saka, sai kuma wani babban jacket mai kyau daya d'aura akai, musamman Dan tarewa kansa, masifaffen sanyin da akeyi.

Fitowa falon yayi cikin shirinsa na office tsab,  zama yayi akan d'aya daga cikin kujerun falon, tare da zaro wayarsa yayi musu ordern abinci.

Laptop d'insa ya bud'e tare da d'an soma tattab'awa, yana nan azaunen kuwa yajiyo k'aran intercom, da'alama kuma order'n abincin da yayi dinne ya iso.

Ahankali ya mike tsaye tare da k'arasawa ya bud'e kofar, kaman yanda yayi hasa she din kuwa hakanne, domin abincin ne aka kawo, karb'a yayi kasancewar kuma free delivery ne, shiyasa shi juyawa ya koma ciki.

Zama yayi tare da bud'e takeaways din, way'anda yaga zai iya ci ya d'an tsakala, batare kuma da yaci sosai ba ya tashi, ya wuce zuwa HSCT centre hospital domin yasan yauma 8:00 am dai-dai zasu shiga meeting.

Fitannasa da kamar 17mn Jannart ta bud'e kofar dakin ta fito,  sanye take cikin wani riga da wandon jeans, da sukayi matukar kama jikinta, kasancewar kayan masu kauri kuma shiyasa, basu wani bayyana surar jikinta sosai ba, uwa uba kuma kaurin nasu ya rage mata kaso 30 acikin d'ari na sanyin da takeji.

Ahankali ta k'araso cikin falon, sauk'e idanunta akan abincin da tayi ne kuma yasa ta sauk'e Ajiyar zuciya, domin kafun yanzu harta fara tunanin wuni da yunwa.

Zama tayi acikin falon tare da kunna TV plasma, Anutse kuma cikin kwanciyar hankali ta soma cin abincin.

Bayan ta kammala ne kuma ta kimtsa falon, tare da dawowa ta kwanta akan wata cushion, din da musamman akayi ta dan shak'atawa.

Acan b’angaren Rayyern kuwa yauma taron nasu ya dau zafi sosai, Dan yau din  kamar karantar dasu akeyi, akan sikila ta yanda za’a magance ta, da kuma yanda za’a iya sanjawa mai d’auke da cutar jini.

Sosai kuma duk Doctors din suke enjoying abunda ake koyar dasu.

*Nigeria*

Mamy ce zaune acikin falon tayi shiru,  saboda duk haka takejin gidan nasu babu dad’i,  domin hatta Ramadan yanzu ba zama yakeyi ba, gaba daya hankalinsa, ya maidashi akan hospital dinsu, Idan ya fita baya dawowa saida yamma.

Abba da shigowarsa kenan, ganin yanda matar tasa ke cikin damuwa ne yasa shi cewa.

“Ruk’ayya.”

Ya k’ira sunanta atausashe.

Hakan kuwa shiya saka ta juyo ta fuskancesa.

“Tunanin me kikeyi haka?”
Abban ya tambaya yana me k’arasowa cikin falon.

Mamyn kuwa Ajiyar zuciya ta sauk’e, cikin dan yanayin sanyin dake dauke da kewa tace.

“Kewar su Rayyern da Jannart nake, gaba d’aya kwana biyun nan gidan duk babu dadi, ga Ramadan ba zama yake ba,  dama ace Riyyam  bai koma ba, to danasan abun da sauk’i, gaskiya nima yanzu kam na matsu ayi batun auren Ramadan, akawo mana Wacce zata na d’an d’ebe mana kewa.”

Mamyn ta k’are maganan cikin dan damuwa.

Abba kuwa murmushi yayi tare da zama akusa da ita, Cikin kulawa kuma yace.

“To in bandake da abunki Ruk’ayya gaki ga mijinki kuma wani kewa ne ya rage miki?”

Murmushi itama Mamyn tayi, kana cikin dan sakin fuska tace.

“Hakane amma nima ai inason kusanci da y’ay’ana matsayin  kewar miji da ban ta yarama da ban ina son yarana.”
Ta ida mgnar hawaye na silalo mata da alamun akwai wani babban abin data tuna wanda ke

damun rayuwarta.

Kai Abban ya jinjina tare da gyara zamansa cikin tausasawa yace.

“Badamuwa maganar auren Ramadan, yanzu muna jiran cewa daga wajen iyayen yarinyar ne,
Insha Allah za’ayi bikinsu nan bada jimawa ba,
Sannan yara kuma keda Allah ya bawa Rayyern, Ramadan, ai saikice Alhamdulillah.”
Uhummm taja wani dogon numfashi tare da zuba mishi ido alamun tuni.
Shi kuwa Abba kai ya jinjina mata, tare kauda zancen da cewa.
“Amma niko tunda yaronnan Riyyam-nsra ya tafi kunyi magana dashi kuwa?.”

Murmushin Jin dadi Mamyn tayi, cikin farinciki kuma tace.

“Masha Allah,eh munyi magana dashi, washegarin tafiyarsa Ramadan ya k’ira ya kuma bani wayar mun gaisa.”

Kai Abban ya jinjina.

Dai-dai lokacin kuma Ramadan ya turo k’ofar falon ya shigo.

Akusa da Mamyn nasa ya zauna, bayan yayi musu sannu da gida ne kuma, ya sake dagowa ya kalli Mamyn nasa, cikin sanyi yace.

“Mamy kina ta zaune duk gidan babu dadi ko?”

Kai Mamyn ta jinjina masa alaman “Eh.”

Hakan kuwa shiyasa Ahankali ya d’an gyara zamansa, tare da cewa.
“Ai Mamy na fad’a miki cewar gidannan bazai yi dadi ba, matukar babu su Hamma Rayyern, duk gidan ya rame mun zama abun tausayi.”

Murmushi Mamyn tayi tare da kallonsa, domin ita ta gama sanin ayanzun me yake nufi, wanda kuma yanzu suka gama maganan abunda yakeso din da Abba.

Cikin son kawar da zancen nasa tace.

“Yauwa kiramin Riyyam nsra mana.”

“To.”
Ramadan din yace tare dayin dialing numbern Riyyam, bugu biyu ya d’aga, bayan sun gaisa ne kuma ya bawa Mamyn waya.

Mamy na amsa Daga can b’angaren Riyyam nsra yace.

“Wallahi I miss you so much Mamy na, nayi missing girkinku keda Aunty Jannart.”

Murmushi Mamy tayi kana cikin danjin dadi tace.

“Muma munyi kewarka Riyyam ya Mammyn ka da kuma Zaytoon?”

“Duk Suna lafiya Mamy yasu Abba, da Hamma Rayyern na, bani da numbernsa na k’asar Mascow.”

Riyyam  din ya tambaya cike da kewa.

Mamy kuwa fuska asake tace masa duk suna lafiya,
Haka dai suka d’an tab’a hira kafun daga bisani sukayi sallama.

Acan Mascow kuwa, kamar dai jiya yau d’inma sai k’arfe biyar, su Rayyern suka tashi ataron nasu.

Ahanyarsa ta dawowa ne kuma ya biya, Halal Mascow on top restaurant ya saya musu abinci.

Koda ya dawo wanka yayi tare da dawowa, falon ya zauna, tashar CNN yake kallo, Ahankali kuma yake d’an cin abincin dake gabansa, wanda kwata-kwata shi yanzu ba wani dadin abincin yakeji sosai ba.

Bayan ya kammala cin abincinne kuma ya wuce masallaci.

Jannart din kuwa kamar jiya haka yau d’inma ta fito taci abinci, saidai bata wani ci sosai ba, drinks din kawai tasha ta koma ta kwanta.

Taso yin k’ira amma kuma tasan layinta, bazai yi amfani awannan k’asar ba sabida bata da kati ko asi, shiyasa ta hakura, gashi shi kuma tun ranan da suka zo ba ganinsa ma takeyi ba.

Wannan dalilin yasa kawai ta soma buga game,  tana cikin yin game dinne kuma bacci ya d’auketa.

*Ethiopia.*

Riyyam-nsra ne zaune akan sofan, dake cikin katafaren falon Mammynsa, daga  can gefensa kuwa Mammyn nasa ce, sai Kuma Zaytoon itama dake gefe.

Kakarsu Didi kuwa kwance take akan kujera.

Riyyam-nsra din ne kuma ya d'ago kansa, tare da jingina da jikin Mammynsa, cikin farinciki da kulawa yace.

"Mammy duk wani abun da muke zato da tunani ya tabbata, Mammy Nigeria tsatson mune, kuma jigonmu ce acan tushen farin cikinmu suke, wallahi Mamy ni harma naji na gaji da k'asar nan, inason komawa k'asata ta Haihuwa kuma k'asar mahaifina."

Ya k'are maganan cikin wani irin bege me karfi dake fusgarsa.

Zaytoon dake zaune agefensa ne ta d'an langwabar dakai, kana Cikin sanyi tace.

"Har gwara kaima Riyyam kaje kaga k'asar, kaje ka ga abunda ni idanuna suka kasa ganemin kaje ka ƙamshin ƙasarmu ka shaƙi iskar ƙarmu."

Idanunsa ya d'an lumshe kana cikin son bawa y'ar uwartasa k'arfin guiwa yace.

"Insha Allah kema zakije Zaytoon, auren Hamma Ramadan na tashi, Mamy zata je kema kuma zakiji harma da Didi, nikam naji dadin zama cikin ahalina, nayi farinciki sosai Ina kuma fatan kasancewa dasu har abada."

Idanu Mammy ta d'an lumshe cikin kuma yanayin sanyi tace.

"Insha Allah Riyyam komai zaiyi dai-dai, watarana komai zai wuce mubi komai ahankali."

Fuska Riyyam din ya d'an kwab'e, kana cikin salon shagwab'a yace.

"Mamy wani irin ahankali tsawon shekaru fa muna zaune ahaka, ayanzu kuma gaba d'aya komai ya tabbata."

Gyara zama Mammyn tayi kana cikin kulawa tace.

"Riyyam nima inaji ajikina cewar watarana zanje, zuciyata ta zak'u akan naje din, saidai bansan meye zuwan nawa zai haifar ba Riyyam, duk wani abu da kake tunani ya wuce nan, har yanzu akwai k'ullin da bai gama warwarewa ba, amma nasa araina cewa Insha Allah zanje watarana, saidai kuma akwai buk'atar muyita addu'a, saboda Allah ya sauk'ak'a mana duk wani tsanani."

Da "Ameen." Duk suka amsa, kana daga nan kuma suka ci gaba da hirarsu.

Ahaka rayuwa taci gaba, aduniyar Rayyern da kuma Jannart, babu wanda yaga d'an uwansa tun zuwansu Mascow'n, wanda ak'alla yau kwanansu shida suna neman na bakwai kenan.

Ko yanzun kuwa Jannart dince ke zaune acikin falon,  zaman nan tayi irin na tankwashe kafafu.

Yayinda take sanye da wani pencil jeans pink colour, da kuma wani t-shirt sai jacket mai nauyi da ta d’aura akan shigar tata.

Ahankali ta dan daga kanta sama, tare da kwantar da kannata ajikin kujera.

Yanayin zaman da tayi dinne kuma yasa, gaba daya duk wani shati na halittar jikinta ya bayyana, more especially breast dinta, wanda ko bra bata saka ba, gashi kuma rigar sanyin nata ya Dan bud’e kad’an.

Idan ka kalleta azahirance zakayi tunanin cewar bacci ne ya d’auketa ahaka, saidai kuma azahirin gaskiya bawai hakan bane, domin gaba daya tunaninta ya tafi ne izuwa Gida.

Ayanzu tunanin halin da Dadynta dasu Abdull suke ciki take, domin tasan koma yaya basa cikin yanayi mai dadi, gashi kuma tunda tazo k’asar batayi waya da Abba Kabir dinta ba ko su Mamy da Ramadan batayi mgn dasuba gaba ɗaya kewarsu ya dabaibayeta.

Ahankali ya turo k’ofar falon ya shigo, hannunsa rike da ledan restaurant da kuma suit d’insa.

Shigowarsa cikin falon kuwa shiya saka shi sauk’e idanunsa akanta.

D’an tsayawa yayi yana me kallonta, tun daga k’afafunta dake tankwashe, har zuwa kan lafaffen cikinta, da kuma kirjinta zuwa dogon wuyanta.

Idanunsa ya d’an k’urawa soft neck din nata, wanda yake dauke da dan siririn chain, sosai wuyan nata ke da kyau ga wani layi layi,  Ahankali ya kuma dawo da kallonsa ga kirjinta.

Lokaci daya kuma cikin sauri ya janye, idanunsa daga kallonta.

Ledan dake hannunsa ya ajiye, tare da ci gaba da takowa  ya k’arasa shigowa cikin falon.

Jannart kuwa jin alamun takunsa ne yasa ta saurin d’ago Kanta, karab kuwa Idanunsu suka sark’e acikin na juna.

Wanda hakan yasa taji zuciyarta tayi wani irin bugawa, lokaci d’aya kuma taji wani irin rauni ya lullub’e zuciyarta.

Ahankali tayi k’asa da kanta, tare da da hannu ta gyara zaman rigar sanyin ta.

Cikin wata irin sanyin murya mai dauke da shagwab’a tace.

“Sannu da dawowa.”

Idanunsa ya d’an lumshe
tare kuma da kawar da kansa, murya akasalance da kuma gajiya yace.

“Uhummm.”

Yanayin yanda ya amsa da Uhummm dinne kuma ya sata lumshe ido, saboda hakanan taji yanayin nasa na kasala, ya tada mata da tsikar jiki.

Ahankali Rayyern din ya soma tafiya, har yakai bakin k’ofarsa kuma saiya juyo, ya kalleta, wani abu yakeson ce mata, amma hakanan sai yaji bakinsa yayi nauyi kana shi kansa bai san me yake son ce matanba, hakan kuwa shiyasa kawai ya wuce daki.

Jannart kuw najin alamun ya shige bedroom ne, yasa Itama ta tashi ta wuce nata dakin, yau ko abincin daren ma bata ci ba.

Shikuwa Rayyern Bayan yayi wankane ya dawo falon, abinci yaci tare da komawa dakinsa ya kwanta.

Washegari kuwa kamar yanda ya saba haka ya fita bayan ya ajiye mata breakfast.

After 2weeks.

Ahaka sukeyin rayuwarsu ita dashi, daga wannan ranan kuwa babu wanda ya sake Ganin d’an uwansa, saidai kullum yana ajiye mata breakfast da kuma dinner, da rana kuwa saidai ta ci ragowar breakfast.

Gaba d’aya duk kad’aici ya dame ta, duk da ta saba da hakan amma yanzu batajin dadin hakan.

Shikuwa Rayyern gaba daya yanzu ya zama busy, domin course din da sukeyi din ya fara nisawa, shi yasa always he’s busy.

Daya dawo kuma ya gaji sosai, daga ya d’an tab’a system d’insa sai bacci.

Yau din kuma tunda ya fita da safe baidawo ba, domin Koda suka tashi ataron nasu, still meeting ya shiga da wasu manyan Doctors na k’asar.

Koda lokacin sallan magriba yayi, bayan yayi sallan meeting din ya sake komawa haka ma sallan Isha.

Basune suka tashi a meeting dinba kuwa sai 1:00 pm.

Agajiye yake sosai yau din, dan ko dak'yar ya iya biyawa ta restaurant ya saya abinci,  da wasu chocolates d'insa, tun acikin mota kuwa yake cin chocolates din ahaka harya iso gida.

Koda ya dawo gidan kusan 11 ake nema.

Haka ya shigo cikin falon, yana mejin yanayinsa na d'an sanjawa, saboda yanzu Kwata-kwata baya ma shan maganinsa, especially now daya zama busy.

Direct d'akinsa ya wuce, tare da sakarwa kansa ruwa.

Itakuwa Jannart tana can cikin d'aki, duk yunwa ya isheta saboda duk yau bataci abinci ragowar breakfast din nata ba.

Tafito falon nasu kuma bata ga komai ba, wannan dalilin yasa ta koma ta kwanta, saidai duk yanda taso bacci yaki daukanta.

Ganin hakanne kuma yasa ta sha ruwa, tare da komawa ta kwanta, ahaka wani baccin wahala ya dauketa.

Ab'angaren Rayyern kuwa yana fitowa daga wanka, kaya ya sakawa jikinsa, batare daya sake bin takan abincin daya kawo ba, ya haura saman gadonsa, bacci ne sosai a idanunsa, shiyasa yana kwanciya bacci ya d'aukesa.

Washegari.

Saturday.

Bakamar sauran ranakun ba, kasancewar yau din weekend ne yasa, bai fito da wuri ba har sai 9:00pm.

Ahankali ya bud'e k'ofar bedroom din ya fito, maida k'ofar yayi ahankali ya rufe.

Ya juyo ya fuskanci cikin falon,  idanunsa ya dan waro lokacin da suka suka sauk'a Akan...!

*Albishirinku! Ma'aurata, GA GARKUWAR KU nan tafe muku da tsarabobi na musamman gareku ma'aurata daga cibiyar mgnin mata mai taken  GARKUWAR MA'AURATA*

NI DAI AYSHA ALIYU GARKUWA.
Ina matukar mamakin wani irin lokaci da ya riske mu mai wahalallan fassara. Kullum dai magana daya ce, akan ma'aurata, fada, rashin jituwa, mutuwar aure, akan kuskure kalilan, rashin kula, rashin yi wa juna uziri. Toh wai duk me ya janyo hakan? Na zurfafa a tsananin

tunani hakan ya tilasta min bincike mai tarin yawa wanda ya kai ni ga gano inda matsalar take? Shin yar'uwa ke macece amma kin san wacece mace ku? Kin san me ake kira mace kuwa? Mace ita ce matar da take zama iyali a wajan namiji ta zame masa bango, sanyin idaniyarsa, ta zame masa gata da farin cikin rayuwarsa ta zame masa ruwa abar kore ƙishinsa ta zame masa mayafi mai karesa daga gigitar kadaice, ta kuma dorar da mijinta kan turbar gaskiya, ta kashe masa jiki da salonta ta rikita shi da baiwa da ni'imar da Allah ya bata idan har ta san hanyar mayar da kanta sabuwa dal awajanta, wato kullun takasance masa tamkar amarya har ya kasa tantance daren amarcinsu da sauran dararen rakun rayuwar su.

Wannan ita ce mace. Ina da wata saukakkar hanyar da zaki zama abar so da kulawa da soyayya a wajan mijinki ta hanya mafi sauki, 09097853276 hanyar ita ce ki gwada amfani da kayana na gyara ki gani, ina mai tabbatar miki da in sha Allahu sai kin dara da murna sai kuma kin gode min. Kayana kaya ne da aka yi shi da zallan itacanmu na gado marasa illa a cikin jikin dan adam musamman mace, kaya ne da suke taimakawa (sex hormones 😍) dinki.
Misali kina kallon India😘, hollywood, Asian film🥰 kina ganin yanda mazansu ke nunawa matansu tsananin soyayya kamar su ba su kyautar ransu!?
Saboda me hakan? Saboda suna sadaukar da lokacinsu wajan gyara jikinsu da kayan da ke tsattsafo da ni'ima cike da tsukewa, kayan nan kuma ana yinsu ne zallar magungunan gargajiya wanda ba su da illa domin haɗine na ingantattun itatuwa da yayansu.
Ina baiwar Allahn da miji ke daure mata fuska babu hirar arziki?
Zo ki ji yar'uwa zan baki gumbata da zallar gari wanda aka yi su da nagartattun itacen da ke da matukar amfani a jikin mace. Gubar ciko, gumbar tsalle dole, gubar da ba'a baiwa mai kishiya, garin maɗi, garin mallaka, tsumin goron tula, tsumin tsartai, tsumin maratsi, pala-pala butar sirri, kwanon k'asaitacciyar mace, furar mata madadararta gareki Hajia takenta sha yanzu mgni yanzu, Ina mata masu fama da sanyi? Sanyin mara ki zo na hadaki da magani na na sanyi wanda yake wanke mara ya fitar da duk wata cuta da ke samun mazauni a wajan.
Ina da ciccibi mai kyau. Ina da hadin amare mai kyau wanda zai gyara yarinya ya kankaro mata kimarta akwai hadin mai jego wanda muke yinsa na asali inada kekkyawan Hadi maida tsohuwa yarinya.

Akwai daya bangaren wato *KAMSHI*
Kimarki gyaranki da kamshinki. Matan da suka gane suka san yanda za su kankaro da mutunci su ne masu amfani da kayan gyara da kuma sanyaya jikinsu da kamshi, ina da turaren wanka da na bandaki na daki na jiki da na kaya dana tsuguno kamshin turarena na dabam ne mai sanyaya zuciyar wanda ya shaka ina da kayan kamshi na amarya da na maijego da na uwargida da dukkan macen da take kokarin mayar da kanta mai daraja a idon kowa ta zamo sarauni a idon mijinta, akwai shu'umar humra, sayan na gari maida kuɗi gida, banda karanta yayin gyara Hajia.

Zaku iya samun kayyakina a duk garin da kike, zakiyi min mgn ta whatsApp number na 09097853276 domin yin zaɓinki, ko karin bayani, zaki tura kuɗin ta account na 0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU in mun gama mgna zan sa miki kaya a mota yazo duk garin da

kike, in baki shirya saya yanzuba Please kada mu wahal da juna ki bari sai kin shirya kafin kiyi min mgn.

🤝🥰😘 Daga taku AYSHA ALIYU GARKUWA
*(GARKUWAR MA'AURATA)*

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:47 - 🥰🥰: Abincin daya kawo jiya da daddaren, idanunsa ya d’an zubawa ledodin, wanda da dukkan alamu babu wanda ya tab’a su, Dan suna nan kamar yanda ya ajiye su.

numfashi ya d’an fesar tare da soma takowa, ya k’araso tsakiyar falon, inda abincin ke ajiye.

Isowarsa wajenne kuma ya sake tabbatar masa da cewar, tabbas babu alamun an tab’a ledodin.

Bakinsa ya d’an tab’e tare kuma da komawa ya zauna, akan d’aya daga Cikin kujerun falon, idanunsa ya d’an lumshe Ahankali, dai-dai lokacin kuma daga can waje aka soma knocking kofar falon.

Ahankali ya d’an bud’e idanunsa, tare da mik’ewa tsaye, saboda already dama yayi musu order’n breakfast, to yanzun ma yasan breakfast din nasu ne ya iso.

K’arasawa yayi ya bud’e k’ofar tare, da karb’an ledodin breakfast din.
Kana ya dawo ya zauna akan sofa.

Duk da cewar baya wani jin yunwa sosai, amma hakan baisa shi kincin abincin ba, bud’e ledan yayi ya somaci, saidai bai wani ci sosai ba ya ture abincin gefe.

Yanda yaji duk baya wani jin dadin cikinsa ne kuma, yasa shi mik’ewa ya koma d’aki,  sachet din maganinsa ya d’auko, tare kuma da dawowa falon ya zauna.

K’wayoyin maganin da sukayi saura ya zubawa ido, wanda kwata kwata basu wuce guda 16 ba, kasancewar akowacce rana mutum zaisha guda d’add’aya ne.
To Yanzu dai way’anda suka rage masan, basu wuce na 2weeks ba, banda ma yayi wasa da shan maganin yasan da yanzu basu Kai haka yawa ba.

B’alle maganin yayi ya saka abakinsa, tare da Korawa da ruwa marar sanyi.

Bayan yasha maganin ne kuma ya mik’e tsaye, babban agogon Bangon dake sak’ale acikin d’akin ya kalla, wanda yake nuna masa 12:pm dai-dai kenan na rana.

Ajiyar zuciya ya d'an sauk'e tare da d'aukar wayarsa, hadi da car key d'insa, domin duk da cewar yau din weekend ne, amma suna da test da zasuyi akan, yanda ake dashen k'oda, wanda kuma yau dinne firstly da zasu fara, gwaji akan abunda aka koya musu.

Kaitsaye ya fice daga cikin falon, direct wajen da ya ajiye motarsa ya nufa, Ahankali ya d'aga kansa yana me Kallon yanayin garin, duk da kasancewar yanzun rana ne, amma sudai awajensu tamkar safiya ne, saboda gaba d'aya yanayin garin babu rana, sai wani irin sanyi mai ratsa cikin k'ashi da bargo, ga kuma dusan k'ank'ara da yake sauk'owa daga sama.
Snow kawai tako ta ina.

Yana shiga cikin motar kuwa yayi mata key, tare da cillata kan titi, kaitsaye ya nufi wani babban asibiti.
*JSC MEDICINA CLINIC MASCOW,* domin acanne zasu yi karatun nasu na yau.

Jin k'aran tashin motar ne, yasa ta bud'e Idanunta dake lumshe.
Ahankali takai dubanta ga jikin window'n dakin nata,  wani irin sassanyar numfashi ta fesar, tare kuma da d'an yunk'urawa ta tashi ta zauna, Allah ya sani tana matukar shiga takura, azaman da takeyi ita d'aya acikin gidan, tana buk'atar waya sosai, amma bata da yanda zatayi, saboda tasani layinta ba kudi, shi kuwa gaba d'aga ya shareta, akullum yanayin abu tamkar baisan da zamanta acikin gidan ba.
Gashi tun da suka zo ko fita bata tab'a yi ba ko dan harabar gidan.

D'an k'aramin tsuka taja, saboda gaba daya ta gaji da kwanciyar da takeyi.

Ahankali ta sauk'o daga kan gadon, tare da zubo da k'afafunta k'asa.

Kallon kanta tayi, saboda sanye take da wani dogon wando mai kauri, wanda ya kama jikinta sosai, sai kuma wani top long sleeve, shid'inma dai mai kauri ne sosai, still kuma sai wata riga jacket da ta d'aura akan shigar nata, kanta kuwa sanye yake da hulan sanyi.

D'an kwab'e fuska tayi, domin duk da irin shigar da tayi din, bai hanata jin sanyin da akeyi ba, Sam har yanzu bata saba da sanyin garin ba.

Wayarta dake kan bedside ta d'auka, sanin da tayi cewar Rayyern din ya fita ne, yasa kaitsaye ta nufo falon.

Koda ta fito kuwa tv ta kunna, saidai gaba d'aya babu wasu channels, sai zallan na turawa, ba haka ta soba amma dole ta hakura, zama tayi tare da bud'e ledodin breakfast din da taga ya ajiye.

Chinese dishes ne, da kuma African dishes, kamar dai yanda ya saba yi musu order akoda yaushe.

Fuskarta ta d’an kwab’e tare kuma da turo d’an k’aramin bakinta gaba.
Cikin shagwab’a tace.

“Ni gaskiya I’m tired da way’annan foodies din, always abu d’aya ni nagaji, Nigerian dishes nakeson ci, me zanyi da Chinese dishes niba
mai kananan idanu ba.”

Ta k’are maganar cikin tura baki tamkar Rayyern din yana gabanta.

Haka dai ta d’an tsakali abincin taci, domin kwata kwata bata iyacin chinese dishes din.

Bayan ta kammala cin abincinne kuma, ta haye saman kujera ta kwanta.

*Kano Nigeria*

Abba da Mamy ne ke zaune, acikin katafaren falon nasu, inda Abban ke zaune akan sofa, Mamy kuwa na durk’ushe agabansa tana had’a masa coffee.

Abban ne ya d’ago kansa ya kalli Mamyn, kana cikin kulawa yace.

“Ni kuwa Ruƙayyah ya labarin y’arki Jannart, tunda suka tafi  kun gaisa da ita kuwa?.”

D’agowa Mamyn tayi ta kalli Abban, domin dama kamar ya Sosa mata inda yakeyi mata k’aik’ayine.

Numfashi ta d’an fesar, cikin kuma rashin jin dadin abunda zata fadad’in tace.

“A’a ba muyi waya da ita ba har yau, kwata-kwata bansan me yake damun Rayyern ba, domin duk sanda zamuyi waya dashi, Idan nace ya bawa Jannart din wayan, sai yace min baya gida, To amma kuma nasan bazaimin k’arya ba, saboda dama ba zamanne ya kaishi ba, kasan Rayyern da sabgogi.”

Kai Abban ya jinjina, tare da gyara zamansa, cikin sanin halin Rayyern din yace.

“Ni ai banma tambayesa itaba, saboda nasan dole wani uzurin zai kawo, amma yanzu ke kinyarda da uzurin da yake baki, na cewar ko yaushe baya gida?  ai tunda yana da lokacin da zai iya dawowa gida yayi bacci yayi wonka ya sauya kaya, To yana da lokacin zama ya bata wayar ku gaisa,  bansan Meyasa Rayyern yake haka ba, da gasken gaske na fahimci cewar, zama da Mace ne bazai iya ba, saboda baisa abun acikin zuciyarsa ba shiyasa, amma babu komai na zuba masa ido, awannan karon zanga iya gudun ruwansa a gari irin Mascow mai yanayi na musamman da kuma mace kamar Jannart da kuma keɓantaccen wuri zan bishi da ido inga iyakar yaudar da zuciyarsa ke masa na cewa zai iya rayuwa ba mace.”

Ajiyar zuciya Mamy dake gefe ta sauk'e, cikin nazartar maganganun mijin nata kuma murmushi tayi tare da  cewa.

“Tabbas nima dai sau dayawa ina mamakin yanda yake cewa baya gida, amma da fari na yarda da maganganunsa, saboda kasan Rayyern bai cikayin k'arya ba, Dan banace baya k'arya ba kwata kwata arayuwarsa, saboda babu wani d'an Adam d'in da baya k'arya a dai wannan ƙarni namu, saidai na wani yafi na wani amman dan nasan karya ba dabiarsa bace,  amma gaskiya nidai kam jikina yayi sanyi, kada fa Rayyern yaje ya ajiye y'ar mutane ne, kawai ya fita harkarta.”

K'wafa Abban yayi tare da d'aukan kofin coffee din nasa, cikin yarda da hukuncin da zuciyarsa ke yanke masa yace.

“Hmmmm zanyi magananinsa kuwa Idan har hakan ta kasance, saboda matarsa ce ko da ace bayasonta kuwa akwai, hakkinta da ya rataya awuyansa, amma ki barni dashi kawai.”

Abban ya k'are maganan yana me Kai kofin bakinsa.

Mamy kuwa shiru tayi, saboda tasan idan abun da tayi yakini gaskiya ne, to kuwa Rayyern bai kyauta ba.

Ganin da tayi kuma Abban ya ci gaba da shan coffee dinne, yasa ta tashi ta wuce kitchine Dan k'arasa had'a abincin dare, domin bata son Ramadan ya dawo ya samu bata gama had'a abincin ba, kasancewar yanzu duk hankalinsa, ya koma kan hospital dinsu, tun safe Idan ya fita sai bayan magrib yake dawowa, hatta yau Weekend ma bai zauna ba.

*Moscow.*

Gaba d'aya cikin d'akin da suke gwaji din, ya d'auki shiru babu abunda kakeji kuwa, sai k'aran na'urori da kuma sanyin, AC dake tashi duk da sanyin dake garin kuwa, amma yanayin aikin da sukeyi din yana tsananin buk'atar sanyi.

Yanayin test din nasu kuwa ya  kasu kashi biyu ne, domin kanana daga cikin Doctors din suna gwada aikinne, akan robot ma'ana wasu halittun da aka kirkira ma tsakaita kuwa, akan halintun kananan dabbobi sukeyi nasu gwajin.

Yayinda manya manyan Doctors din, da suka amsa sunansu masu experience ke gwada, aikin akan mutane majinyata way'anda, suke fama da lalurar kidney.

Acikinsu kuwa harda Dr. Rayyern Bashir Muhammad Mai-nasara, wanda ya bada gaba d'aya attension d'insa, akan wanda yakeyiwa aikin,  agefensa kuwa Dr. Sulaiman ne da kuma Dr. Nick Michel, wanda shima Babban Dr. ne ak'asar France.

Saidai duk da k’warewansa idanu ya zubawa, Rayyern alokacin da yake aikin dashen k‘odan.

Saboda su iya nasu mik’o masa kayan aiki ne.

Adai-dai lokacin da Rayyern ya kammala, dasa k’odan bayan ya d’inke cikin mutumin dake kwance, ne ya sauk’e wani irin nannauyar Ajiyar zuciya, tare kuma dasa hannu ya dafe saitin zuciyarsa.

“Yah Rabbi”

Ya k’ira sunan Allah abayyane,
Cike da gamsuwa hadi da samun k’arfin guiwa, da yarda akan cewar Allah’n ne maiyi, shine kuma mai bada sa’a akoda yaushe shike rayawa ya kuma kashe.

Kashe wutan theater room din da yake ciki yayi, da kansa kuma ya turo gadon da mutumin ke kwance har zuwa wani extra room, wanda acikinsa ne za’a jere way’anda akayiwa surgeryn, saboda a tabbatar da lafiyarsu.

Kusan Atare Doctors din suka kammala aikin nasu.

Yayinda zuciyoyinsu ke cike da alhinin, yanda way’anda sukayiwa aikin zasu tashi.

Dukansu kuwa Fatansu shine, patients din su tashi lafiya batare da wata sabuwar matsala ba.

Almost 1hour suna zaune cikin zullumi, saboda har yanzu babu d’aya daga cikin majinyatan da ya farka.

Ak’a’idan aikin nasu kuwa, wanda patient d’insa ya fara farkawa batare kuma da wata matsala ba shine yazo first.

Cikin sa’a kuwa Patient din Dr. Rayyern Muhammad Mainasara ne ya fara bud’e idanunsa.
Inda kuma ya tashi garau batare da juyewan, brain ko haddasuwan wata matsalan ba, Dan Koda ya bud’e idanunsa acikin hayyacinsa yake sai yan kananun surutan da suke dole, bayan ƙaƙkanin lokaci kuma ya zama dai-dai.

Wani irin farinciki na ya cika zuciyar Rayyern, lokaci d’aya kuma ya shiga godewa Allah, saboda yasan bayin kansa bane, kowacce Nasararsa daga Allah ne.

Gaba daya Doctors din sun Taya Rayyern farinciki, tare kuma da mamakin k’warewarsa, musamman Envigelators da suka kasance consultant's ne, saboda basu tab’a tunanin wani Daga cikin Doctors din zai k’ware da sauri akan abun har haka ba, musamman ma shi da yake d’an Nigeria, basu tab’a tunanin shi zaiyyi wining ba.

Domin faruwar hakan alamace dake, nuna musu babban nasararsa, shine kuma zai karb'i award na ban girma, tare kuma da certificate din da zai nunawa duniya, cewar shi babban likita ne, amintacce kuma yardajje akowacce k'asa.

Tabbas Rayyern yaji dadin hakan azuciyarsa, domin ko babu komai zai kankaro mutumcin k'asar sa.

Alhamdulillah Sauran
Patients dinma, da akayiwa operations din sun bud'e idanunsu, cikin sa'a kuwa kowanne da hayyacinsa ya dawo hakama nasu Dr Sadiq da sukayi gwajin su kan ƙananun dabbobi suma na Dr Sadiq ya tashi Ify bisa alamu gaba zai taka matakin da Rayyern ya taka a yau.

Sosai Doctors din sukayi kokari, harma way'anda suka gwada nasu akan mutum mutumi.

3:00 pm Dai-dai suka kammala, duk wani abunda zasuyi, Ganin garin nata k'ara gumewa da snow ne kuma, yasa duk suka watse, kaitsaye Rayyern ya nufo gida.

Saidai kuma kafun ya k'araso saida ya tsaya, amasallaci yayi Sallan La'asar, kana ya biya Halal restaurant yayi musu takeaway, na Arab dishes kafun ya nufo gidan kaitsaye.

Gaba d'aya yau din jin zuciyarsa yake wasai, badon komai ba kuwa saidan wannan nasarar daya samu.

Shigowa cikin falon yayi, tare da neman waje ya zauna, bayan ya zare jacket din dake jikinsa, kasancewar duk ta b'aci da dusan k'ank'ara dake dan sauka.

Kallon d'an table din dake cikin falon yayi, rashin Ganin ledodin daya bari awajen ne kuma, yasa shi gane cewar Jannart din ta fito, domin ta hakanne kawai yake gane fitowarta, ko rashin fitowarta, kasancewar Idan ta fito takan kwashe ledodin takai kitchine.

Ledan daya shigo dashi din, ya d'auko tare da d'aukan chicken kebab ya soma ci, bai wani ci sosai ba ya ajiye, sai kuma pizza da drinks din daya d'ansha.

Bayan ya kammala ne kuma kaitsaye ya wuce bedroom d'insa, saboda yana so ya d'an watsa ruwa.

Koda ya shiga bedroom din kayan jikinsa ya rage, tare da fad'awa bedroom ya sakarwa kansa ruwa.

Bayan ya fito awankanne kuma ya shirya, kansa cikin wasu Sabin riga da wando, tare da d'aura

wata jibgegiyar rigar sanyi akai.

Still kuma car key d'insa ya d'auka, direct ya fice daga Cikin gidan.

Daga gidannasa kuwa kaitsaye wani babban  shagon saida kaya ya nufa.
Mall Yevropeyskiy ya wuce kai tsaye dan yafi kusa da inda yake.
kayan sawa da kuma sweaters Chocolate's
masu yawan gaske ya saya.

Har ya juya zai tafi ne kuma, idanunsa suka sauk'a akan wasu, womenswears masu azabar kyau, wanda dukansu kaya ne da zasu tare sanyi.
Domin irin jibga jingan rigunan nanne da y'an k'asar suke sawa.

K'arasawa wajen clothes din yayi, tare kuma dasa hannunsa ya zaro wasu manyan jacket masu kyau, guda biyu ya ciro jacket din, sai kuma wasu wanduna masu kyau, way'anda ya ibosu sama da guda biyar haka nan yake kallonsu yana murmushin, a hankali ya lumshe idanunsa da alamun yana so  tuno wani abune.

Zuba su yayi acikin basket din dake hannunsa, kaitsaye kuma ya nufi wajen biyan kudi.

Koda akayi masa bill bai damu da yawan kudin ba, haka ya mik'a musu atm card d'insa suka cire.

Daga mall din kuwa, kaitsaye wajen sport ya nufa, saboda yana son dan motsa kafafunsa.

Acan gida kuwa Jannart tunda ta k'ule d'aki bata sake fitowa ba, ko da kwanciyar ma ya isheta bacci ne ya d'auketa, ba ita ta tashi ba kuwa sai dab Sallan Magriba, bayan tayi Sallah ne kuma, ta d'auko wani book dinta, ta soma karantawa.

Tana nan azaune har aka kira Sallah'n Isha, tana idar da Sallan kuwa ta haye kan gado, saboda sanyin garin ya sake yawaita.

Rayyern kuwa tunda ya fita bai dawo ba sai yanzun.

Ahankali ya bud'e murfin motar ya fito, tare da Kwaso manya manyan ledodin kayan daya saya, kaitsaye ya nufi cikin gidan.

Yana shiga cikin falon kuwa, idanunsa suka sauk'a akan, ledan abincin daya sayo d'azun, babu alaman an tab'asa.

Kauda kansa gefe yayi, for the first time kuma kenan daya d'aga, idanunsa ya kalli kofar dakin nata haka nan yaji kamar ba dadi.

Bakinsa ya d’an tab’e kana kaitsaye ya wuce dakinsa.

Yana shiga ya dire ledodin dake hannunsa, tare da wucewa toilet yayi wanka, bayan ya fito ne kuma ya shirya kansa, cikin wasu kayan bacci masu nauyi.

Hayewa saman gadonsa yayi, tare da kunna laptop d’insa, ya soma receiving sakonnin da ake turo masa, kaitsaye sakon maganer’n Companynsa ya fara dubawa, inda yake shaida masa yanda abubuwan companyn suke tafiya, da kuma yanda manyan y’an kasuwa, ke zuba hannun jari acikin companyn, komai dai yana tafiya normal.

Domin Koda ya duba details na companyn, ya ga abun na tafiya akan dai-dai.

Iya sakon da yasan suna da muhimmanci yayi replying, sauran sak’onnin kuwa ko duba su, baiyi ba ya kashe laptop din nasa.

Idanunsa ya d’an lumshe, dai-dai lokacin kuwa wayarsa dake gefe ta soma k’ara.

Ganin sunan Ramadan na yawo akan screen, din wayar ne kuma ya sashi d’agawa, tare da kara wayar akan kunnensa.

“Good Evening Hamma Rayyern, I hope you’re okay.”

Daga can b’angaren Ramadan din ya tambaya.

Idanunsa ya d’an lumshe tare kuma da gyara kwanciyarsa, Cikin kulawa yace.

“I’m Okay Ramadan, you? Ina Mamy da Abba?”

Murmushi Ramadan yayi tare da cewa.

“Same to you Hamma, Mamy da Abba kuma suna lafiya, Ina Aunty Jannart?”

Idanunsa ya d’an lumshe, kana cikin yin kasa da murya yace.

“Tayi bacci.”

Kai Ramadan ya jinjina, Jin kamar Hamman nasa agajiye yake ne kuma, yasa shi danne dariyarsa,  domin shi wani tunani na daban zuciyarsa ta basa.

“Okay Hamma gud night, but please ka gaishemin da Aunty Jannart Idan ta tashi.”

“To.”

Rayyern din ya fad'a agajarce, domin bayason Ramadan ya sake yi masa wata tambayar, daga haka sukayi sallama.

Ahankali ya zare wayar daga kan kunnensa, tare da mik'ewa tsaye, ya k'arasa gaban fridge din dake cikin dakin.
Koda ya bud'e fridge din dan siririn tsaki yaja, saboda ganin da yayi babu ruwa aciki.
Gashi kuma yana buk'atar ruwa, saboda tunowa da yayi baisha maganinsa ba.

Kaitsaye ya nufi kofar fita daga cikin d'akin.

Dai-dai lokacin kuwa Jannart, da fitowarta daga, d'akinta kenan ta nufi kitchine, saboda Itama ruwan take da buk'ata.

Saidai kuma ganin duhu da tayi afalonne yasa ta, d'an tsayawa tare da soma laluben inda makunnin wutan falon yake.

Dai-dai lokacin kuwa Rayyern din ya fito, ko kad'an kuwa duhun bai tsorata shi ba, kasancewar yasan kan gidan shiyasa, baya wani buk'atar haske kaitsaye, ya nufi kitchine din.

Dai-dai ya kawo tsakiyar falon ne kuma, itama Jannart din ta iso wajen, wanda Jin motsin mutum da tayi, ya saka duk ta tsorita, juyowan da zatayi ne kuma sukayi karo, inda take kafad'ansa ya bugi hab'arta.

Wani irin k'ara ta saka tare da saurin, sanya hannayenta ta kama hab'ar nata.

Rayyern kuwa d'an ware idanunsa yayi, saboda bai tab'a kawowa aransa cewar tana cikin falon ba.
Jin yanda tayi k'ara ne kuma yasa shi, matsawa cikin sauri ya kunna, wani dan blue din hasken wuta dake cikin falon.

Idanunsa ya sauk'e akanta, wanda har yanzu tana rik'e da hab'ar nata, ta kuma rumtse Idanunta, da alama ya bugeta sosai.

Ahankali ya soma k'arewa shigar dake jikinta kallo, wata doguwar riga ce mai kauri, sai kuma hulan sanyin dake kanta, Yayinda dogon gashin kanta ya sauk'o kan kafad'unta.

Duk da cewar hasken daya kunna din, bayi da karfi sosai, amma hakan bai hanashi kallon yanda fuskarta, tayi fayau ba, ga kuma shatin nipples dinta da suka bayyana, kasancewar gaban rigar nata akwai tsagu ne, kuma yasa yake iya ganin tsakiyan kirjinta, ma'ana tsakiyan breast dinta.

Idanunsa ya mayar kan fuskarta,  tare da soma takowa ahankali ya shiga matsowa inda take.

Dai-dai yazo kusa da ita ne kuma ya tsaya cak, kyawawan hannayenta ya kalla, akaron farko a iya tsawon rayuwarsu, ya sake matsowa kusa da ita sosai, har hakan ya bawa hucin nufashinsa dama sauk'a akan kirjinta.

"Meye?"

Ya fad'a da wata irin husky voice, din dake bayyana baccin da yakeji.

Jannart kuwa dake tsaye, Jin muryarsa da tayi akusa da ita ne, yasa ta saurin bud'e Idanunta da suka cika da k'walla, ta sauk'esu akansa.

Shek'in ruwan hawayen da idanun nata keyi ne, ya sashi jefa nasa idanun acikin nata, still cikin wata irin muryar daya kusan sata rud'ewa yace.

"Meye? Kinada damuwa ne? Me kikeso, uhummmm tell meeee."
Yaja ƙarshen mgnar cikin kasalalliyar murya a tausashe
Hawayen dake cikin idanun nata ne suka gangaro, lokaci d'aya kuma tayi k'asa da kanta, tare da had'e yatsun hannunta waje d'aya.

Shi kuwa Rayyern a hankali ya m...!

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:49 - 🥰🥰: "Naan please ka bud'e idanunka, Dan Allah kayi numfashi!!"

Ta kare maganan cikin matsanancin kukan, dake bayyana karyewar zuciyarta da rauninta.

Hakan da Dr. Sulaiman ya ganine kuma ya sashi, k'arasowa cikin falon da sauri, hankalinsa amatukar tashe yace.

"Innalillahi Wa'inna Ilaihirraju'un, please Jannart stop crying, kiyi min bayanin abunda yake damunshi."

Jin muryar Dr. Sulaiman acikin kunnuwanta ne kuma, ya sata d'ago Kanta da sauri cikin shasshshek'an kuka, kana murya asark'e tace.

"Ka taimakamin Doctor, Dan Allah ina tsoron ya rasa rayuwarsa, numfashinsa tafiya yakeyi, tun d'azu cikinsa keyi masa ciwo, kuma bansamu maganin da zan basa ba."

K'arasowa wajen nasu Dr Sulaiman yayi, cikin kuma tsananin yanayin damuwa yace.

"Calm down Jannart, Insha Allah Rayyern zai samu lafiya, ki daina kuka kinji."

Ya k'are maganar yana me lalub'o waya daga aljihunsa.

Rayyern dake rungume acikin k'irjinta kuwa, har yanzu da sauran numfashinsa, sannan kuma ahankali zuciyarsa ke bugawa, wanda kuma hakan na tafiya ne, da taimakon bugun zuciyar Jannart din da yake iya jiyowa acikin kirjinsa, kasancewar k'irjinsa da nata suna manne awaje d'aya.

K'warai yana so ya bud'e idanunsa da suke lumshe, amma kuma bashi da k'warin guiwar yin hakan,  saboda zuwa yanzu komai na jikinsa yayi sanyi.

Jannart kuwa ahankali tasa hannayenta, ta sake matsetshi acikin jikinta, still kuma hawayen dake kwance akan fuskarta na d'iga ajikinsa.
Duk ta rud'e Yayinda Idanunta sukayi ja sosai.

Dr. Sulaiman kuwa Ganin yanda take arud'en ne yasa shi d'an rank'wafowa, kana cikin kulawa yace.

"Ya kamata mu kaisa asibiti mafi kusa, domin bashi taimakon gaggawa, amma firstly yanzu sakeshi bari na fara sakashi a mota."
Ya ƙare mgnar yana matsowa kusa dasu,
Sunkuyowa yayi da niyar janye Rayyern dake jikinta.

Dai-dai lokacin kuma Rayyern ɗin ya fara wani irin numfarfashin masu nauyi.

Saurin girgiza kanta tasoma yi, cikin tsoro da kuma fargaban abunda ka iya zuwa tace.

"A'a Doctor Idan na sakeshi suma zaiyi fa.
Kalli yadda numfashinsa keyifa zai d'auke gaba d'aya, Ina jin tsoro ni dai bazan iya sakeshi awannan yanayin ba, Dan Allah kakira mana Dr yazo ya duba shi."

Ta kai k'arshen maganan nata tana me, sake rungume Rayyern din acikin jikinta, Yayinda hawayen dake kwance akan fuskarta kuwa ke ci gaba da tsiyaya, tamkar ankunna famfo.

Baki Dr. Sulaiman din ya bud'e da niyar cewa wani abu, saidai kiran daya shigo cikin wayar tasa ne, yasa shi yin shiru tare da d'aukan wayan ya kara akan kunnensa.

Daga can b'angaren Ramadan jin Dr Sulaiman din ya d'aga wayan, cikin tsananin tashin hankali yace.

“Please Dr ya ake ciki, ya jikin Hamma Rayyern din? Kun kaishi asibitin Ina fatan babu abunda ya sameshi?”

Ramadan yayi tambayan duk agigice.

Kai Dr  Sulaiman din ya girgiza, kana cikin yanayin damuwa yace.
“Ramadan ya zanyi Jannart ta rik’e sa gam, ta yanda babu yanda zan iya d’aukarsa, saboda tace wai Idan ta sakeshi suma zaiyi, na rasa makama Ramadan Domin ciwon nasa ya tashi sosai awannan karon.”

“Innalillahi wa’inna Ilaihirraju’un, Dr Sulaiman kayi wani abu mana, kayi wani abu kada Hamma na ya rasa ransa, Dan Allah ko Doctor ne kaje ka kira a waje.”

Ramadan ya fadi haka cikin tashin hankali.

Kai Dr Sulaiman ya jinjina, tare kuma da kad’a kansa cikin gamsuwa yace.

“Okay Ramadan amma inajin tsoron tafiya nabarsu awannan yanayin, Rayyern yana gab da suma, gashi Jannart kuma sai kuka take kamar zata shid’e, gaba d’aya na kasa iya control dinsu dukansu biyu.”

“Yah Allah help us.”

Ramadan ya fad’a cikin muryarsa da tayi rauni sosai, cike kuma da tausayin d’an uwan nasa, ga kuma Jannart dake ta kuka, domin daga cikin wayar yana iya jiyo sautin kukan da takeyi.

Jannart dake rungume da Rayyern din kuwa, kwata kwata bama tasu Dr Sulaiman din takeyi ba, damuwarta shine taga Rayyern din ya bud’e idanunsa.

Ahankali ta dawo da kallonta garesa, tare dasa hannunta d’aya ta tallafo hab’arsa cikin kuka tace.

“Dan Allah  Naan ka bud’e idanunka, kada ka daina numfashi, kada kuma ka cire rai da rayuwa in sha Allah, ai zaka samu sauki ko, nasan zaka warke zaka samu lafiya mu koma Nigeria Ify en Mamynka da Abbanka su ganka Ify, za kayi rayuwa kamar kowa muna bukatar ka a tsakiyar mu, dan Allah ka bud’e idanunka yanzu, ka dawo cikin hayyacinka Dan Allah...”

Ta k’are maganan cikin tsananin kuka da kuma raunin zuciya, ahankali kuma tasa hannunta akan kumatunsa tana d’an bubbugawa, cike dason taga ya bud’e idanunsa.

Idanu Dr Sulaiman ya zuba musu, lokaci daya kuma duk jikinsa yayi sanyi, musamman da yaga yanda Jannart din ke kuka sosai da sosai.

Maida wayar tasa cikin aljihu yayi, cikin sauri kuma ya d'auki key din motar Rayyern din, da ya gani akan table,  tamkar wanda zai tashi sama saboda sauri, haka ya sa Kai ya fice daga cikin falon.

Kaitsaye wajen da motar Rayyern din yake ya nufa, yana shiga kuwa ya cilla motar kan titi, tare da nufar  babban hospital din garin, wanda kuma shine mafi kusa dasu.

Jannart dake zaune kuwa duk da taji fitansa, amma bata d'ago Kanta ta kalleshi ba, Idanunta har yanzu suna kan fuskar Rayyern, still kuma ko wani d'igon hawayenta d'aya, da zai fita akan fuskarsa yake sauk'a.

Ahankali take yawo da hannunta dake kan hab'arsa, har ta k'araso zuwa kan kirjinsa. Lallausan tafin hannunta ta kife akan kirjin nasa, dai-dai saitin zuciyarsa, Jin zuciyar tasa na d'an bugawa ahankali ne kuma ya sata, lumshe Idanunta tare da motsa labb'anta cikin sanyi tace.

“Ya Allah ka taimaki Naanu na Yah Allah ka bashi lafiya, kasanya juriya acikin rayuwarsa, Allah kagani  bamu da kowa anan saikai, Kai ke kulawa damu akoda yaushe, Ya Allah yauma ka kula damu, ka saukaka mana tsanani izuwa sauki ya Allah ka rufa min asiri ka bawa Naanu na lfy.”

Takai karshen maganan hawaye yana me shatata akan fuskar nata.

Rayyern dake kwance ajikinta kuwa, duk wani abu da take fadi yana jinsu acikin kunnuwansa, saidai kuma yakanji kalaman nata da sautin amon muryar nata tamkar acikin mafarki, saboda gangar jikinsa ne kawai take wannan duniyar, hankalinsa kuwa ya tafi izuwa wata duniyar ta daban.

Suna ahakanne kuma k'iran Ramadan ya shigo cikin wayar Rayyern din dake gefe, Ganin sunan Ramadan ne kuma, yasa ta d'aga wayar da sauri tana k'arawa akan kunnenta, ta sake fashewa da kuka, still cikin muryar sheshshek'a tace.

“Ramadan har yanzu  baidawo cikin hayyacinsa ba, na shiga uku Ramadan banason wani abu ya sameshi, duk jikinsa rawa yakeyi, gaba daya ya fita ahayyacinsa, Ramadan ya zanyi....”

Sautin kukan nata ne yasa Ramadan d'an rumtse idanunsa, zuciyarsa cike da damuwa, da kuma tashin hankali yace.

“Zai dawo Hayyacinsa Aunty Jannart, Insha Allah nan bada  jimawa ba Hamma Rayyern zai dawo hayyacinsa, ki daina kuka dan Allah, ki kula dashi kafun Dr. Sulaiman ya dawo.”

Cikin kukan ta jinjina kai, saidai ta kasa cewa komai sai sheshshekanta da yake tashi.

Acan Nigeria din kuwa Mamy dake gefen Ramadan, itama hawaye takeyi gaba daya ta shiga cikin damuwa.

Haka ma Abba wanda ya zauna yayi ta gumi, abubuwa da yawa yake sak'awa acikin zuciyarsa, kallo daya kuma zakayi masa kafahimci cewa yana cikin matsananciyar damuwa.

Kasancewar kuma Ramadan din a hands free ya saka wayar ne, yasa dukansu suke iya jiyo kukan Jannart din, harma da nishin Rayyern dake tashi k'asa k'asa.

Ahankali Abban ya d'ago ya kalli Ramadan, da hannu Yayi masa alama akan ya bashi wayar.

Ganin hakanne kuma yasa Ramadan mik'a masa,  kara wayar Abban yayi akan kunnensa, cikin son b'oye damuwa da kuma tausasa murya yace.

“Jannart.”

Jannart dake zaune kuwa jin muryar Abban acikin wayanne yasa ta d'an zabura, cikin rawar murya tace.

“Abba Hamma! Hamma!! Abba jikinsa yana ta b'ari,  ga numfashinsa ya kusa d'aukewa, ciwo yakeji sosai, Dan Allah Abba ka taimakeshi.”

Idanu Abban ya d'an lumshe saboda tsananin tausayin yarinyar da yaji, domin ayanzu kukan ta yafi komai d'aga musu hankali sabida yanaga tashin hankali da take ciki zai hanata yin abinda ya dace.

“Jannart, Jannart!!”

Abban ya kira sunanta ahankali.

Yanda taji sautin muryar Abban ne kuma yasa ta, d'an tsagaita kukan nata tare da amsawa.

“Kiyi shiru kinji ki kwantar da hankalinki, ki daina wannan kukan In sha Allah Rayyern zai samu lafiya, ki daina kuka ki zama mai juriya akan ciwon sa kinji ko Jannart, yanzu addu'a ya kamata ki masa, ki daina kuka domin yawan kuka zai iya jawo miki wata matsalar kema, saboda haka ki share hawayenki Allah nanan kuma zai Iyar muku.”

Abban ya fad'i haka cikin son bata k'arfin guiwa.

Jin hakanne kuma yasa ta sanya hannu ta share hawayenta, cikin nuna biyayyarta agaresa tace.

“To Abba.”

Kai Abban ya jinjina cike da yabawa halin yarinyar, kana Ahankali ya zare wayar akunnensa ya kashe, saboda shi d'inma dazai samu dama, kukan zaiyi Domin har abada bazai tab'a son ace wani abu ya samu Rayyern din ba, haka kuma bazai so ace Rayyern yabar duniya batare da ya sauk'e wani k'aton nauyin dake wuyansa ba, Lallai zaiso ace Rayyern ya rayu, har zuwa lokacin da gaskiya zatayi halinta.
Baya ga haka kuma Rayyern din shine komai nasu, shine AHALI'nsu kuma k'ashin bayansu.

Ahankali ta zare wayar daga kan kunnenta, tare da lumshe Idanunta tana mejin yanda Rayyern din ke sake shigewa cikin jikinta, Yayinda ya saka duka hannayensa biyu ya rungume cikinta gam.

Wanda hakan da yayi din kuma alamace dake, nuna cewar yanajin ciwo sosai.

Acan b'angaren Dr Sulaiman kuwa.
Koda yaje EUROUPEAN Medical senter mascow (E.M.S) din emergency Doctor ya nema, bayan ya shaidawa Doctorn matsalan Rayyern din ne kuma, suka nufo gidan kaitsaye.

Suna isowa kuwa ko gama dai-dai-ta parking ba suyi ba, direct suka nufi cikin gidan Dan bawa, Rayyern din agajin gaggawa.

Jin motsin shigowar su Dr Rayyern dinne, kuma ya sata d'ago da kanta ahankali ta kallesu.

Dr James ne wanda Sulaiman din ya d'auko, ya k'araso cikin falon tare da matsowa inda suke, Cikin kulawa da kuma harshensa na turanci yace.

“Madam ko zaki iya matsawa na dubashi, saboda akwai buk'atar sai nayi checking nasa sosai.”

Idanunta da sukayi jajur ta zubawa farin baturen likitan dake gabanta, kaman mai nazartar wani abu, Cikin sheshshek'an kuka kuma ta girgiza masa kai, murya araunace tace.

“Ka dubashi ahaka saboda bazan iya barinsa ba, inaji ajikina Idan na barshi mutuwa zaiyi, Dr ka kalla fa numfashinsa seizing yakeyi, Dan Allah kayi sauri ka dubashi ahaka kada wani abu ya sameshi.”

Kai Doctorn ya girgiza saboda yasan duba, patient din ahaka ba abu bane da zai yiwu, saboda akwai buk'atar dole sai anyi checking d'insa, saidai kuma da gaske yaga Jannart ba zata tab'a bari a dubasa, ba tare da yana jikinta ba.

Sanin cewar Idan aka k'ara wasu mintuna ahaka komai zai iya faruwa ne, yasa doctor din matsowa, ya d'aura hannunsa akan wuyar Rayyern, tare dasa wani abu mai kaman na'ura adai-dai kan cikin Rayyern din.

Bayan ya gama saka abunne kuma, ya d'ago ya kalli Jannart dake hawaye, shikam har acikin ransa yana me mamakin k'arfin halinta.

Wani k'wayan magani ya b'allo daga cikin wani sachet, mik'a mata maganin yayi kana Cikin harshen turanci yace.

"Kisa masa wannan ak'asan harshensa, saboda zaifi saurin yi masa aiki, zai kuma yi tasiri acikin jijiyoyin jikinsa."

Da sauri ta jinjina kai tare da karb'an k'wayar maganin,  kasancewar har yanzu Rayyern din na kwance ajikinta ne kuma, yasa ahankali ta juyo da fuskarsa, ya zamana suna fuskantar juna, fuskar tasa da tayi ja sosai ta d'an kalla, cikin sanyi da kuma tsananin tausayawa, tasa hannunta na dama ta saka mishi cikin bakinsa, d'aya daga cikin yatsunta tasa ta d'an d'aga harshensa, tare da tura k'wayan maganin ak'asan harshen nasa, kamar yanda doctor d'in ya buk'ata.

Ganin nan take maganin har ya soma narkewa, acikin bakin nasa ne yasa ta, zare yatsarta ahankali tare da zubawa kyakkyawar fuskarsa idanu.

Lokaci d'aya har rama ta bayyana akan fuskar tasa, Yayinda saman fatar idanunsa sukayi wani irin ja, haka ma labb'an bakinsa, da tsabar ja tamkar zaka latsa jini ya fito.

Dogon hancinsa da ya tafi straight ta kalla, hadi da Zara zaran gashin idanunsa wanda sukayi wasar wasar.

Wani irin hawayen tausayinsa ne ya cika Idanunta,  wanda yasa ahankali tasa hannu ta shafa fuskar nasa.

Sauk'an d'umin hannunta akan fuskarsa ne kuma, ya sashi sauk'e wani irin ajiyar zuciya.

Ahankali kuma ya sake shigewa jikinta, batare da sanin abunda yakeyi ba kuwa, ya cusa fuskarsa acikin k'irjinta, domin ananne kad'ai Idan ya saka kansa, yakejin nutsuwa na saukar masa, duk da baisan cewa akan k'irjinta yake ba, amma aduk sanda ya d'aura kansa akan kirjin nata, yana iya jiyo sautin bugun zuciyarta, hakan kuwa na taimakawa zuciyarsa, wajen ci gaba da bugawa amaimakon tsayawa da take kokarin yi.

Jin yanda ya saka fuskarsa acikin k'irjinta ne kuma, ya sata lumshe Idanunta,  tare da d'aura hannunta akansa, ahankali ta shiga tura y'an yatsun hannunta, acikin tarin sumar kansa.

Dr James kuwa fatar jikin Rayyern din ya tsurawa ido, ganin yanda kowacce gashin jikinsa ke mimmikewa ne, kuma ya sashi zare wannan abu mai kaman na'urar daya lik'a masa acikinsa.

Ahankali ya koma kan kujera ya zauna, saboda yasan zuwa yanzu maganin daya bawa Rayyern din ya soma aiki, kasancewar yasan maganin yana da k'arfi sosai.

Ganin Dr James din ya zauna ne, yasa Dr. Sulaiman shima ya zauna.

Kallon Dr. Sulaiman James din yayi, cikin son bashi k'warin guiwa yace.

"Zaiyi sauki domin maganin dana bashi yana da karfi sosai, just 20mn zai samu relief don't worry."

Ajiyar zuciya Dr Sulaiman ya sauk'e, Dan bashi da wani burin da ya wuce haka.

Duk idanu suka tsurawa su Rayyern din, wanda har yanzu jikinsa ya kasa daina b'ari.

Jannart kuwa hab'arta ta d'an d'aura akan Rayyern din, tare da zubawa hannunsa dake kan marar tasa idanu.

Ganin yanda yake ta danna marartasa ne, yasa ahankali ta d'aura hannunta akan nasa hannun.

Aikuwa kamar jira yake hakan ya kasance, cikin sauri ya kamo hannun nata ya d'aura ak'asan nasa.
Ak'agauce ya shiga danna hannun nata asaman cikinsa,  wanda da dukkan alama anan yafi jin ciwon.

Ahankali hankali kuma ya shiga tura hannun nata zuwa kan mararsa, har dai ya zamana yatsunta na d'an tabo boxer d'insa, ma'ana asalin kan mararsa, wanda hakan yasa take iya tab'o, kwantaccen gashin dake saman marar tasa.

Ahankali ta lumshe Idanunta, da suke fitar da wasu irin hawaye masu zafi, duk da tasan cewar agaban su Dr Sulaeman suke, amma ta kasa janye hannunta daga inda ya kai mata, kuma Koda ace zatayi hakan ma, to ba zata samu dama ba, saboda wani irin riko da yayiwa hannun nata.

Sake damk'e hannun nata yayi, cikin kuma zafin ciwon da yakeji ya danna tafin hannunta akan mararsa da k'arfi.

Atake ya saki wani irin nishi da kuma Ajiyar zuciya mai karfi, still cikin gigita ya sake danna hannun nata akan mararsa, wanda ayanzu har tana iya jiyo tudun marar tasa.

Idanunta ta sake lumshewa, fahimtar abunda yake so dinne kuma yasa, Ahankali ta soma yawo da hannunta akan marar tasa, tare da d'an daddanawa tana yi masa massaging jin yanajin sassaucin ciwon yasa cusa hannunta cikin boxer ɗinsa kad'an yana mai danna hannunta.

Dai-dai hannunta ya iso saman penis d'insa ne kuma, ta d'an danna kad'an, batare da ta bari kuma hannunta ya tab'a penis din nasa ba.
"Hyyyyhhhhhhhhhimm".
Haka da tayi dinne kuma yasa shi, sauke wani irin nannauyan Ajiyar zuciya, tare da jan dogon numfashi, ya sake shigewa cikin jikinta.
Bayan ya d'aura hannunsa akan nata hannun.

Haka ya dinga danna hannunta akan marar nasa, yana me sauke Ajiyar zuciya akai akai, idanunsa dake arufe kuwa, ahankali suka soma matsawa,  saidai yanajin yanayinsa tamkar wani d'an maye.

Ahankali ya gyara kwanciyarsa, tare da juyawa ya kifa kansa akan cikinta, saidai kuma still har yanzu hannunta na kan mararsa, tana d'an mammatsa mishi.

Dr James ne ya kuma Kallon Dr Sulaiman da yayi jigum.

duk alamomin damuwa sun bayyana akan fuskarsa.

"Calm down Dr, zai samu sauki na fad'a ma, saidai maganin dana bashi yana sa bacci, amma daya farka komai zai dawo normal, saidai  amma kada yayi wasa da maganin, ya zamana yana sha kullum kuma akan lokaci."

Dr James din ya fadi haka yana me mik'awa, Dr Sulaiman magungunan Rayyern din.

K'arb'an maganin Dr. Sulaiman yayi cikin kuma nuna godiyarsu yace.

“Dan Allah Rayyern kana kulawa da kanka, kada kana yawan wasa da magungunan da aka baka, yanzu irin yanda ciwon nan naka ya tashi, inda ace babu Jannart akusa dakai da yaya kake ganin abun zai kasance? Dan Allah kana kulawa da kanka kaji Rayyern.”

Abban ya fadi haka cikin tausasawa.

Rayyern din kuwa jin abunda Abban ya fad'ane ya sashi sake lumshe idanunsa.
Yayinda acikin zuciyarsa yake maimaita sunan Jannart.

Jannart dake tsaye kuwa Ganin yanda ya lumshe idanunsa, batare kuma da ya saka kaya ajikinsa bane, yasa ta d'an kalli saman chest d'insa, inda kwantattun gargasa suka k'awata wajen.

D’an d’auke idanunta daga kallonsa tayi, kana ahankali cikin tafiyarta na nutsuwa ta juya ta nufi hanyar fita daga d’akin.

Jin takun tafiyarta ne kuma yasa Rayyern din bud’e idanunsa ya sauk’esu akan bayanta. Yanayin yanda hips dinta ke motsawa ya kalla, lokaci daya kuma yayi saurin d’auke idanunsa, saboda yanda shape din hips din nata ya bayyana sosai, kasancewar kayan da ta saka yabi jikinta.

Abba kuwa jin Rayyern din yayi shiru ne, yasa shi katse wayar ta hanyar cewa, zai kirasa anjima.

Rayyern kuwa dama hakan yakeso, saboda har yanzu bashi da wani karfin yin magana.

Ahankali ya sunkuyo tare da d’aukan kayan da Jannart din ta ajiye masa.
T-shirt ne da kuma dogon wando irin mai yawan aljihun nan.
Ahankali ya zura wandon ajikinsa, bayan ya saka t-shirt dinne kuma, ya d’an saka hannayensa duka biyu ya d’afa bango.
Saboda wani irin jiri da yakeji, gaba d’aya kwata kwata jikinsa babu k’wari.

Bayan ya d’an huta ne kuma ya soma sauk’e numfashi akai-akai, tare da hawa kan sallayan da Jannart din ta shumfud’a masa ya tada Sallah.

Ab’angaren Jannart kuwa tana fita daga d’akin Rayyern din, kaitsaye d’akinta ta wuce, kayan dake jikinta ta rage, cikin d’an kuzarin da take dashi kuma ta shige bathroom dan had’awa kanta ruwan wanka.

Sanin da tayi kuma cewar gari  ya soma haske ne, yasa bata wani b’ata lokaci awajen wankan ba ta fito.

Wani d’an k’aramin towel ta d’auka, ta tsane jikinta, tare da shafa body lotion ajikin nata, kana ta fesa sassanyan turarenta mai dadin kamshi, dangane da kwalliya kuwa powder kawai ta shafa akan fuskarta, sai kuma lipsgloss mai d’an shek’i.

Ahankali ta k’arasa wajen trolley dinta, tare da bud’ewa ta zaro wani had’add’en doguwar rigar engilsh wears, sai kuma hulan sanyi irin wanda ta saba sawa.

Koda ta zura rigar ajikinta d’as tayi mata, saidai duk da cewar rigar bata da tsawo sosai, amma tayi mata kyau ajiki,  hulan ta saka akanta tare da d’aukan hijab mai girma ta saka.

Bayan ta shumfud’a sallayane kuma ta tada Sallah.

Adai-dai lokacin kuma Rayyern ke idar da nashi sallan, bayan ya d’anyi addu’o’i da azkhar ne kuma, ya gyara zamansa akan sallayan tare da maida kansa, ya jingina da jikin drawer.

Idanunsa ya d’an lumshe ahankali, acikin zuciyarsa kuwa yana me tunanin maganganun da Abba ya fad’a masa, har zuwa yanzun kuwa moment din daren jiyan ya kasa fita daga cikin tunaninsa, domin aduk sanda ya tuno da sautin kukanta, sai yaji tsikar jikinsa na tashi, zuciyarsa kuwa haka zata shiga bugawa da sauri.

Ga kuma wani irin shegen kasala da yakeji, musamman akan abunda tayi masa d’azun, har yanzu jin marar tasa yake wani iri, Yayinda penis d’insa ke maaifar harbawa, tamkar Wacce take fitar da numfashi wanda hakan ya kasance mishi bakon yanayin da bai san dashi ba idonshi ya lumshe sabida duk sanda ya tuna sai yaji wannan harbawar.

Ahankali Jannart din ta mik’e tsaye, bayan ta idar da sallah tare da sa hannu ta zare hijab din dake jikinta, baby pink jacket ta d’aura akan kayan nata, kana  kaitsaye ta fice daga d’akin, tana me nanata fad’ar.
“Hasbiyallahu la’ila ha illahuwa alaihi tawakkaltu wa huwa rabbul arshil azim.”

Koda ta fito falo ledodin abincin da Dr.Sulaiman ya kawo mata ta bud’e, tare da zaro takeways din ta soma bubbudewa, Ganin duka abincin babu wanda ya b’aci ne, yasa ta d’aukan ledodin ta nufi kitchine.

Acikin plate ta juye chicken pepper onin sauce, da kuma saurce na liver sai kuma pancake, wanda aka yi masa gashi na musamman.

Warming abincin tayi bayan ta kammala ne kuma ta had’a musu coffee,

Acikin wani d’an tray ta saka musu abincin, kaitsaye ta nufi d’akin Rayyern din.

Ahankali ta tura kofar d’akin ta shiga, bakinta d’auke da sallama.

Jin motsin shigowarta ne kuma yasa, Rayyern din bud’e idanunsa, Ahankali kuma ya d’ago kansa ya kalleta.

Kyakkyawan shigan da tayi da kuma fuskarta ya zubawa idanu, wanda kuma tun kafun ta k’araso k’amshinta ya riga daya cika masa hanci.

Jannart kuwa cikin nutsuwa ta k’araso inda yake zaunen, batare da ta lura da irin Kallon da yakeyi mata ba.

Ahankali ta d’an durk’usa ta ajiye tray din agabansa, kana itama ta zauna tare da tank’washe k’afafunta,  sai alokacinne kuma ta d’ago idanunta ta kalleshi.

Karab kuwa idanunsu suka had’e acikin na juna, saboda har yanzu Rayyern din kallonta yakeyi.

“Ina kwana.”
Ta fad’a tana meyin k’asa da Idanunta.

“Lafiya.”
Ya amsa mata asanyaye tare kuma da janye idanunsa daga kallonta.

Itakuwa Jin alamun ya daina kallonta ne, yasa ta d’an gyara zamanta, tare da d’agowa ta kalleshi, tray din abincin ta sake turowa gabansa, kana cikin d’an yin k’asa da murya tace.

“Naan ga abinci kaci sai kasha magani.”

Bud’add’un idanunsa ya lumshe, tare da fesar da numfashi ahankali, saboda Jin yanda sautin muryarta ke fita, yasa duk yaji tsikar jikinsa ya tashi.

“Nakoshi.”
Ya fad’a ta hanyar motsa y’an k’ananan lips d’insa.

Jin hakan ne kuma yasa Jannart din d’agowa, ta kallesa da sauri, lokaci d’aya kuma ta kwab’e fuska.

“Please Naan kaci abincin please.”

ta fad’i hakan tana me langwab’ar da kanta gefe.

Lips d’insa ya dan cije saboda, yanda yaji tayi maganan tamkar Wacce take tsokalo wani abu daga sashi na jikinsa, akaro na farko kenan da yaji sautin muryarta na neman zautar dashi, abunda bai tab’aji ba arayuwarsa.

“Banajin yunwa.”
Ya sake fad’a atak’aice saboda bashi da wani k’warin jiki.

“Please ko coffee kasha.”
Jannart din ta fad’i haka cikin tausasawa.

Jin hakan da yayi dinne kuma yasa shi, d’an ya motsa fuska, tare da mik’a mata hannunsa alaman ta bashi cofin coffee din.

Da sauri kuwa ta mik’a masa kofin, Ganin da tayi ya soma shan coffee din ne kuma ya sata tashi, Anutse ta cigaba da tattare masa d’akin, bayan ta kammala ne kuma ta wuce falo, magungunansa ta d’auko tare da dawowa cikin d’aki’n.

Kallon yanda yake sipping coffe din ahankali tayi, yanayin yanda bakinsa ke d’an motsawa ne, yasa ta jin wani iri ajikinta.

Ahankali ta k'araso inda yake zaunen.
Zama tayi agefensa tare da d'ago Kanta ta kalleshi.

"Naan."
Takira sunanshi da wata irin unique voice, dinta Wacce tasa duk wani gargasan jikinsa mikewa.

Idanunsa ya kuma lumshewa, tare da Dan motsa bakinsa saidai bai iya amsa mata ba duk da zuwa yanzu ya gama fahimtar sunan data raɗa masa kenan (Naan) ya kuwa gane ƙarshen sunansa ta ƙawata ta bashi kekkyawan lafazi.

Ita kuwa Jannart dama  bata damu daya amsa mata ba, plate din abincin ta d'auko tasa akan cinyarta, cikin dan tausasawa hadi da  shagwab'a tace.

"Please Naan kaci abinci, ko kad'annne, kaga babu kyau mutum yasha magani batare dayasa komai acikinsa ba, coffee bazai rik'e ka ba, please Hamma Nanu karkace a'a."

Ta k'are maganar tana me Kallon fuskarsa, tare kuma da karyar da wuyanta gefe.

Akasalance ya bud'e idanunsa ya kalleta, Ganin irin Kallon da yakeyi mata dinne kuma ya sata mik'a masa plate din.
Babu musu kuwa ya karb'a, saidai bawai Dan yanajin zai iya cin abincin ba, pancake d'aya ya d'auka yasa abakinsa, tare da soma taunawa Ahankali.
Idanu Jannart din ta zuba masa, domin daga Ganin yanda yake tauna abincin bayajin dadin bakinsa.

Amma duk da hakan taji dadi daya karb'a yaci, saboda magananin zaifi saurin yi masa aiki.

Lomansa biyu kacal ya zare hannunsa, tare da daukan tissue ya goge hannun sa.
Akasalance ya d'ago oily eyes d'insa ya kalleta.

"Jannah Nak'oshi."
Ya fad'a yana me sake gyara zamansa.

Murmushi tayi tare dasa hannu ta karbi plate din, magungunansa dake hannunta ta b'are hade da daukan goran ruwa ta mik'a masa.
Babu musu kuwa ya karb'a yasha.

"Muje ka kwanta."
Ta fad'a tana me mik'ewa tsaye.

Tare da mik'a masa hannunta alaman ya kama.

D'an Kallon hannun nata yayi, kamar bazai kama ba kuma sai ya cije labbansa, tare dasa

hannun nasa acikin nata, Ahankali ya Mike tsaye bisa taimakonta.

Ganin ya tsaya ne kuma ya sashi zare hannunsa acikin nata, tare da d'an matsawa ya kwanta akan gado.

Kusan Atare suka sauke sassanyar Ajiyar zuciya, shida Jannart din, saidai kuma kowannensu da manufar sauke tasa Ajiyar zuciya.

Fararen tafin k'afansa ta zubawa ido, Yayinda shikuwa ya maida nasa idanun ya lumshe.

Dai-dai lokacin kuwa kunnuwanta suka soma jiye mata knocking kofar falon da akeyi.

D'an kallonsa tayi ganin ya rufe idanunsa ne kuma yasa kaitsaye ta nufi falon.

Ahankali ta daura hannunta akan handle din kofar tare da budewa.

Dr. Sulaiman da kuma su Dr. Sadiq ne tsaye, abakin kofar shigowa falon, ganinsu da tayi dinne kuma, ya saka ta sakin murmushi, kana cikin sakin fuska tace.

“Bismillah ku iso sannnunku da zuwa.”

“Yauwa Jannart.”
Dr. Sulaiman ya amsa mata shima fuskarsa d'auke da murmushi.
tare kuma da yiwa sauran Doctors din jagora, suka karasa shiga cikin falon.

Anan cikin falon suka zazzauna.
Yayinda Jannart kuwa Kai tsaye kitchine ta wuce, inda ta kawo musu ruwa da drinks.

Amutumce suka gaisa da sauran Doctors din, bayan sun gaisa dinne kuma Dr. Sulaiman ya kalli Jannart din, Cikin kulawa yace.

“Ya mai jikin, Ina fatan babu wata sabuwar matsala da ta kunno ko.”

D'an murmushi tayi tare dasa hannu, ta gyara zaman jacket din dake jikinta, murya asake tace.

“Jikinsa Alhamdulillah, tun jiya daya sha maganin dai ciwon bai sake tashi ba.”

Kai Dr Sulaiman ya jinjina, cike kuma da samun gamsuwa yace.

“Masha Allah ai haka akeso, amma daren jiyan ya samu bacci kuwa?”

“Eh ya samu, yanzu ma yana kwance inaga baccin zaiyi, but bari nayi mishi magana.”

Ta fad'a tana kokarin mikewa tsaye.
Saurin dakatar da ita Dr. Sadiq yayi, ta hanyar cewa.

"No basai kin taso sa ba, zamu dawo anjima da yamma nasan zuwa lokacin ya sake samun k'arfin jikinsa, ga wannan mu zamu wuce wajen aiki."

Ya k'are maganan yana me ajiye wata babban ledan restaurant dake hannunsa.

Ganin hakanne kuma yasa sauran Doctors dinma duk suka mik'e.

"Mungode sosai."
Jannart din ta fad'a, tare da taka musu har bakin kofar fita daga falon.

Saida taga tafiyarsu kuma kafun ta dawo ta zauna, ledan da Dr. Sadiq din ya kawo ta bud'e, tare da ciro takeway daya na African dishes ta soma ci.

Bata wani ci sosai ba kuwa ta ture abincin gefe, tare da daukan bottle water tasha ruwa, sauran ragowan abincin ta Kai kitchine.

Kana ta dawo kaitsaye ta wuce d'akinsa.

Ahankali ta murd'a handle din k'ofar ta shiga bakinta d'auke da siririyar sallama.

Yana nan kwance kamar yanda ta barshi, Yayinda kuma har yanzu idanuwansa ke lumshe.

Ahankali ta k'araso jikin gadon, tare da matsowa inda yake kwance.

Kyakkyawar fuskarsa ta zubawa ido, bata ko kyaftawa, daga gefe guda kuwa anutse kunnuwanta, ke jiye mata sautin fitar numfashinsa.

"Yayi bacci."
Ta fad'a abayyane cikin kuma sanyin murya, yanda tasan bazai jiyota ba.

Zama tayi ad'an gefen gadon,
tare da d'aukan hannunta na dama, Ahankali ta kife tafin hannun nata akan goshinsa.

Wani irin b'oyayyar ajiyar zuciya ya sauke, tare kuma da d'an motsa hannunsa batare da ya bari taga hakan ba.
Taushi da kuma laushin hannun nata, hadi da daddad'an kamshin turarenta, shiyasa shi jin wani iri acikin jikinsa.

Itakuwa Jannart sanin da tayi cewar bacci yakeyi, shiyasa ta sauko da hannunta ahankali zuwa kan lallausan sajensa, wanda daga jiya zuwa yau take matukar jin dadin tab'ashi.

Ahankali ta d’an shafa sajen nasa, tare da lumshe Idanunta cikin sanyin murya tace.

“I pray wish you quick recovery Naan, soon zaka samu sauki Insha Allah, then babu wata cuta da take d’aurewa aduniya, you’ll be okay Insha Allah Naanu.”

Ta k’are maganan tana me gangaro da hannunta, kan wuyansa, tare da tura yatsun hannunta acikin wuyan rigar sa, wanda kuma hakanne ya bata daman jiyo sautin bugun zuciyarsa.

Idanunta ta lumshe ahankali, hade da sake saukar da hannunta k’asa, har ta iso kan mararsa.

Lallausan tafin hannunta ta kife akan mararsa, cikin kuma tsananin tausayinsa da takeji, murya araunace tace.

“I’m sorry Naan ai nasan zakaji sauki, maranka zai daina daurewa haka ma cikinka zai daina ciwo, so Sorry.”

Ta fad’i hakan ashagwab’e, tare da soma d’an shafa masa saman marar, wanda kuma ta nayin hakanne, da tunanin bacci yakeyi.

Shikuwa Rayyern saukan dumin tafin hannunta akan D d’insa, ba k’aramin tayar masa da tsikar jiki yayi ba, saboda yakanji hakanne amatsayin wani salo na musamman, sannan yakanji kansa acikin wani irin yanayi a duniya ta musamman.

Idanunsa ya d’an rumtse da k’arfi, tare da fusgar numfashin da ke neman k’wace masa.

Allah yasani bai tab’ajin irin abubuwan da yakeji ayanzun ba.
Musamman Idan hannunta na yawo asaman marar tasa, yakanji duk wasu jijiyoyi dake jikinsa sun motsa, haka ma Rayyern d’insa da yakejin na harbawa.

“Yah Salam.”
Ya fad’i haka acikin zuciyarsa, Yayinda abayayyane kuwa ya fesar da wani irin zazzafan numfashin da yasa Jannart din ta d’ago ta kalleshi.

“Naan.”
Ta d’an kira sunansa ahankali, tare kuma da zare hannunta dake kan marar tasa.

Duk da cewar ya jiya amma sai yayi shiru bai amsa taba.

Itakuwa Jannart shirun da yayi dinne, yasa ta tashi daga kan gadon.
Ahankali taja blanket ta rufe masa jikinsa.

Kana ita kuma ta koma k’asa nan kan carpet ta zauna.

Rayyern kuwa jin da yayi Jannart din tabar kusa da shi ne, yasa shi sauke Ajiyar zuciya, tare da d'an gyara kwanciyarsa, ta yanda ba zata sake samun daman tab'a saman marar tasa ba, domin yayi imani Idan taci gaba dayi masa hakan, zata iya d'aid'aita tunaninsa da nitsuwarsa dama rayuwarsa gaba ɗaya ya tabbata yana gab da sakin kuka idan har zatake sashi cikin wannan yanayin.

Jannart kuwa Koda ta zauna akan sofan, wayarta ta d'auka tare da soma latsawa.

Tana nan zaune kuma wayarsa ta soma k'ara, da sauri ta jawo wayar tare da saka ta a silent saboda, batason karan wayar ya tashe sa daga baccin da yakeyi.

Wani kiran ne ya kuma shigowa, cikin wayar tasa Ganin da Tayi sunan Riyyam na yawo, akan screen din wayarne kuma, yasa ta picking call din, tare da kara wayar akan kunnenta.

Daga can b'angaren Riyyam kuwa jin anyi picking call dinne, ya sashi gyara zama tare da cewa.

"Hamma Rayyern."

Ajiyar zuciya Jannart din ta d'an sauk'e, kana murya ad'an sanyaye tace.

"Riyyam."

"Na'am Aunty Jannart ya jikin Hamma Rayyern, yanzu Yah Ramadan yake fadamin wai jikin Hamma Rayyern ya tashi sosai jiya, Dan Allah ina yake ya jikin nasa kuma, Ina fatan dai ya samu sauki."

Riyyam'n yayi mata duka tambayoyin, alokaci daya kuma cikin dan yanayi na rudewa.

Jin yanayin Riyyam dinne kuma yasa, Jannart sakin ranta, cikin son kwantar masa da hankali tace.

"Jikinsa da sauki Riyyam, yanzu haka ma ya samu bacci, saidai jiya na tsorata sosai Riyyam, naji tsoro kada ya mutu barni a wannan duniya da ban san kowaba."

Ta fad'i hakan hawaye na cika mata idanu, lokaci daya kuma duk wani raunin ta ya bayyana.

Riyyam kuwa jin abunda ta fad'ane yasa jikinsa, yin sanyi asanyaye yace.

"Allah ya k'ara sauki, duk hankalinmu ya tashi ni da su Mammy, amma yanzu da naji ya samu relief Alhamdulillah, ga Mammy nan zaku gaisa."

Ya kare maganan yana mikawa Mammy dake gefensa wayan.

“Jannart”
Mammy ta kira sunan Jannart din tana kara wayar akan kunnenta.

“Na’am Mammy Ina kwana.”
Jannart ta amsa mata cikin ladabi da matukar girmamawa.

“Lapia kalau Jannart ya mai jikin?”
Mammy ta tambaya cikin dan yanayin damuwa.

“Alhamdulillah jiki da sauki sosai, yanzu ma bacci yakeyi.”

“Allah ya kara sauki yasa kaffarane, ya kuma yaye masa wannan ciwon yasa kiyi farar jinya.”

Mammy ta fad’i hakan da iyaka gaskiyar dake zuciyarta.

Jannart kuwa cikin dan jin dadi tace.

“Ameen Mammy mungode sosai da kulawa, Ina Zaytoon.”

“Ganinan Aunty Jannart am ya jikin Hammana?”

Cewar Zaytoon da ta cafe wayar da sauri.

D’an murmushi Jannart tayi, kana murya asake tace.

“Jikinsa da sauki zaytoon ya school?”

“Alhamdulillah My beloved please ki kulamin da Hamma kinji, Allah ya kara masa lafiya .”

“Ameen.”
Jannart ta amsa tana me fadada Murmushin dake kan fuskarta.

Riyyam  kuwa dake gefen Zaytoon k’wace wayar yayi, tare da maidashi kunnensa, cikin dan yanayin sigar tsokana yace.

“Gaskiya Aunty Jannart jiya kin tayar mana da hankali, duk kinsa muntsorata, Koda mukayi waya da Hamma Ramadan dazu, saida yayi ta miki dariya saboda yace, jiyan kuka kikeyi harda shid’ewa, irin bakyason mijinki ya mutu nan why?”.

Yanayin yanda ya kare maganan cike da tsokana ne, kuma yasa Jannart din shagwabe fuska, Cikin yanayin tura baki tace.

“Wallahi Riyyam banaso.”

Dariya gaba d’aya suka kwashe dashi, musamman Riyyam da Zaytoon din, harma da Mammy saidai ita nata kasa-kasa takeyi.

Jin yanda suke dariya ne kuma yasa Jannart din turo baki, ashagwab’e tace.

“Mammy ina kinajin su Riyyam ko.”

Da sauri Mammy ta kwace wayan, tare da cewa.

“Rabu dasu abunki, jeki kula da mijinki gaba dayansu duk rashin aikinyi ne ke damunsu, Allah ya miki albarka Jannart, kamar kuma yanda kika kula da Rayyern, kema Allah ya kula dake.”

“Ameen Summa Ameen.”
Jannart din ta amsa tana murmushi, tare da sunkuyar da kanta k’asa.

Mammy kuwa zuciyarta cike da nutsuwa, ta kashe wayan

Tare da watsawa su Riyyam din hararan wasa.

Cikin sakin fuska tace.

“Yarinya tana kulawa da mijinta zaku dameta, idan tayi kuka ai soyayyace ta kawo hakan, da bata sonshi bazatayi kuka akanshi ba.”

Murmushi Riyyam nsra yayi, cikin matsanancin farincikin da yakejin kansa aciki yace.

“Mammy ba auren soyayya fa sukayi ba, Hamma Rayyern bayaso itama haka, amma yanzu naga kaman rayuwar tasu tana ta juyawa, game din na canjawa, I cant wait ranan da Hamma Rayyern da Aunty Jannart zasu so juna.”

Murmushi Mammy tayi, tare da gigirza kanta, batare da tace musu komai ba kuma taci gaba da sabgoginta.

Jannart kuwa ajiye wayar tasa tayi, tare da maida kanta ta jingina da jikin gadon, ahankali take sauk’e numfashi, Yayinda zuciyarta ke cike da tunani kala daban daban.

Rayyern dake kwance kuwa, duk wani hiran dasu Jannart din keyi yana jinsu, harta k’are wayan kuwa bacci bai d’aukesa ba.

Ahankali yake sauke ajiyar zuciya, Yayinda kunnuwansa kuwa ke jiye masa sautin fitan numfashinta, kasancewar ta kashe AC’n dake d’akin, ko ina kuma yayi shiru shi yasa ko wanni

sautin motsinta, akan  kunnuwansa suke sauka.

Yana nan ahaka har bacci b'arawo yazo ya d'aukeshi.

Jannart dake zaune akan carpet kuwa, game ta d'an soma yi awayarta,  tana cikin game din kuma itama bacci ya d'auke ta, inda tayi pillow da hannunta na dama.

1:30 pm.

Ahankali ta bud'e Idanunta, wanda tashin farko suka sauk'a akan agogon dake cikin dakin.

Da sauri ta d'an tashi zaune, tare da juyawa ta Kai dubanta kan gadon.

Idanunta ta sauke akan Rayyern, da har yanzu bacci yake, Yayinda ya sake nad'e jikinsa da blanket.

Yunk'urawa tayi Ahankali ta tashi, gudun kada motsinta ya tashe sa ne kuma, yasa cikin sand'a take tafiya, harta k'arasa bakin kofar fita, ahankali ta bud'e kofar dakin ta fice.

Tana fita kuwa ya bud'e idanunsa, saboda kusan Atare suka farka, kawai dai shi yayi jinkirin tashi ne.

K'ofar d'akin nasa yabi da kallo, kana ahankali ya zuro da kafafunsa k'asa, tare da tashi daga kan gadon ya tsaya akan k'afafunsa.

Ajiyar zuciya ya dan sauke, saboda kwarin da yaji ajikinsa, ba kamar dazu ba da ko tsayuwa yayi sai yaji jiri na neman kada shi.

Direct bathroom ya shiga ya d'auro alwalan sallan azahar, bayan ya fito ne kuma ya shimfud'a sallaya tare da tada Sallah.

Acan gefen Jannart kuwa Koda tabar d'akin nasa, nata d'akin ta wuce, tare dayin alwala tazo tayi sallah.

Bayan ta idar da sallan ne kuma, ta tashi ta fice daga d'akin, direct dakinsa ta nufa Dan ta dashi yayi sallah.

Anutse ta tura kofar dakin ta shiga bakinta d'auke da sallama.

Bayan ta maida kofar dakin ta rufe ne, kuma ta juyo tare da kallon kan gadon.

Ganin gadon babu kowa ne kuma yasa ta, zaro Idanunta tare da k'arasa shigowa cikin dakin.

Karab kuwa Idanunta suka sauk'a akansa, Inda yake kwance akan sallaya, ya lumshe kyawawan idanunsa.

Ajiyar zuciya ta d'an sauk'e tare da k'arasowa inda yake kwancen.
Batare da tunanin komai ba ta zauna agefensa, tare da  sauk'e idanunta akan lafaffen cikinsa.

"Naan."

Takira sunansa in a silent voice din daya sashi bud'e idanunsa ahankali ya watsa mata su a narke.

Fuskarta tad'an shagwabe, cikin kuma son lallab'asa tace.

"Please Naan na kawo maka abinci?."

Yanayin yanda ta kare maganan cikin sakalci ne, yasa Rayyern din zubawa lips dinta idanu.

Yana mejin wani abu nayi masa yawo acikin jikinsa.

"Naan. "
Jannart din ta sake kiran sunansa, da murya mai kamada rad'a.

"Ummmmmmmmm."

Ya amsa mata da thesame irin muryar da ta kirasa.

"Na kawo maka abinci please."

Ta sake maimaita tambayar.

Kansa kawai ya iya gyad'a mata alaman.
"Eh."
Saboda zuwanta kusa dashi yanzun, duk ya sashi jin mutuwar jiki da kasala.

Jannart kuwa Ganin ya bukaci abincin ne, ya sakata sakin murmushi tare da tashi ta fice daga cikin dakin.

Kaitsaye kitchine ta wuce, abincin da Dr. Sulaiman ya kawo musu d'azu, ta zuba a plate, bayan ta d'auko goran ruwa ne kuma ta dawo dakin.

Duk da cewar yana kwance amma agabansa, ta ajiye plate din,  tare da kallonsa Cikin kulawa tace.

“Naan tashi kaci, please koba mai yawa ba kaci kadan kaji.”

Tayi maganan tana me zama akusa da kafafunsa.

Shikuwa Rayyern  tashi yayi ya zauna.
Tare da jawo plate din abincin kasalance ya soma ci.

Ganin yafara cin abincinne kuma yasa, Jannart daukar wayarta ta soma dannawa.

Ahankali yake tauna abincin abakinsa, yana me Kallon y’an yatsun hannunta dake kan wayarta, ahaka har ya d’anji ya koshi, duk da bai ci abincin da yawa ba, amma haka yaji ya koshi, ruwa yasha tare da sake maida bayansa ya jingina da jikin drawer.

Jannart kuwa fahimtar ya koshi ne yasa ta tartare wajen, bayan takai plate din kitchine ne kuma ta dawo dakin.

Again kusa dashi ta sake dawowa ta zauna, tare da d’an mik’e k’afafunta.

Wanda hakanne kuma ya bashi daman, sauke idanunsa akan legs dinta.
Kallon legs din nata yake Ahankali har ya gangaro zuwa kan lafaffen ciki da kuma kirjinta.

Ahankali ya saki wani Murmushi ta gefen bakinsa, wanda babu wanda zaisan yayi sai shid’in.

“Uhummm wai gadina takeyi kenan?.”

Ya fad’i haka acikin zuciyarsa, tare da Kallon fuskarta.

Itakuwa Jannart hankalin ta duk ya tafi, akan game din da yakeyi.
Kwata kwata tama manta cewar a gabansa take,  Ahankali take latsa waya tata, tare dasa teeth dinta tana d’an taune lips dinta.

Lips din nata yake kallo yanajin tsikar jikinsa na tashi sosai, batare kuma daya san dalilin hakan ba.

Ahankali ya lumshe idanunsa tare da hade hannayensa ya rungume su akirjinsa.

Ahaka suka kasance har tsawon awa d’aya, kafun wani dan guntun bacci ya kuma daukar Rayyern din, saboda maganin daya sha bai gama sake shi ba.

Jannart dake gefensa kuwa game take tayi, time to time amma takan d’ago Kai ta kalleshi.

5:30 pm

Fitowarta kenan daga cikin bedroom dinta, Inda ta sanja shigar dake jikinta, zuwa riga da wando na Pallazo, sai kuma wani babban jacket mai kaman suit da ta d'aura akan kayan.

Tayi kyau sosai sai faman baza kamshi takeyi.

Isowar ta cikin falon kuwa yayi dai-dai da knocking din kofar falon da aka somayi.

Da d'an sassarfa ta k'arasa ta bud'e kofar, ganin su Dr Sulaiman ne kuma yasa ta fad'ad'a fari'arta, had'e  dayi musu iso suka k'araso cikin falon.

Bayan sun zauna ne kuma ta wuce dakin Rayyern din, dan sanar masa da zuwan su Dr. Sulaiman din.

Koda ta shiga akwance ta sameshi, Yayinda shima yayi wanka ya kuma sauya shigar dake jikinsa.

“Naan.”

Takira sunansa ahankali.

Juyawa yayi ya kalleta, saidai bai amsa taba, saima tsaida idanunsa da yayi akan shigar dake jikinta, wanda yayi mata kyau sosai.

“Su Dr Sulaiman sunzo.”
Ta fad'a itama tana me kallonsa.

Idanunsa ya d'an lumshe, kana ahankali ya yunkura ya tashi, cikin dan kuzarin da yake dashi ya Mike tsaye.

Da tafiyarsa wacce yakeyi ahankali, ya nufi falon, Yayinda ita kuwa Jannart ke biye dashi abaya.

Ahankali take nazartar sa, saboda ta fahimci har yanzu bashi da wani isashshen karfi ajikinsa.

Fitowarsu Cikin falonne ne kuma yasa, su Dr. Sulaiman din kallonsa, lokaci daya duk ya sanja, yar rama ta bayyana ajikinsa, saidai kuma ya kara haske.

K'arasowa cikin falon yayi ya zauna, tare da mikawa su Dr. Sulaiman din hannu suka gaisa.

“Dr. Ya jiki?”
Dr. Sadiq ya tambaya.

Kansa ya gyad’a alaman da sauki, saboda baya wani son magana sosai.

Dukansu ya jiki sukayi masa, inda yayi kokarin amsa musu, bayan sun gaisa dinne kuma, ya kalli Dr. Sulaiman tare da tambayarsa, yau me akayi awajen meeting.

Ajiyar zuciya Dr Sulaiman ya sauke, tare da Dan gyara zama yace.

“Test mukayi akan surgery, amma dai next week zamuyi original test akan dashen zuciya, then na fad’awa Sauran manyan Doctors din, duk abunda mukayi kuma sun tura ma ta email dinka, muna saran Allah ya baka lafiya before next week.”

“Ameen.”
Ya fada yana me jinjina kansa, saboda shi kansa zaizo ace baiyi missing ko daya na daga cikin abunda ya kawo sa ba,  musamman dashen zuciyan.

Haka dai suka Dan tab’a hira, Ganin lokacin sallan magriba ya kusa ne kuma yasa, su Dr. Sulaiman din tashi suka tafi.

Tun kafun su tafin kuwa Jannart ta koma d’akinta.

Shikuwa bathroom ya wuce ya d’auro alwala, tare da fitowa ya tada sallah, saboda bazai tab’a iya zuwa masallaci ba, dama ace masallacin na kusa ne.

Bayan ya idar da sallan ne kuma Yana nan zaune akan sallaya, Wayarsa ta soma k’ara, Ahankali ya kalli wayar ganin sunan Barrister Kabeer na yawo akan screen din wayar ne, kuma ya sashi picking call din, bakinsa d’auke da sallama ya kara wayar akan kunnensa.

Barrister Kabir dake kan layi kuwa, Jin an d’aga wayarne yasa shi, amsa sallaman cikin sakin fuska yace.

“Rayyern barka da dare ya jikin naka?”

“Alhamdulillah Barrister jikina yayi sauki, ya fama da Jama’a.”

Rayyern din ya amsawa Abba Kabir din atausashe.

Dai-dai lokacin kuma Jannart ta bud’e kofar d’akin ta shigo, hannunta rike da wani cup, wanda ta zuba zuma aciki.

D’ago idanunsa yayi ya kalleta.

Yayinda daga can b’angaren kuwa Barrister Kabir cewa yayi.

“Masha Allah Allah ya kara sauki, ya kumasa zakkan jikine, d’azu mukayi waya da Abbanku shine yake shaidamin rashin lafiyar taka, Allah ya kara afuwa.”

“Ameen Summa Ameen Barrister nagode.”

Still ya kuma fada atausashe.

“Ba komai Rayyern ka gaishe min da Jannart.”
Barrister Kabir din ya fad’i haka da niyar katse kiran.

Kai Rayyern din ya jinjina, batare kuma daya bari Abba Kabir din ya katse kiran ba yace.

“Ga tanan ma bari na bata ku gaisa.”

Yana fad’an haka ya mik’awa Jannart, da ta zauna agefensa wayar.

Saurin d’agowa tayi ta kalleshi, Ganin irin Kallon da takeyi masa dinne kuma yasa shi, kawar da kansa gefe, cikin yin k’asa da murya yace.

“Abban ki ne.”

Da sauri ta karb’i wayan tare da karawa akunnenta, cikin jin dadi da samun nutsuwar zuciya tace.

“Abbana.”

Murmushi Barrister Kabir  din yayi had’e da cewa.

“Na’am Jannart dina, ya kike ya mai jiki?”

Idanunta ta d’an lumshe cikin jin dadi tace.
“Alhamdulillah Abba jikinsa da sauki sosai, kaifa Abba ya kake yasu Aunty Dijat da Momy da Daddy na.”

Ta k’are maganan cikin raunin murya, saboda tunawa da Dadynta da tayi, wanda akullum kewarsa dana gidan nasu ke damunta.

Jin rauni acikin muryar Jannart dinne kuma, yasa Abba Kabir jajircewa, cikin son bata karfin guiwa yace.

“Duk Suna lapia Jannart, Dadynki ma yana lafiya haka su Momy da Abdull, kowa da kowa yana lafiya, kada kice zaki saka damuwa aranki kinji, ki kula kawai da mijinki saboda ayanzu, yafi kowa muhimmanci agareki, shine Garkuwanki, haka kuma shine Jagora akan komai na

rayuwarki.”

Idanunta da suka cika da k’walla ta d’an lumshe, murya asanyaye tace.

“To Abba nagode.”

“Yauwa Jannart Dan Allah ki kula da kanki kinji, kada ki bari damuwar wasu tayi tasiri acikin zuciyarki, domin su ba Lallai ya zamana kamar yanda kike jinsu aranki, haka suma sukejinki ba, duniya ce Jannart akwai abubuwa da yawa wanda baki sani ba, saboda haka kada kibar damuwa tayi tasiri acikin zuciyarki ta hanaki kula da mijinki wanda al'jannarki ke karkashin digadiginsa.”

Barrister Kabir din ya fada cike dason bata confidence.

Itakam kanta kawai ta jinjina, batare da ta fahimci maganganun Barrister Kabir din ba, wanda ya fad’a mata su adunk’ule.

Wanda kuma hatta Rayyern dake gefe, saida ya fahimci wani abu acikin kalaman, kasancewar wayan an sa call volume d’inta duka shiyasa, sometimes Idan kana waya, akeji Koda kuwa baka sata a ansakuwa ba.

Ahankali ta zare wayan daga kunnenta, tare da d’an zamewa ta kwantar da kanta ajikin hannun kujera.
Idanunta ta lumshe batare kuma da ta mik’a wa Rayyern din wayar ba.

Rayyern kuwa shima d’an mirginawa yayi, ya kwanta akan sallayan.

Wanda hakanne kuma ya bashi daman facing dinta, inda ya sauke idanunsa akan kirjinta, saboda yau d’inma haka take zaune, bata saka bra ba, shiyasa yake iya hango shatin nipples dinta, da suke tsaitsaye tamkar zasu tsone masa idanu.

Ganin ta bud’e Idanunta ne kuma yasashi, saurin kawar da kansa gefe.

Itakuwa Jannart ba tare da sanin ita yake kallo ba, ta tashi tsaye, direct gaban tv plasman dake cikin bedroom din ta nufa.

Bayan ta kunna tv’n ne kuma ta dawo ta zauna.
Tare da maida hankalinta ga tv’n, saboda wata tasha da taga suna haska indian film, me suna (Ashquie).

Anutse take Kallon film din, wanda take da yakinin cewar zai rage mata kewa.

Jin sautin film din ne kuma yasa, Rayyern ma juyawa ya kalli tv’n.

Almost 30mn suka d’auka kowannensu hankalinsa, nakan film din.

Dai-dai anfara wak’an Tumhiho ne kuma, Atare duk suka d’an lumshe idanunsu.
Saboda yanda amo da sautin wakan ya fara dukan zuk’atansu.
Musamman alokacin da stars din, suka samu keb’ancewa daga ruwan sama.
Kamar yanda suka lumshe idanun nasu atare, Atare suka kuma bud’ewa.

Ahankali Jannart ta d’an juya da niyar Kallon Rayyern din, karab kuwa idanunsu suka sauk’a acikin na juna.

Idanun nasa masu kalan bacci da suke a narke ya d’an lumshe, tare kuma da d’an turo bakinsa gaba, cikin yanayi mai kama da na shagwab’a cike da kasala yace.

“Meye kike wani kallona, ki kalli abunda kika saka mana.”

D’an juyawa tayi ta kalli tv,n saidai da sauri ta d’auke idanunta, saboda wani gani da idanun nata yayi mata,  inda Arjay da Arohi suka fad’a cikin wata duniya ta daban.

sake yin kasa da Idanunta tayi, akasalance kuma cikin yanayin shagwab’a, kamar yanda yayi mata tace.

“To ni ai bansan na kalleka ba, kuma ma ai dole ne na duba lafiyarka.”

Idanun nasa dake ci gaba da sanja launi ya lumshe tare dayin wani narkekken mik’an da yasa D dinsa mikewa sama, da wani irin yanayin dashi kansa baisan yana dashi ba yace.

“Why gadi na kikeyi ne?”

“Ummm dole ne ai, saboda haka nema nazo nan.
Tunda abinda ya kawoni k’asar ma kenan, can you imagine idan da ka suma jiya bana nan, you think me zai faru.”

Tayi maganan tana cije labb’anta, tare da karyar da wuyanta gefe.

Hakan da tayi dinne kuma ya sashi zuba mata ido, domin sai ya ganta like babies,  Yayinda daga cikin jikinsa kuwa shi kad’ai yasan me yakeji, akan kowanne shagwab’arta, to mimmik’ewan jijiyoyin jikinsa ne.

D’an d’ago Kanta tayi ta kalleshi, Ganin yanda ya kura mata idone kuma yasa ta, turo baki kamar yanda yayi mata d’azun tace.

“Nima me yasa kake kallona?”

Kansa ya d’an girgiza, lokaci daya kuma ya janye idanunsa daga kallonta, tare da maidasu kan tv, yana kallon yanda taurarin film din ke romancing juna, acikin blanket d’aya hakan yasa ya karajin wani irin azabebben kasala mai narka jiki da zuciya idanunshi duk suka juye suka narke kamar d’an maye.

Murya can ƙasan maƙoshinsa yace.
“Na kalla ɗin, ai halal na gani don na biya sadaki”.
Yayi mgnar ta yadda yasan bazata jiba.

Ita kuwa Jannart kasa sake d’agowa ta kalli tv’n ma tayi, saboda abunda akeyi din ya wuce tunaninta da saninta.

Kofin zumanta ta d’auka tare da soma lasa ahankali, bata d’ago Kanta ba kuwa, har saida taji an wuce wak’an.

After 1hour.

“Zanyi wanka.”

Rayyern din ya fada ahankali batare kuma daya bude, fitinannun idanunsa dake lumshe ba, domin film din da ya gani yanzun duk yasa, mood d’insu na safiyar yau ya dawo masa sabo jinsa yakeyi tamkar ya hayewa babu.

Jin abunda ya fad’a d’inne kuma yasa Jannart, juyowa ta kalleshi, saidai kuma ganin ba ita yake kallo bane, yasa ta cewa.
“To.”
Ahankali ta tashi ta wuce bathroom d’insa.

Ruwan wanka mai d’an d’umi ta had’a masa, Koda ta fito kallonsa tayi tare da cewa.

“Na had’a maka ruwa a bathtub.”

Kansa ya jinjina hade da mikewa tsaye, da d’an kuzarin  daya rage masa din ya wuce toilet.

Itakuwa Jannart drawer’n sa ta bud’e, hade da ciro masa wasu kayan bacci masu taushi ta ajiye masa akan gado.

Ganin har zuwa lokacin bai fito bane, kuma yasa ta wuce nata d’akin, inda itama ta sake sabon wanka.

Rayyern kuwa Koda ya fito a wankan, Ganin bata cikin dakinne yasa shi zare towel din jikinsa kamar yadda ya yakeyi a lokuta da dama, dashi ya tsane ruwan jikinsa ka ya shirya kansa

anutse.

Bayan yasa kayanne kuma ya koma kan gado ya zauna.

Acan d’akin Jannart kuwa, shirya kanta tayi, cikin wani sleeping gown mai adon net, duk da yana da kauri, amma hakan bai hanashi yi mata yaro yaro ajiki ba.
Sosai rigar tayi mata k’yau, saidai ganin yanda breast dinta, ya bayyana karara ne yasa ta d’aura jacket akan rigar.

Duk tunaninta ayanzun ya tafi ne akan yanda zata kwana ad’akin Rayyern din, saboda batajin zata iya barinsa ya kwana shi kad’ai.

Kashe wutan dakin nata tayi, tare da jawo kofar dakin ta rufe, kaitsaye ta nufi d’aki nasa...!

*Albishirinku! Ma'aurata, GA GARKUWAR KU nan tafe muku da tsarabobi na musamman gareku ma'aurata daga cibiyar mgnin mata mai taken GARKUWAR MA'AURATA*

NI DAI AYSHA ALIYU GARKUWA.
Ina matukar mamakin wani irin lokaci da ya riske mu mai wahalallan fassara. Kullum dai magana daya ce, akan ma’aurata, fada, rashin jituwa, mutuwar aure, akan kuskure kalilan, rashin kula, rashin yi wa juna uziri. Toh wai duk me ya janyo hakan? Na zurfafa a tsananin tunani hakan ya tilasta min bincike mai tarin yawa wanda ya kai ni ga gano inda matsalar take? Shin yar’uwa ke macece amma kin san wacece mace ku? Kin san me ake kira mace kuwa? Mace ita ce matar da take zama iyali a wajan namiji ta zame masa bango, sanyin idaniyarsa, ta zame masa gata da farin cikin rayuwarsa ta zame masa ruwa abar kore ƙishinsa ta zame masa mayafi mai karesa daga gigitar kadaice, ta kuma dorar da mijinta kan turbar gaskiya, ta kashe masa jiki da salonta ta rikita shi da baiwa da ni’imar da Allah ya bata idan har ta san hanyar mayar da kanta sabuwa dal awajanta, wato kullun takasance masa tamkar amarya har ya kasa tantance daren amarcinsu da sauran dararen rakun rayuwar su.

Wannan ita ce mace. Ina da wata saukakkar hanyar da zaki zama abar so da kulawa da soyayya a wajan mijinki ta hanya mafi sauki, 09097853276 hanyar ita ce ki gwada amfani da kayana na gyara ki gani, ina mai tabbatar miki da in sha Allahu sai kin dara da murna sai kuma kin gode min. Kayana kaya ne da aka yi shi da zallan itacanmu na gado marasa illa a cikin jikin dan adam musamman mace, kaya ne da suke taimakawa (sex hormones 😍) dinki.
Misali kina kallon India😘, hollywood, Asian film🥰 kina ganin yanda mazansu ke nunawa matansu tsananin soyayya kamar su ba su kyautar ransu!?
Saboda me hakan? Saboda suna sadaukar da lokacinsu wajan gyara jikinsu da kayan da ke tsattsafo da ni’ima cike da tsukewa, kayan nan kuma ana yinsu ne zallar magungunan gargajiya wanda ba su da illa domin haɗine na ingantattun itatuwa da yayansu.
Ina baiwar Allahn da miji ke daure mata fuska babu hirar arziki?

Zo ki ji yar’uwa zan baki gumbata da zallar gari wanda aka yi su da nagartattun itacen da ke da matukar amfani a jikin mace. Gubar ciko, gumbar tsalle dole, gubar da ba'a baiwa mai kishiya, garin maɗi, garin mallaka, tsumin goron tula, tsumin tsartai, tsumin maratsi, pala-pala butar sirri, kwanon k’asaitacciyar mace, furar mata madadararta gareki Hajia takenta sha yanzu mgni yanzu, Ina mata masu fama da sanyi? Sanyin mara ki zo na hadaki da magani na na sanyi wanda yake wanke mara ya fitar da duk wata cuta da ke samun mazauni a wajan.
Ina da ciccibi mai kyau. Ina da hadin amare mai kyau wanda zai gyara yarinya ya kankaro mata kimarta akwai hadin mai jego wanda muke yinsa na asali inada kekkyawan Hadi maida tsohuwa yarinya.

Akwai daya bangaren wato *KAMSHI*
Kimarki gyaranki da kamshinki. Matan da suka gane suka san yanda za su kankaro da mutunci su ne masu amfani da kayan gyara da kuma sanyaya jikinsu da kamshi, ina da turaren wanka da na bandaki na daki na jiki da na kaya dana tsuguno kamshin turarena na dabam ne mai sanyaya zuciyar wanda ya shaka ina da kayan kamshi na amarya da na maijego da na uwargida da dukkan macen da take kokarin mayar da kanta mai daraja a idon kowa ta zamo sarauni a idon mijinta, akwai shu'umar humra, sayan na gari maida kuɗi gida, banda karanta yayin gyara Hajia.

Zaku iya samun kayyakina a duk garin da kike, zakiyi min mgn ta whatsApp number na 09097853276 domin yin zaɓinki, ko karin bayani, zaki tura kuɗin ta account na 0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU in mun gama mgna zan sa miki kaya a mota yazo duk garin da kike, in baki shirya saya yanzuba Please kada mu wahal da juna ki bari sai kin shirya kafin kiyi min mgn.

🤝🥰😘 Daga taku AYSHA ALIYU GARKUWA
*(GARKUWAR MA'AURATA)*

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:53 - 🥰🥰: Ahankali ta tura k’ofar d’akin ta shiga, bakinta d’auke da sallama.

Jin sallaman nata ne yasa Rayyern dake zaune akan gado, d’ago idanunsa ya kalleta.

Akaron farko kenan da yaji ya kasa d’auke idanunsa daga kallonta, musamman saboda yanda rigar jikin nata tayi mata kyau, tunda suke kuwa bai tab’a kallonta acikin irin shigar ba.

Ahankali ta k’arasa shigowa cikin d’akin, kasancewar kuma akwai k’arancin haske, acikin dakin shiyasa ta nufo inda yake Kai tsaye, Yayinda hannuwanta ke rik’e da sachet din magungunansa.

“Naan.”
Takira sunansa in a silent voice.

“Ummm.”
Ya amsa mata adai-dai lokacin daya maida bayansa, ya jingina da jikin kan gadon sabida wata fitinenneyar kasala da yaji muryarta ya fara sakar masa.

Itakuwa jin ya amsata ne yasa ta zama akan bedside drawer, tare da ajiye bottle water’n dake hannunta, magungunan nasa ta b’are tare da juyowa, cikin sanyi tace.

“Ga magungunanka kasha.”

Idanunsa yadan lumshe, tare da mik’a mata hannu yana me shak’an daddad’an k’amshin jikinta.

Akokarinta na zuba masa maganin acikin tafin hannunsa ne kuma, hannayensu suka had’e waje d’aya.

Da sauri ta zuba masa maganin, tare da janye hannunta daga cikin nasa, kana ta mik’a masa bottle water.

Saka maganin abakinsa yayi, tare da korawa da ruwa.

“Kana buk’atar wani abu?”.

Ta tambayesa asanyaye, saboda duk sanyi ya dameta, duk da cewar ta saka jacket amma tanajin sanyi sosai.

Kansa ya d’an girgiza mata alaman babu, kana ya d’an zame ya kwantar da kansa.

Ganin hakanne kuma yasa Jannart din shagwabe fuska, cikin lalllashi tace.

“Naan abinci fa, kaci koda babu.....”

“Shiiiiii nakoshi.”
Ya fad’i hakan ta hanyar katseta, da kuma wata irin muryar da tasa duk jikinta yayi week.

D’an k’aramin bakinta ta turo gaba, batare kuma da ta sake ce masa komai ba, ta tashi ta koma tsakiyan d’akin.

Rayyern kuwa Idanunsa ya zubawa bayanta, ga mamakinsa kuma, sai gani yayi ta zame ta

kwanta ak'asan sofa, batare dako pillow da blanket ta d'auka ba.

Still idanunsa ya sake tsura mata, acikin zuciyarsa kuwa cewa yayi.

"This girl me take nufi, anan zata kwana ne ko meye, wannan wanni irin jarababben gadi ne? Shin wai bata san kusancinta dani zai matsala bace".

Itadai Jannart bata sanma me yake fad'a acikin zuciyar tasa ba, batare da ta damu ba  gyara kwanciyarta tayi, hade da d'aukar wayarta ta soma dannawa.

Wannan dalilin yasa d'akin nasu ya d'auki shiru, babu abunda ke tashi sai sautin latsa waya da kuma system d'insa.

Almost 30mn suka d'auka ahaka, wanda zuwa yanzu Jannart ta ajiye wayan nata, Yayinda ta kwanta idanunta na Kallon sama, jacket din dake jikinta kuwa, tuni ya zame wanda hakan ya bawa, breast dinta daman bayyana ta cikin net din saman rigar.

Rayyern dake saman gado kuwa, time to time yake d'ago idanunsa ya kalleta, Yayinda Bedside lamp din dake gefen gadon nasa, ke  haskata hakan yasa yake iya ganin, komai da komai nata.

Acikin zuciyarsa kuwa mamakinta yake, tare da tunanin inda zata kwana, saboda yana ga kamar kwananta acikin d'akinsa bazai yiwu ba.

Saboda ya tabbatar da abunda yake zargi dinne kuma, yasa shi zamewa ya d'an kishingid'a akan  gadon, tare da ture system d'insa gefe, Ahankali ya lumshe idanunsa,  saboda har yanzu yana jin kamshin turarenta, acikin hancinsa.

Jannart kuwa jin d'akin yayi shiru ne, yasa ta juyowa ta zuba masa kyawawan Idanunta.

Ganin kamar bacci yayi azaune dinne, kuma yasa ta tashi ta zauna, still kuma kallonsa take, bata kawar da Idanunta ba.

Shikuwa Rayyern duk da cewar yaji ajikinsa tana kallonsa, amma saiya fusge bai ko motsa ba.

Ahankali ta taso daga zaunen da take, tare da takowa ta k'araso inda yake.

Zama tayi ad'an gefen gadon, hade kuma da turo bakinta gaba,abayyane kuma cike da shagwab'a tace.

"Ka mayi baccinka cikin jin dadi, baka damu ba Koda ma zanji sanyi, kuma dubi yanda kayi bacci azaune, kamar baby boy tayaya ma to, ni zan fara iya gyara maka kwanciya bayan nasan kana da nauyi, ato gaskiya ni dai a'a zan barka a haka kawai, idan ka fad'o ma kai ka  jiyo, tunda kaima ai kanka ka sani."

Ta k'are maganan tana me kwab'e masa baki, tare da jifansa da harara, still kuma cikin shagwab'a tace.

"To Idan ya fad'o ma ai dole nine zanyi jinya, Idan ba haka ba yata narke jiki da idanu, yana cewa zafi-zafi, kalleshi da wani dogon hanci da jan bani, kamar na muntsine shi ma, Idan yaso ya farka ya gyara kwanciyar da kansa."

Ta kai karshen maganan nata, me Kallon faffad'an chest dinta, wanda gashin samansu suka kwanta lub.

Rayyern da yake jinta kuwa wani, irin dariyarta ne ya kamasa, saidai sam bai nuna mata cewar ba bacci yake ba, hasalima duk abunda takeyi din, yana kallonta ta tsakan kanin gashin idanunsa, Dan bawai ya rufe idanun nasa duka bane haka nan yakejin tamkar ya fizgota ya ruggume ta.

"Mutum sai yawan bacci, ko ayayama baccinsa yakeyi."

Ta kuma fad'a abayyane tare dakai hannunta, tayi kaman zata muntsine shi.

Shikuwa Rayyern Ganin hakane yasa shi, d'an matsawa tare dayin kamar zai fad'o kasa.

Ganin hakan yasa da sauri ta taroshi, wanda dalilin hakan yasa ya fad'a jikinta, kirjinsa da nata suka had'e waje d'aya.
Yayinda d'ayan hannunta kuwa tasa ta taro, system d'insa dake kokarin faduwa.

Rayyern kuwa jinsa acikin jikinta ne, yasa shi sake lumshe idanunsa tare da sakar mata duk wani nauyinsa, acikin zuciyarsa yace.

"Zanyi maganinki ne yarinya."

Wani irin numfashi taja, cikin wahalan jin nauyinsa tad'an zame tare da soma kokarin kwantar dashi.

Awahalce tace.
"Kai Gaskiya Naan kana da nauyi, sai kace wani doki, wayyo Allah na."

Ta kare maganan tana me fad'awa kan gadon, wanda hakan ya bata daman kwantar dashi, abaki bakin gadon.

Ajiyar zuciya ta sauke, tare da sake turo bakinta gaba still Cikin shagwab'a tace.

"Yanzu kam Idan ka sake fad'owo, Allah bazan taroka ba, saboda nauyinka zai iya b'allamin

murfin kirji."

Ta kare maganan tana me jera masa pillows agefensa.
Gudun kada ya fad'o din.

Ahankali ta zare hannunta dake k'asansa, cike da gajiya kuma ta juya ta sauk'a akan gadon.

K'asan sofa ta kuma komawa ta kwanta, tare da juya masa baya, tana me sauke numfashi akai akai, tamkar Wacce tayi wasan tsere.

Rayyern kuwa ganin ta kwanta ak'asan ne, yasa shi bud'e idanunsa, tare da sauke ganinsa akan bayanta.

Sosai yake kallonta musamman shape din jikinta, da ya bayyana.
Cikin mgnar zuci yace.
"Uhummm nine ma kamar doki ba".
Yana nan ahaka kuma har ya soma jiyo, sautin numfashinta na fita slowly, da alama kuma bacci ne ya d'auketa.

Ajiyar zuciya kawai ya sauk'e, tare da lumshe idanunsa, yana tuno irin yanda take ta hidima dashi tun daren jiya.

Hakanan yaji zuciyarsa tayi rauni sosai.

Ahankali ya kuma dawo da kallonsa gareta, idanu ya zuba mata ganin yanda take ta karkarwa, da'alama kuma sanyi ne ke damunta.

Ahankali ya zuro da k'afafunsa k'asa, Cikin dan kuzarin da yake dashi ya mik'e tsaye.

D'aya daga cikin pillows din dake kan gadon, ya d'auka ahankali ya nufo inda take kwance.

D'an rank'wafowa kanta yayi tare da sa hannunsa, ya d'aga kanta  ahankali ya saka mata pillown, dai-dai lokacin kuma ta juyo, tare da fesar da numfashin, dake nuna cewar baccin nata yayi nisa.

Idanunsa ya sauk'e akan breast dinta, wanda duk  suka fito suka bayyana kansu ta saman rigar ta.

Wani irin yaarr yaji ajikinsa, wanda hakan ya sashi saurin janye idanunsa daga wajen, saboda tunda yake bai tab'a ganin breast din mace haka ba.
Wani irin masifeffen karkarwa jikinsa ya farayi tamkar wanda aka jonawa wuta.
Da sauri ya janye Jikinsa baya, tare da d'aukan blanket ya rufa mata, ahankali ya koma ya kwanta, tare da rumtse idanunsa, yanajin yanda zuciyarsa ke bugawa da karfi, saboda ganin

kirjinta da yayi.

Ahaka da tunani kala kala acikin zuciyarsa, bacci ya d'aukesa.

5:00 am.

Ahankali ya d'an bud'e idanunsa, wanda bacci ya cika cikinsu, Jin k'aran alarm din dake tashi ne kuma, yasa shi mik'a hannunsa ya kashe alarm din.

D'an yunk'urawa yayi tare da tashi ya zauna.
Ahankali kuma ya juyar da kansa, inda ya sauk'e idanunsa akan Jannart dake kwance.
Bacci take cike da kwanciyar hankali, Yayinda duka jikinta kuma ke lullub'e da blanket din daya rufa mata, kasancewar kuma blanket ne mai kyau,  shiyasa kwata kwata ko sanyi bataji.

D'auke kansa daga kallonta yayi, tare da tashi anutse ya wuce bathroom.

Koda ya shiga da kansa ya had'a ruwan wanka, bayan yayi wankanne kuma ya d'auro al'walan sallan asuba.

Ahankali ya murd'a handle din kofar bathroom din ya fito, daga shi sai towel dake daure akunkuminsa, Yayinda duk jikinsa kuwa ke d'auke da danshin ruwa.
K'arasawa gaban mirror yayi, hade da daukan wani karamin towel ya shiga goge jikinsa.

Jannart dake kwance acan gefe kuwa, Jin alamun tafiyarsa ne yasa ta sake lumshe idanunta, tare da gyara kwanciyarta, kasancewar  tun tashinsa itama ta farka, saboda Acan cikin baccinta ta jiyo, k'aran alarm din, saidai ganin ya riga ta tashi, shiyasa tayi kamar mai bacci.

Shikuwa Rayyern gaba d'aya ma ya sha'afa da cewar, ba shi kad'ai bane ad'akin, saboda haka ne ma yaci gaba da sabgoginsa normal kamar yadda ya saba.

Bayan ya gama tsane ruwan jikin nasa ne kuma, ya ajiye towel din dake hannunsa,  batare da tunanin komai ba kuma yasa hannunsa ya zare, towel din daya d'aura akan waist din nasa. Wanda hakan ya sashi zama naked.

Wannan kuma yana daga cikin d'abi'arsa ta yau kullum, da kuma Koda yaushe, shiyasa arayuwarsa yafison zama shi kad'ai, saboda bayason wani ya gane masa tsiraicinsa Sabida muddin ya fito wonka a lokuta da dama yana tsane ruwan jikinsa yake wurgar da towel din gefe, kana yasa boxer.

Jannart dake kwance kuwa, Ahankali ta d'an bud'e Idanunta, kasancewar ta rufe duk jikinta har zuwa fuskarta da blanket dinne, kuma yasa ta sanya hannayenta, Ahankali ta d'anyi k'asa da blanket din, wanda hakan ya bawa fuskarta daman bayyana.

Jin motsin Rayyern din da tayi asaman ta, ne kuma yasa ta d’an juyowa, dai-dai lokacin kuma Rayyern din ke maida hankalinsa, ga agogo dan duba lokaci yayinda hannunsa ke riƙe da towel din yana ƙara tsane sumar kanshi da towel d'in kana yama mai mamakin tun daren shekaran jiya da Naan ɗinsa ta ta harba ta miƙe har yanzu bata rusunaba, kanshi ya ɗan jujjuya tare da cewa.
“Bataga haka bama tana cemin doki”.
Kwaffa ya ɗanyi tare da taune lip enshi na ƙasa.
Jannart kuwa d’ago Idanunta da tayi dinne, yasa ta sauk’e idanun nata akan surar jikin D ɗinsa dake tsaye tamkar an kafashi.
Cikin wani irin yanayi mai kama da tsananin kad’uwa, firgici kid’ima had’i da gigita ta saki wata iriyar k’ara tare da fusgo numfashinta, dake kokarin kwacewa, amatuk’ar tsorace ta rumtse Idanunta.
“Innalillahi wa innailaihi rajiun. hasbunallahiwani'imanwakil.
Hehyyyyyyyyyhhhhh!!!”.
Ta saki sautin da k’arfi tare da zazzaro idanunta gaba kana jiki duk na kerma da sauri kuma ta rumtse idanunta da azaban ƙarfi saboda tayi masifar razana da ganinsa a zaratan kuma ingarman  namijinsa.

Rayyern kuwa jin sautin fusgan numfashi, da kuma addu'o'in da k’aran da tayi ne, yasa shi dawowa hayyacinsa, cikin sauri ya kalli inda Jannart din take, lokaci d’aya kuma ya ware towel din nasa ya rufe jikinsa.
Cike da wani irin b’acin rai, takaici hadi kuma da tsananin kunyan gane masa surar jiki da tayi.

Sake maida kallonsa gareta yayi, yana mejin ransa nayi masa wani irin suya, afusace ya nufo ta.

Yayinda Ita kuwa Jannart duk jikinta ke ta faman rawa da makerketa, har yanzu kuma ta kasa bud’e Idanunta dake rumtse bare ta yi yunkurin huduba.

Rayyern kuwa cikin fushi da tsananin b’acin rai, ya nufota gadan-gadan,  yana isowa kusa da ita kuwa, ya sunkuya tare da yaye blanket din dake jikinta.

Hannunta ya kama tare da mik’ar da ita tsaye, cikin zafin nama da takaici, ya nufi hanyar fita daga d’akin.

Dai-dai sun iso bakin kofar ne kuma ya tsaya, tare dasa hannu ya bud’e kofar.

Kallon Jannart din yayi, ad’an hasale ya saka hannusa na dama ya tura ta waje.
Da karfi kuma ya maida kofar tasa ya rufe.

Jannart kuwa sai alokacin ta bud’e Idanunta, ganinta acikin falon da tayi ne kuma, ya sakata sauk’e wani kakkarfan Ajiyar zuciya, saboda awajenta itakam ya taimaketa nema, daya fito da ita daga cikin  d’akin.

Dan daya barta ta k’ara mintuna kad’an numfashinta zai iya daukewa, saboda abunda ta gani yafi k’arfin tunaninta ya dugunzuma lissafinta ya dai-dai-ta mata tunaninta.

Rayyern kuwa Koda ya maida kofar ya rufe, idanunsa ya rumtse cike da takaicin kansa, hadi da tsananin kunyan abunda ya aikata da jin takaicin wannan banzan ɗabiar tasa.

Hannayensa duka biyu yasa ya dafe kanshi, cikin d’acin rai yace.

“Why Rayyern Why? Meyasa zan bari wannan yarinyar ta ganni haka? Meyasa zan manta da cewar tana cikin d’akin? Meyasa? Jiya-jiya nan tace min inada nauyi kamar doki yanzu kuma ta ganni haka ya salam cewa zatayi D ɗina kamar na doki!!!”

Ya k’are maganan yana me sake matse kanshi,  Yayinda zuciyarsa ke masa wani irin kuna, naban takaici da kuma haushin kansa da yakeji bai tab’a jin takaicin wannan d’abi'ar tasaba sai yau.
A fili yace.
“In kuma ta kuskura tacemin abuna kamar na doki zataga yadda doki keyin sukuwa kuwa in ya samu sarari, zanyi mgnin bakin tsiwarne”.
Ya ƙare mgnar yana rumtse idanunshi.

Jannart kuwa dake waje a guje ta wuce bedroom dinta tana gudu harda wai-wai dan ji take kamar ma yana biyota ne, tana shiga kuwa ta maida kofar ta rufe k’am.

Hannayenta tasa duka biyu ta dafe kirjinta, dake bugawa kamar zai rabe biyu.

Idanunta ta d’an rumtse saboda wani irin juyawa da taji kanta nayi mata, saidai kuma ko second 6 ba ayi ba,  ta sake bud’e idanun amatuk’ar tsorace, saboda abunda ta gani din again shike yi mata yawo acikin Idanunta.

Da sauri ta d’an soma girgiza kanta, Cikin yanayin fargaba da kuma tsoro murya araunace tace.

“Nashiga uku ni Jannart meye idanuna suka ganemin? Meyasa na bud’e idanuna har na kalleshi da wannan ƙaton abun naaa, wayyo Allah na! Na shiga uku”.

Ta fad’a da  karfi saboda yanda idanunta,  ke sake d’auko mota hoton surar jikinsa.

Jikinta kuwa sosai yake rawa, saboda tsoratan da tayi ne kuma, yasa numfashinta kasa dawowa dai-dai.
Tunda take aduniyarta bata tab’a ganin Namiji haka ba, bata tab’a ganin full halittan Namiji haka ba sai yaudin.

Da sauri ta dan soma bubbuga kanta, ganin tsayuwa bazai yi mata bane kuma, yasa kaitsaye ta wuce toilet.

Tana shiga kuwa ta sakarwa kanta ruwa, duk da sanyin ruwan kuwa, amma bata jinsa, saboda duk atsorace take da abunda ta gani.

Haka dai tayi wankan ba'a nutse ba ta fito, bayan ta dauro alwala.

Yau din kam ko ruwan dake jikinta bata tsane ba, haka ta d'auko wata bubu abaya ta zura ajikinta, hijab ma babba ta saka, bayan ta hau kan sallaya ne kuma ta tada Sallah.

Acan b'angaren Rayyern kuwa, cikin takaicin kansa haka ya saka boxer, tare da daura farar jallabiya akai.

Bayan ya idar da sallah ne kuma, ya zauna dab'as Akan sallayan, tare dasa hannayensa ya dafe kansa.

Acikin zuciyarsa yakejin inama da ace, Ana dawo da abunda ya wuce, to Tabbas shikam daya dawo da wannan yanayin baya, ta yanda kafun yakai ga bayyana surarsa, zai tasheta yace ta tashi ta fice masa daga d'aki.

Babu abunda ke kona ransa kuma, face Idan ya tuna cewar Jannart din taga komai nasa, duk wani abu nasa na sirri ta gani abinda babu wani mahaluk'in daya gani daga Mamynshi sai Abbanshi suma tun yana yaro abinda babu wata ɗiya mace data taɓa ganin koda hanyan wurin ne,
"Yah Salam". Ya fad'i kwaffa ya kumayi.

"Mtswww."
Yaja wata tsuka mai sauti, tare da jingina kansa da jikin gadon, shi kad'ai ya soma sakin kwafa, Yayinda acikin ransa yake nadamar, kwana d'aki d'aya da ita.

Domin da ace ba'a d'akinsa ta kwana ba, da yanzu duk hakan bai faru ba.

Haka dai ya hau saman gado ya kwanta, yana me sakawa da kuncewa, inda kuma duk haushin kansa yake ji can kuma wani sashi na zuciyarsa ya fara raɗa masa wasu kalamai.

Jannart kam Koda ta idar da sallah, hayewa saman gadonta tayi tare, da takure jikinta waje daya.
Saboda har zuwa yanzu wani sashi na jikin nata, bai daina karkarwa ba.

Yayinda Idanunta kuwa bata isa lumshe suba, saboda da ta rufe idanun nata, hoton surar cikekken namijin duniya ne ke yawo acikinsu.

Ahankali ta soma dan karanta addu'an samun nutsuwa, cikin ikon Allah kuwa acikin mintuna kad'an taji zuciyarta, ta samu nutsuwa, wanda hakan shi yasa ta tashi, ta koma falo saboda

duk wani bacci, ya k’auracewa idanunta sabida data rufesu abinda ya firgitatan take gani tsagal a tsaye.

Koda ta fito falon zama tayi, duk wani tunanin da zai suffanta mata surar tasa kuwa, idan yazo kawar dashi take da gaggawa, wannan dalilin yasa take jin kamar bataga komai ba.

Tana nan dai azaune har gari ya gama wayewa.

Rayyern dake cikin d’aki kuwa, har yanzu abun na damunsa, saidai kuma babu yanda zaiyi, tunda har ta riga da ta gani.

Kamar yanda ya sabayi kullum, haka ma yau din domin, ganin gari ya gama yin haske ne ya sashi yi musu ordern abinci.

7:30 pm

Dai-dai ya bud’e murfin kofar dakin nasa ya fito, cikin shirinsa na riga da wando, wanda sukayi matukar yi masa kyau sosai.

Jin motsin fitowarsa ne kuma yasa, Jannart dake zaune afalon saurin sake yin k’asa da kanta, tare da kama y’an yatsunta ta had’esu awaje daya.

Kirjinta kuwa dukan uku uku ya shiga yi, saboda tsoro da kuma fargaba.

Shikuwa Rayyern ganinta acikin falonne, yasa shi tsare ta da idanu, ahasale yake kallonta, saboda yanason ganin ko zatayi tsaurin idon Kallonsa yaga iya fitsararta.

Cikin takun nuna isa ya karaso tsakiyan falon, duk da cewar bashi da isashshen lafiya amma haka ya cije.

Jannart da zuciyarta ke bugawa da karfi, Jin alamun takun tafiyarsa ne, yasa ta sakeyin kasa da kanta.

Ad’an tsorace kana cikin rawan murya tace.

“Ina kwana ya jiki.”

Harara ya watsa mata, tare da gyara tsayuwansa, cikin tsare gida da kuma son amayar da abunda ke zuciyarsa yace.

“Ya isa haka! Dan Allah ya isa haka nan domin naji sauki, ni yanzu babu abunda yake damuna, saboda haka dan Allah Janna ki dakatar da wannann gadin da kike min, bana buk’ata, nagaji da wannan takuran, bazan iyaba wallahi, bayan yawan kallona da kikeyi bai isaba, har kuma da

kalleni a yanayin da bai halatta ki kalleni ba, wannan wanne irin abune.
Yanzi ke kinji daɗin ganina a hakane Jannaaaaa?."

Ya kare maganan cikin wata iriyar narkekkiyar murya mai haɗe da sassayan sautin da baisan dalilin yinsaba.

Jannart kuwa Jin abunda ya fad'a d'inne ya sata, sakeyin kasa da kanta, tare da lumshe Idanunta, saboda ita bata ma da abuncewa, cause ba laifinta bane tunda ta sani ba'a yiwa ido shamaki.

Saidai koma meye ita tajawa kanta tasani, da bata kalleshi ba Aida yanzu tana zaune lafiya.

Dai-dai lokacinne kuma aka soma knocking kofar falon.

D'an hararanta Rayyern din yayi, tare kuma da wucewa yaje ya bud'e kofar, Ganin kuma ordern breakfast dinsu ne, ya samu isowa ya sashi karb'a, tare da juyowa ya dawo falon.

Akan d'aya daga cikin kujerun falon ya zauna, batare kuma daya sake kula Jannart dinba, ya bud'e breakfast din ya soma ci.

Jannart kuwa har yanzu kanta na k'asa, domin ta kasa d'agowa, sai faman wasa da yatsun hannunta da takeyi ta yaya ta ina zata iya d'ago kai bare ta kalleshi.

Kallo daya kuma zakayi mata kafahimci cewa, duk jikinta yayi sanyi, sannan kuma akwai alamar damuwa atattare da ita da yanayin tsananin kunya da takura.

Ahankali ya d'ago kansa tare da Kallon ta, ya tsaida idanunsa akanta.

Almost 3min yana kallonta, kafun daga bisani ya janye idanunsa daga kallonta,
for the first time kenan da yaji yayi mata, wani abu na rashin kyautawa.

Idanunsa ya dan lumshe Ahankali tare da fesar da sassanyan numfashi, lokaci daya kuma ya soma tuno, moment dinta alokacin da bashi da lafiya, sautin kukanta ya somaji nayi masa yawo acikin kunnuwansa.
Sannan ya tuna cewar akan k'afafunta, a jikinta ya share sama da 8hours akwance, batare da ta turesa ko nuna alamar gajiyawarta ba, tayi kuka sosai har saida Idanunta suka kumbura, duk saboda shi, then now tana zaune ne kuma, agarin da babu kowa nata still duk saboda shi.

Ahankali yaji wani irin rauni ya sauk'a acikin zuciyarsa, wanda hakan yasa shi sake d'aga idanunsa ya kalleta.

Dai-dai lokacinne kuma wayarsa ta soma k'ara.

Hannayensa yasa acikin aljihun wandonsa, tare da zaro wayar tasa.

Ganin sunan Riyyam  na yawo akan screen din wayar ne, kuma ya sashi picking call din.
Tare da kara wayar akan kunnensa.

“Good Morning Hamma Rayyern ya jiki?”

Riyyam din ya tambaya cikin kulawa.

Ahankali yadan sauke ajiyar zuciya, tare kuma da gyara zamansa cikin sanyi yace.

“Morning Riyyam jiki Alhamdulillah, yasu Mammy?”

“Duk Suna lafiya Hamma, yanzu ma Mammynce tace nakira mata kai, bari na bata wayan.”

Riyyam din ya fadi haka yana me mikawa Mammy dake gefensa waya.

“Barka da safiya Maud’ona.”
Mammy ta fad’a cikin kulawa, da kuma tausasa murya.

Wanda har saida hakan yasa Rayyern din sakin murmushi, cikin yanayin nishadin daya samu kansa aciki da jin sanyi a ransa da cikekkiyar nitsuwa yace.

“Yauwa Mammy inafatan kun tashi lafiya.”

“Lafiya k’alau Maud’o na, ya jikin naka?.”

Mammyn ta tambaya.

Idanunsa ya kuma lumshewa tare da cewa.
“Alhamdulillah Mammy naji sauki sosai.”

“Masha Allah, haka akeso ai Allah ya kara afuwa, Ina surukata Jannart sarkin kuka?”
Mammyn ta fad’i hakan cikin d’an sakin fuska, saboda har acikin zuciyarta, takejin son yarinyar.

Shikuwa Rayyern tambayar da Mammyn tayi masa ne, ya sashi bud’e idanunsa tare da Kallon Jannart din, da duk mood dinta ya sanja zuwa asalin Jannart ɗinta mai cikekken rauni da rashin anci da tsoron fushin wani.

Yayinda har yanzu kuwa saman Idanunta ke d’an kumbure, saboda kukan da tayi daren shekaran jiya.

Maida idanun nasa yayi ya lumshe, saboda wani irin abu na musamman da yaji, ya tab’a k’ahon

zuciyarsa yana mai ratsa zuciyar tasa yana shiga cikin asalin ƙahon zuciyartasa.

Ahankali kuma cikin sanyin murya yace.

“Tana lafiya Mammy.”

Daga can b’angaren kuwa murmushi Mammyn tayi, hade da cewa.

“Masha Allah  Idan tana kusa bata wayan mu gaisa.”

“To.”
Ya fad’a asanyaye, tare kuma da d’ago kansa ya kuma Kallon Jannart din.

“Zo nan Janna”
Ya fad’a yana kallonta.

Ita kuwa Jannart shiru tayi tana tunanin ta yaya zata fuskanceshi.
“Kizo”.
Ya kuma fad’a cikin narkekkiyar murya tare da d’ansa hannunshi ya rufe speaker'n wayar.
K’ara sunkuyar da kanta tayi k’asa sosai.
“Zo nan Janna mai masoya da yawa. Kizi kuyi magana da Mammy kinji ko Janna.”

Ya fad’i hakan cikin tsareta da idanu, tare kuma da mik’a mata hannunsa dake rike da wayar.

Jannart kuwa sanin cewar da ita yake ne kuma jin yadda yayi mgnar murya a dakene, yasa ta tasowa batare kuma da ta kalleshi ba, ta karaso ta karbi wayan.

“Assalamu Alaikum Ina kwana Mammy.”
Jannart d’in ta fad’a cikin sanyin murya, hade kuma da juyawa Rayyern din baya, domin batason su hada idanu.

Mammy dake kan layi kuwa, Jin muryar Jannart dinne ya sata fad’ad’a murmushin ta, cikin sakin fuska tace.

“Wa’alaikissalam, lafiya kalau Jannart ya mai jiki?”

“Da sauki sosai Mammy yasu Zaytoon da Riyyam.”
Jannart din ta tambaya tana me kokarin boye damuwarta.

“Lafiyansu kalau, Jannart dama nace bari na kira na tambayi lafiyarsa, Allah ya kara karfin jiki, dan Allah  ki ci gaba da kulawa dashi, sosai kinji Jannart Insha Allah. Allah zai baki ladan hakan.”

“To Mamy Insha Allah nagode sosai.”
Jannart din ta fadi haka cikin girmama, maganan Mammyn saboda haka kawai takejin matar, tana da matsayi awajenta.

Bayan sunyi sallama da Mammyn ne kuma, ta zare wayar daga kunnenta, tare kuma da juyowa ahankali ta mika masa wayan.
Saidai har yanzun bata bari Idanunta sun kalleshi ba sabida masifar kunyarsa da shakkar sa da takeji, domin wallahi muddin kaga tsiraicin wani to sai kaji kama fiji jin kunyar.

Lura da hakan da yayi dinne kuma yasa, shi karb’an wayan nasa, saidai ya kasa dauke idanunsa daga kallonta.

Itakuwa Jannart komawa tayi ta zauna, tare da tank’washe kafafunta kai a sunkuye, cikin sanyin murya tace.

“Mammy tace kana cin abinci, haka Mamy ma kullum sai ta fad’a, please kana cin abinci saboda zama da yunwa yana yiwa mutum illa.”

Ta k’are maganan tana me wasa, da adon bakin kasan rigar dake jikinta.

Rayyern din kuwa idanunsa ya d’an lumshe, kana ahankali yace.

“Uhumm naji Likita”.
Idonta ta jujjuya watoma gatse ya mata.
Idon ta dam juya kad’an jin yana cewa.
“Yanzu ke kizo kici abinci.”

Kanta ta d’an girgiza, still batare da ta kalleshi ba tace.

“Ni nak’oshi, kuma ai kaine marar lafiya Kai ya kamata kaci sai kasha magani.”

D’an k’aramin bakinta dake motsawa ya kalla, lokaci daya kuma cikin kasalan daya sauk’ar masa yace.

“Bani kad’ai nake da buk’atar abinci ba ai har dake, oya zo ki zauna kici kiji ko Janna.”
Ya yi maganan nasa cikin bada umarni.

Kanta ta d’an girgiza Ahankali, tare kuma da shagwabe fuska, cikin turo baki tace.

“Ni nakoshi sai anjima zanci.”

Idanunsa yadan jujjuya tare da jinjina kansa, batare daya sake cewa komai ba, kuma ya Mike tsaye.

Sai alokacin tayi saurin d’ago da kanta ta kalleshi, cikin rashin sa'a kuwa karab  idanunsu suka fad’a cikin na juna.

Da sauri ta kawar da kanta gefe.
Shi kuwa baki ya tab’e tare da cewa.
“Taurin kai ba! Da gardama ko”.
Bata fahimci mgnar tasa ba saima,
Ganin da tayi kamar fita zaiyi ne kuma yasa ta cewa.

“Baka sha magungunan kaba.”

Cikin yanayin kwaɓe fuska yace.
“Bazan shaba”.
Da sauri ta zarin Iedan maganin tare da matsowa gabansa.
Cikin rauni ido na gab da kawo hawaye tace.
“Please Naanu kasha mgni”.
Wani irin shu'imin kallo ya tsareta dasu,
haka nan yaji kamar zuciyarsa na buɗe wa ne.

“Nasha.”
Ya fad’a atakaice, tare kuma da nufar kofar fita daga falon.

Bayansa tabi da kallo, Ganin da gaske fita zaiyi ne kuma, yasa ta maida kanta kasa, murya asanyaye tace.

“Please Idan ka fita tayaya zan iya sanin halin da kake ciki?”
Ta kare maganan cikin dan inda inda, wanda hakan ke nuna masa zallan abunda take nufi.

Hannunsa yasa acikin al'jihunsa, tare da zaro k’aramar wayarsa ya mika mata.
Hannu tasa ta karb’ wayan, Yayinda shikuwa kaitsaye ya fice daga cikin falon.

Ganin fitan nasa ne kuma, yasa Jannart din Iumshe idanunta, tare dakai hannunta kan hancinta, tana me shak’an daddad’an kamshinsa, wanda ya kama tafin hannunta, sanadiyar rik’e wayarsa da tayi.

Rayyern kuwa yana fitowa motarsa ya shiga, inda direct Babban EUROUPEAN Medical senter mascow (E.M.C) Hospital din da suke gudanar da taron nasu ya nufa.

Koda yaje sunyi mamakin ganinsa kwarai, amma saidai sanin jajircewarsa akan aiki yasa su jinjina masa.
Haka dai suka fara meeting di nasu, wanda suka sabayi akowacce rana.

Acan gida kuwa Jannart ba ita tayi breakfast dinba, sai wajajen karfe sha biyu, bayan ta kammala breakfast dinne kuma ta kimtsa wajen, tare da dawowa falon ta kunna kallo.

Karamar wayar tasa Samsong dake hannunta, take Dan jujjuyawa ahankali, zuciyarta cike take dason sanin halin lafiyarsa, saidai kuma amma bata da numbernsa wacce zata kirasa dashi. Domin Koda ta bincika wayar daya bata din, bata samu komai ba Gallery ta leƙa nanma wayam babu komai kwaffa tayi tare da cewa.
“Shi ko hotama bayayi”.

Hakanne kuma yasa ta yanke shawaran, daukan numbern Ramadan ta kirasa.

Bugu biyu kuwa Ramadan din ya dauka.

“Ramadan.”
Jannart din ta kira sunanshi.

“Na’am Aunty Jannart.”
Ramadan din ya amsa mata, Cikin kulawa tare dayi mata tambayar ya gida.

Da lafiya ta amsa, kana tace ya tura mata numbern Rayyern din, saboda tanason zatayi magana dashi.

Murmushi Ramadan yayi, cikin kuma jin dadin irin kulawan da Jannart din ke bawa Hamman nashi, yace.

“Don’t worry Aunty Jannart bari na turo miki.”

Hakan kuwa akayi domin cikin mintuna 2 Ramadan ya turo mata numbern.

Ganin ya turo mata numbern ne kuma yasa ta tashi, tare da wucewa bathroom ta dauro alwala.

Anan cikin falon ta dawo tayi sallah, bayan ta  idar da sallan ne kuma, tayi dialing numbern Rayyern din.

Wanda adai-dai lokacin ne kuma suka fito daga taron k’arawa juna sani da suka shiga.

Tsaye yake akan step yana Kallon wani ruwan swimming pool shi kansa bai san nazarin me yakeyiba bai kuma san me yake tunawa ba, kai baima san me yake kallo a cikin ruwanba, Jin wayarsa na k’ara ne kuma yasa shi, zaro wayar daga cikin al'jihunsa.

Ahankali ya zubawa screen din wayar tasa ido, saboda ganin numbern dake kira, wanda yake mallakinsa ne,  d’an jim yayi har saida wayan ta kusa katsewa, kafun ya d’aga tare da kara wayan akan kunnensa.

Daga can b’angaren Jannart kuwa jin an d’aga wayarne, yasa ta yin sallama kana murya atausashe tace.
“Naan”.
Cikin wata iriyar fitinenneyar murya yace.
“Na'am Janna”.
Cikin sanyi tace
“Naan ya jikin naka? babu inda yakeyi maka ciwo ko? Kaci abinci ko?”.

Idanunsa ya d’an lumshe, Ahankali kuma Cikin sanyi kamar yanda tayi masa maganan yace.

“Da sauki sosai Janna, I think I’m telling you na warke.”

Ajiyar zuciya ta d’an sauke ahankali, batare kuma da ta damu da abunda yace dinba, cikin tausasa murya tace.

“Please Hamma Naanu kaci abinci?”

“A'a banajin yunwa, but Idan na dawo zanci.”

Ya fadi hakan saboda bayason ta matsa mishi da yawan tambayoyi da muryata dake sashi wani yanayin.

Fahimtar hakan da tayi dinne kuma yasa ta, gyara zamanta tare da cewa.

“Uhumm Saika dawo.”

“Yauwa.”
Ya fad’a tare da zare wayar akan kunnensa.
Kana cikin sanyin da yaji zuciyarsa tayi, ya juya ya koma cikin dakin taron nasu.

Itama Jannart tana ajiye wayan kwanciya tayi, tare da lumshe Idanunta, domin sai ayanzu taji sauki sakamakon jin cewar yana lafiya.

8:30 pm Dai-dai ya shigo cikin gidan, hannayensa rike da ledodin Sabor de la vida restaurant.

Anan cikin falon ya zauna, tare da bud’e ledodin, ganinsa ne kuma yasa Jannart din yi masa sannu da dawowa.
Tare da d’auko plate ta zuba masa abincin.

Yana kammala cin abincin nasa ne kuma ya wuce d’akinsa, saboda yana da buk’atar yin wanka.

Tashin nasa ne kuma ya bawa Jannart daman, cin abincin bayan ta kammala ne kuma ta wuce d’akinta.

Almost 1hour

Tsab ya gama shirya kansa cikin kayan bacci, bayan ya kammala duk wani abunda yakeyi dinne kuma,  ya hau kan gadonsa ya kwanta.

Anutse ya zubawa kofar shigowa dakin nasa idanu, wanda kuma shi kansa baisan me yake kallo ba.
Saidai kuma har acikin ransa baya jin dadin, rashin zuwan da Jannart batayi ba,  wanda yasani kuma akan maganan daya fada mata d’azu ne ya fahimci tana da saurin amsar umarni da bin dokar mutum.

Idanunsa ya dan lumshe yana mejin wani yanayi akan abunda yayi mata din.

Saboda Tabashi dukkan  kulawa sosai alokacin da yake buk’atar hakan.

Ahankali ya juya ya kwanta tare da rumtse ido.
3 mnt tsakani ya kuma juyowa ya tashi zaune tare da zuro  kafafunsa kasa, tare da tashi tsaye daga kwancen da yake.

Kaitsaye batare da kokwanto ko gama yanke hukunci ba, ya bud’e kofar dakin nasa ya fice.

Koda ya fito falon kaitsaye bedroom dinta ya nufa.

Dai-dai lokacin kuwa Jannart din ta gama shirya kanta cikin, wani purple sleeping dress mai kyau, wanda yabi duk jikinta, kana kuma ya sake bayyana hasken fatarta.

Tsaye take agaban mirror tana tubke gashin kanta, dai-dai lokacin ya turo kofar dakin ya shigo.

Jin motsin kofane kuma yasa ta, juyowa da sauri ganinsa da tayi, abakin kofar ne kuma yasa ta juyowa tare da nufosa, gaba daya kuma ta manta da irin shigar dake jikinta.

Haka ta nufosa, shikuwa Rayyern tsayawa yayi yana kallonta, musamman yanda shape din jikinta ya bayyana.
Ga kuma breast dinta da yake ganinsu abayyane, saboda shigar dake jikinta sunyi wani cir kamar zasu tsole mishi idanu.

“Naan.”
Jannart din ta kira sunansa.

Kasa amsa mata yayi, saima zuba mata idanu da yayi yana kallonta.

Yayinda yakejin wani irin abu na fusgansa akanta.

Jannart kuwa Ganin hakanne yasa ta gyara tsayuwarta, tare da kallonsa Cikin kulawa tace.

“Naan kana buk’atar wani abune?”

Kansa ya gyad’a mata kana ahankali murya can ƙasa maƙoshi a narke yace

“Zaki tsole min idofa su tsiyay...”.
Ya faɗi mgnar a fizge bisa alamu bai san ta subce mushiba.
Sabida yadda ya haɗiye rogowar mgnar a cikinsa.
Tare kuma da yin kici-kici da fuska ya zuba mata ido.
Cikin rashin fahimta kalamansa tace.
“Zan tsole maka ido kuma? Ta yaya da me d’in zan tsole maka idon?”.
Bai kulataba kuma bai janye idanunsa a kantaba, ganin haka yasa cikin sanyi tace.
“Naan kayi shiru kayi mgna mana me kake buƙatar?”.
Numfashi ya d’an fesar a hankali kana yace.
“Yau bazaki tayani kwana bane?”

Idanunsa ta d’an kalla tare da cewa.

“To baka warke ba.”
A hankali ya sauke hannunsa dake harde a kirjinsa, kana yayi taku biyu zuwa uku
Matsota yayi sosai tare kwantar da kanshi bisa kafaɗarsa narkakkun idanunsa ya watsa mata murya a narke yace.
“Ni..!

*GARKUWAR taku ce dai MA'AURATA, da masu shirin aure, da masu jego, da yan gayu masu son k’amshi kece raini, da gyaran da zaike maimaita muku dararen forkon kuruciya*

Ko kunsan Jikinmu na da sinadaran hormones da suke taimakawa dan’adam akan komai musamman lokacin da mace take mu’amalar aure da mijinta. Mafi akasari wannan hormones din ne ke samun matsala ko su yi sanyi koma su daina aiki kwata-kwata shi ne dalilin da zai sa mace tace bata jin sha’awa ko bata san dadin aure ba. Albishirinku ina da kayan da ke taimakawa wannan sinadaran du dawo aiki tukuru don karkato miki da kimarki wajan mai gida sannan su taimakawa wannan sinadaran hormones dinki su dinka secreting din ni’ima wadatacciya da zata taimaka miki ki gamsu mijinki ya gamsu fiye da tunaninki. Note: Kayana ba sa tsinka ruwan ni’ima suna dai taimakawa hormones dinki ne su tsattsafo da ni’imar musamman wacca cutar sanyi ko dattin mahaifa ya dankarar da su ya hana su yin aikinsu

yanda ya kamata. Haka zalika idan kina da kyau ki kara da wanka. Zaki iya amfani da magani na na gargajiya wanda zai gyara miki sex hormones din kullum ki kasance cikin humidify wato cikin damshi mai albarka kamar yanda ake son mace. Yana gyara miki mara.

Sai kamshi. Hajiyata daure ki fara amfani da turarena ki ji irin salon kamshin sa salo ne da zai daidaita ki da mijinki ya kankaro miki da kimarki a wajansa. Siyan na gari mayar da kudi gida.

Ga masu buƙata ga number' wayata wanda nake whatsApp dashi 09097853276 kimin mgn ta whatsApp in har kin tabbatar kin shirya saya mu dai-dai ta, kayana ba ƙanana bane, shiyasa bana harkan karanta, muddin kinsan baki shirya sayaba Please kada kiyi min mgn ki bari sai kin shirya kuɗinki a hannu,  ba ina nufin kayana bana talaka bane, no akwai ƙananan set na masu karamin karfi, banson aimin mgn a ɓatamin lokacin aiyukana a shirme baki shiryaba. Shine karantan da bana so.
0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU. In kin shirya ga number ta ga kuma account number ta wanda in mun gama mgn zaki turo kudin ki, kana insa miki kaya a mota, duk ƙasar da kike kayana zaije gareki, amman fa in kinada dalilin zuwan nasune🤝🏻sayan na gari meda kudi  gida.

GARKUWAR MA'AURATA

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:55 - 🥰🥰: TUBALI
Page 19
NA
*AYSHA ALIYU GARKUWA*

“Ni kuma........”
Ya fad’i maganar cikin wata irin kasalalliyar muryar, dake bayyana mood din da yake ciki, kana daga gefe guda kuwa ga idanunsa dake lumshewa.

Jannart dake tsaye kuwa Ganin yayi shiru ne, yasa ta d’an zubawa kyakkyawar fuskarsa ido. Saboda bata tab’a ganinsa acikin irin wannan yanayin ba.

“NAAN!”
Takira sunansa asanyaye, cikin kuma Dan yanayin karyar da wuyanta gefe.

Saboda saukar muryarta acikin kunnuwansa ne kuma, ya sashi jin wani irin abu na sauk’a had’i da yawo acikin  jikinsa.

Wanda hakan yasa  ahankali, ya ajiye idanunsa akan yatsun k'afarta.
Anutse kuma ya soma yawo da idanun nasa, yanayin sama dasu,  har dai ya kawo idanun nasa, izuwa kan tsarerren hips dinta.
Still kuma da maraitattun idanun nasa, ya kuma tafiya har zuwa kan kirjinta,  inda breast dinta suka bayyana sosai, ta saman wuyan rigar   Dake jikinta, kasancewar kuma rigar nata irin mai net dinnnan ne, kuma black colour shiyasa, hasken fatarta ya bayyana sosai.

Idanun nasa daya kuma sauk'ewa akan, beautiful nipples dinta ne ya sashi jin, wani irin abu ya tsarga masa, tun daga tafin k'afarsa har zuwa tsakiyan bayansa, da kuma D.... d'insa.

Wani irin fusga  numfashin nasa yayi, wanda hakan yasa awahalce ya janye idanun nasa daga kan k'irjinta, tare da maida kallonsa ga fuskarta.

Itakuwa dake tsaye ganin ya dawo da kallonsa, ga fuskarta ne yasa ta janye Idanunta, daga Kallon gefen fuskarsa da takeyi, da sauri tayi k'asa da Idanunta, tare da had'e yan yatsunta waje d'aya ta soma murzasu.

Siraran labb'anta wanda suka sha, lips gloss ya kalla, kana ahankali ya kuma matsowa kusa da ita, sukayi kusan ci sosai.

Hakanne kuma yasa numfashinsa, sauk'a akan  kyakkyawar fuskarta.

Narkakkun idanunsa ya zuba mata, cikin kuma wata irin murya, irin Wacce bata tab'a ji daga garesa ba yace.

"Muna fad'a ne.....!"

Ya k'are maganan cikin salo na musamman, tare kuma da fesa mata numfashinsa akan fuskarta.

A sanadiyar hakan ne kuma, yasa taji tsikar jikinta na tashi,   Ga kuma wani irin abu da taji acikin jikinta, wanda bata tab'a jin makamancinsa.

Tabbas ba zata iya jurewa yanda suke dinba, domin akowani saukar numfashinsa ajikinta, wani irin abu takeji na yawo acikin jikinta.

Sanin da tayi cewar ba zata iya kallonsa bane kuma, yasa ahankali ta lumshe Idanunta, tare da girgiza masa Kai, cikin sanyin yanayi alaman babu.

Kansa ya d'an girgiza shi d'inma, tare da sake matsowa kusa da ita, ahankali yace.

"To Meyasa kike fushi dani?"

“Nifa Naan bana fushi...”
Ta fad’i maganar cikin sigar shagwab’a, tare kuma da turo d’an k’aramin bakinta gaba.

Lips din nata ya kuma kallo, still yana mejin wani irin abu nayi masa yawo acikin jikinsa, in a silent voice yace.

“To Meyasa yau bakizo kin bani mgnina ba, bakince kina gadina ba, kuma dama ai kince saboda gadi na ne, kawai Abba ya turo ki, yanzu har kin gama gadinne ko kuma umarnin Abbanne ya k’are ummmmm?”.

Ya Kai karshen maganan nasa, cikin wani sautin daya sata d’agowa ta kalleshi.
Saidai kuma ganin yanda cikin idanunsa, suka sauya launi izuwa na maye ne yasa tayi saurin k’asa da kanta.

Asanyaye kuma tace.
“To baka ce ka samu lafiya ba.”

“Ummm.”
Ya amsa mata ahankali, tare da zura duka hannayensa acikin aljihun rigarsa.

“To Allah ya kara sauki.”
Jannart din ta fad’a ashagwab’e, tare kuma da kawar da kanta gefe, saboda matukar numfashinsa, ya ci gaba da sauk’a akan fuskarta, To babu makawa zata iya sume masa.

Shikuwa Rayyern ganin hakan da yayi ne, yasa shi jinjina kansa, had’e da cewa.

“Ameen.”
ahankali kuma ya janye jikinsa baya, tare da juyawa batare da ya sake ce mata komai ba ya fice daga cikin dakin.

Jin alamun takun tafiyarsa, da kuma yanda ya fad’i Ameen din, acikin rashin dad’in yanayi ne, yasa ta d’ago Kai ta kalleshi.

Amma kuma sai taga ko juyowa baiyi ba, direct ya fice daga cikin d’akin.

Asanyaye tabi bayansa da kallo, tare da sauk’e ajiyar zuciya, cikin sanyi kuma ta lumshe Idanunta, tana me sake shak’an kamshinsa mai matuk’ar dadi.

Shikuwa Rayyern yana fita daga d’akin nata, direct cikin falo ya fito, ahankali ya zauna akan d’aya daga cikin kujerun falon, tare da jingina jikinsa da kujeran ya lumshe idanunsa.

Almost 10mn Ahankali ya sauke ajiyar zuciya, tare kuma da zamewa ya kwanta akan kujeran.

Hakanan yakejin tamkar babu wani abu akusa dashi, like yayi losing  wani important abu nasa.

Jannart kuwa Ganin ta fiyar nasa ne, ya sata koma ta kwanta, akan gadonta  hade
da lumshe Idanunta, Ahankali take sauraran yanda zuciyarta ke bugawa, sanadiyar kusan cin
da suka samu atsakanin junansu d’azun.

Rayyern kuwa Ganin da yayi zaman falon ya ishesa ne, ya sashi komawa d’aki, ya d’auko
system d’insa.

Jin da yayi dakin Yayi masa sarari da maraicine kuma, ya sashi sake dawowa falon.

Anan kan kujera ya zauna, tare da d’aukan laptop din nasa ya soma duba bayanan sabon
companyn su.
Wanda zuwa yanzu komai na companyn yana tafiya dai-dai, domin sun samu share holders da
yawa, baya ga haka kuma ana nan anata, sarrafa kayan masarufi, ba kuma iya alkama kawai
suke sarrafawa ba, harma da shinkafa shanshera, wanda yanzu haka managernsa ya tafi,
Gombe Dan saro musu shinkafan.

Kusan mintuna 20 ya share yana duba, yanda harkar companyn nasa ke tafiya, bayan ya
kammala ne kuma ya shiga, cikin mails dinsa saboda amsar sakonnin da ake tura masa arana,
kusan sama da 1000.

Kamar Koda yaushe kad’an daga cikin sak’on ya duba.
Sakon last daya duba kuma shine, wanda ya kama dole sai yayi reply, saboda wasu code ne zai
turawa d’ayan companynsa.

Kansa ya d’an dafe Ahankali saboda, tunawa da yayi cewar code din suna cikin karamar
wayarsa, Wacce ke hannun Jannart.

Ahankali ya d’an juyo da kansa ya kalli, kofar dakin nata,  duhun da yagani ta tsakankanin kofa
ne kuma, yasa shi fahimtar cewa harta kwanta.

D’an k’aramin tsuka yaja, tare da rufe laptop din, Ahankali ya maida jikinsa ya kwantar akan
kujeran.

Numfashi ya d’an fesar, tare kuma da lumshe idanunsa, kwata kwata baisan Meyasa yakejin
kansa, kamar ba’a daidai ba haka nan yakejin sa kamar yana cikin maraicin kaɗaici.
Haka kuma baisan dalilin da yasa shi, yake yawan jin kasala ba, Yayinda bakin abubuwa ke
bijiro masa acikin Y’an kwanakin, gaba d’aya yasan ba haka yake ba.

Sake gyara kwanciyarsa yayi, tare da rumtse idanunsa way’anda keyi masa gizo da

kyakkyawan surar jikin Jannart din, musamman kirjinta wanda akoda yaushe Idan ya kalla, sai yaji tsikar jikinsa ya tashi.

Kasancewar tun kallo dazu da yayi mata, har zuwa yanzu tsikar jikinsa baidaina tashi ba.
Haka kuma yakejin wani irin abu na yawo acikin jikinsa, musamman jijiyoyin  dick d’insa dake mommotsawa.

Matse jikinsa waje d’aya yayi, tare da d’aukan trow pillow ya d’aura kansa akai.
Da k’arfi ya kuma rumtse idanunsa, tare da fatan Allah yasa bacci yayi gaggawar d’aukarsa.

Kasancewar kuma yasa maganinsa, mintuna 30 da suka wuce, shiyasa bai wani sha wahala ba baccin ya d’aukesa ahaka, Yana nan kwance akan kujera batare daya shiga cikin bedroom d’insa ba.

Ab’angaren Jannart kuwa sam bacci ya ki d’aukarta da wuri, saboda hakanan takejin duk jikinta yayi sanyi, Yayinda zuciyarta ke raya mata cewar, kamar Rayyern din yayi fushi ne.

Sake gyara kwanciyarta tayi hade da lumshe Idanunta, wanda sukeyi mata gizo da  nasa idanun.

Tananan ahaka bacci ya d’auketa, saidai har acikin zuciyarta da tunaninsa tayi bacci.

*Washegari.*

Kamar yanda ya saba tashi akowacce rana haka yau dinma.
Ahankali ya dan bud’e idanunsa tare da tashi ya zauna.
Acikin bakinsa yake ambaton sunan Allah, tare kuma da d’an k’arewa falon kallo.

Duk da kasancewar babu isashshen haske acikin falon, amma hakan bai hanashi Ganin lokaci, ajikin agogon dake kafe ba.

Sanin da yayi cewar Idan ya tsaya zai iya rasa jam’ee ne, yasa shi mikewa tsaye tare da nufan d’akinsa.

Koda ya shiga alwala yayi, kasancewar yanajin karfin jikinsa yau dinne kuma, ya sashi daukan carkey d’insa, tare da bud’e kofar dakin ya fice.

Koda ya fito compound din gidan motarsa ya shiga,ba tare daya tsaya wani b’ata lokaci ba kuma, kaitsaye ya nufi masallaci.

Jannart kuwa jin Karan fitan motarsa ne, yasa ta bud’e Idanunta ahankali, tare da mik’a hannunta sama ta kunna wuta.
Agogo ta kalla, Ganin lokacin sallah yayi ne, kuma ya sata saukowa daga kan gadon, direct

toilet ta wuce ta d'auro alwala.
Tana fitowa kuwa ta shumfud'a Sallaya ta tada sallah.

Koda ta idar da sallan komawa tayi ta kwanta, saboda duk ji take baccin bai isheta ba.

Acan b'angaren Rayyern kuwa, Koda suka idar da sallah bai bar cikin masallacin ba, har saida gari ya fara haske.

Bayan yayi musu ordern abinci ne kuma, ya kama hanyar dawowa gidan.

Kaitsaye dakinsa ya wuce, bayan ya rage kayan jikinsa ne kuma, ya shiga wankan da mintuna 20 kacal ya b'ata wajen yinsa.

Ahankali ya murd'a handle din kofar, toilet din ya fito hannunsa rike da  Dan karamin towel yana tsane jikinsa.

Bayan ya kammala tsane jikin nasa ne kuma, ya shafa body lotion mai kamshi, tare da bud'e drawer ya ciro, wani had'add'en suit mai tsadar gaske.

Anutse ya saka boxer da singlet d'insa, kana cikin dan hanzarin kada ya makara ya shirya kansa cikin suit din nasa, mai kalan army green wanda yayi matukar yi masa kyau.

Cikar haibar kwalliyan nasa ya sake fitowa ne kuma, musamman daya saka takalmin sau ciki army green, da kuma agogon kamfanin Rolex ahannunsa.

Briefcase da kuma wayarsa ya d'auka, cikin takunsa na alfarma ya fita zuwa falon.

Dai-dai lokacin ne kuma delivery ya kawo masa ordern abincin da yayi.

Karb'an abincin yayi, tare da komawa Cikin falon ya zauna.

Bud'e ledan yayi tare da ciro takeaway d'aya ya bud'e,  Kallon abincin dake cikin takeway din yayi, kana ahankali kuma ya d'ago da kansa ya kalli kofar d'akin nata.

Idanunsa ya dan zubawa kofar domin baiga alaman cewa an bud'eta ba,  na yan wasu mintuna ya kalli kofar, lokaci daya kuma ya dauke kansa, tare da daukan spoon ya soma d'an tsakalan abincin dake gabansa.

Kwata kwata kuma bai wuce loma 4 yayi ba, ya ture takeway din gefe saboda har yanzu bawai yana wani jin dadin bakinsa bane Chocolate din daya ɗebo ya fara gutsara yana taunawa a hankali saida yaji ya ɗa koshi kana yaja ledan maganibsa.

Bayan yasha maganinsa ne kuma ya mik'e tsaye, still ya kuma Kallon kofar dakin nata, kamar

wani wanda ke tsammatan wani abu, dai-dai lokacin kuma wayarsa dake cikin aljihunsa ta soma k'ara.

Zaro wayar daga cikin aljihun nasa yayi, Ganin da yayi sunan Abbansa na yawo akan screen din wayarne kuma ya sashi, picking call din tare da kara wayar akan kunnensa, cikin dan yanayin girmamawa yace.

"Assalamu Alaikum Abba Ina kwana."

Daga can b'angaren Abba dake zaune akusa da Mamy, Jin muryar Rayyern din wasai ne ya sashi, Dan fadada murmushi kana cikin kulawa yace.

"Wa'alaikassalam, lafiya kalau Rayyern ya jikin naka?"

"Alhamdulillah Abba naji sauki sosai, Dan yanzu haka ma wajen aiki zan tafi."

Rayyern din ya fada yana me janye idanunsa daga Kallon kofar dakin Jannart din.

Abba kuwa Ajiyar zuciya ya sauke, saboda ko daga sautin muryar Rayyern din, kasan Masha Allah yaji sauki.

Cikin jin dadin hakan kuwa yace.
"Masha Allah haka akeso ai, Allah ya kara maka lafiya, amma kada ka manta da shan magunguna akan lokaci, ina Jannart fatan tana lafiya?"

Idanunsa ya dan lumshe ahankali, kuma cikin sanyin murya yace.

"Lafiyanta kalau."

Kai Abban ya girgiza kana cikin gamsuwa yace.

"masha Allah to adawo lafiya amma Rayyern ka kula da kanka sosai, ka daina sakaci akan cin abinci da kuma shan magani."

"To Abba."
Rayyern din ya fad'a atsanake, jin Abban ya kashe wayanne kuma, yasa shima ya zare wayar akan kunnensa,  tare da maida ita cikin aljihun rigarsa.
Gudun kada ya makara ne kuma yasanyashi, d'aukan  Briefcase d'insa ya fice daga cikin falon.

Koda ya fito waje motarsa ya shiga, cikin dan hanzari yayi mata key, tare da cillata kan titi kaitsaye ya nufi, babban hotel din da acikinsa zasuyi lecture din yau.

10:00 pm

Ahankali ta bud’e murfin kofar dakin nata ta fito, saidai kuma daddad’an k’amshin turarensa da ya gauraya da numfashinta ne, ya sata lumshe ido tare da shak’an wani sabon numfashi.

Ahankali kuma ta bud’e Idanunta tare da soma k’arewa falon kallo,  wanda komai na cikinsa tsab tsab yake.

Idanunta da suka sauk’a akan ledodin takeaway din dake kan table ne, ya sata karasowa cikin falon.

Sanin da tayi kuma cewar Rayyern din baya gidanne, yasa ta nemi waje anan cikin falon ta zauna, batare da ta damu da irin shigar dake jikinta ba.

Ahankali ta jawo ledodin takeaway din, abunda taga yayi mata ta d’anci kad’an, bayan ta kammala cin abincinne kuma, ta koma ta kwanta tare da lumshe Idanunta, tana me  sauraran wak’an film din Kalho Naho, dake tashi acikin babban tv’n dake falon.

Azahirin gaskiya wakan take saurare, saidai kuma amma abunda ke cikin zuciyarta daban yake, domin gaba daya tunaninta ya tafi ne izuwa ga rayuwarta.

Sau da yawan lokaci takan ji ta wata ta daban acikin wannan duniyar, takanji kanta amatsayin wata halitta wacce bata da gata, halittar da rayuwar ta ta kasance tamkar haja a kasuwa, ko kuma kwallo ta yanda kowa ke bugata yanda yake so.

Tabbas tasan k’addara na iya zuwarwa bawa, ayanda bai tsammata ba, amma ita tata k’addarar akullum da salon wasa da rayuwa take zuwar mata.

Kamar dai yanzu da take rayuwa awata duniyar ta daban, wanda babu iyayenta akusa da ita.

Ada ta fuskanci takura kad’aici da kuma tsangawa ma, awajen Yah Junaid, takanyi kuka sosai aduk sanda Junaid ya musgunawa rayuwarta, haka kuma takanyi  takaici da mamaki aduk sanda, yayi yunkurin kusanto da kansa gareta, ta sani cewar shidin Yayanta ne na jini, amma har yau tambayar da takeyi wa kanta shine, Meyasa Junaid din da ya kasance dan uwa agareta, ke kokarin keta haddinta akoda yaushe?

Ajiyar zuciya ta Dan sauke ahankali, cikin sanyi kuma tasa hannu ta sharce hawayen, daya gangaro ta gefen fuskarta.

Sakamakon tunawa da tayi cewar, ayanzu wata kalan rayuwa takeyi daban, cikin kuma k’addarar da ta d’aukota daga gidansu, ta raba ta da Mahaifinta, da kuma y’an uwanta.

K’addarar da ta kawota wannnan k’asar da take ganinta amatsayin sabuwar duniya.

Numfashi ta kuma fesarwa, tare da gyara kwanciyarta akan kujeran, ahankali ta kuma lumshe Idanunta.

Tana kwance ahaka da tunani kala kala, acikin zuciyarta bacci b'arawo ya d'auketa.

Acan b'angaren Rayyern kuwa tun 8:00 pm suke lecture, basu ne suka fito ba sai 1:00 am, nanma breaktime ne da suka samu, domin bayan sunci abinci zasu sake komawa wani lecture din.

Kasancewar kuma akwai musulmai da dama, acikinsu ne yasa sukayi amfani da breaktime din sukayi Sallan azahar, bayan sun idar da  sallan azahar dinne kuma, suka wuce cafe dan cin abinci.

Shidai bai wani ci abincin sosai ba, sai drinks  kawai da yasha kan Chocolate ɗinsa da yaci.

Kasancewar kuma agefen cafe din akwai, wani sasanyan furanni da swimming pool ne, yasa ko ina dake wajen ya d'auki sanyi, daga inda su Rayyern din ke zaune kuma, suna iya jiyo koke koken tsuntsayen dake shawagi awajen.

Saboda daddad'an sanyin dake ratsa sa ne, kuma yasa shi d'an lumshe idanunsa ahankali.

Wani irin yanayi yakejin kansa aciki, ma'ana yanayi mai kama da shauk'i, akaro na farko kuma acikin rayuwarsa daya fara tunanin wata mace.

“Naan! Naanu!!”

Ya maimaita sunan da take kiransa dashi, Yayinda acikin kunnuwansa kuwa, yakejin tamkar sautin muryar nata ne keyi masa gizo.

Idanunsa dake alumshe kuwa, salon shagwab'arta suke hasko masa, musamman yanda takeyi Idan tana magana, Ahankali yake ganin lips dinta na motsawa, Idan acikin fushi take kuwa, to lips din nata take turowa gaba, then saita dan karyar da wuyanta gefe.

Sassanyar Ajiyar zuciya ya sauke, ahankali kuma yake saurаran sautin bugun zuciyarsa dake tafiya kadan kadan, batare da ya ankara ko sanin abunda yakeyi ba, kuwa yaji heart din nasa tayi sanyi sosai.
Take kuma wani bakon yanayi  mai kama da farinciki, ya ziyarcesa.

D'an bud'e idanunsa yayi Ahankali, ya saukesu akan wasu kyawawan tsuntsaye dake shawagi asaman wasu fararen furanni wani yalwataccen murmushi ya subce masa.

“Rayyern.”

Dr. Sulaiman dake zaune agefensa ya kira sunansa, fuskarsa d'auke da mamaki saboda, wannan ne karo na farko aduk rayuwarsu, daya taba ganin Rayyern din ya nutsu yana tunani, wanda  da'alama kuma abu mai mahimmanci yake tunawa.

Jin sautin muryar Dr. Sulaiman acikin kunnuwansa ne, yasa shi juyowa batare kuma daya kalli Dr Sulaiman dinba yace.

“What happened?”

Idanu Dr. Sulaiman din ya zuba masa, saidai duk yanda yaso karantar yanayin Rayyern din bazai iya ba, saboda Miskiline na k'arshe, Dan kuwa gashi yanzu yanzun ya sanja mood din fuskarsa.

“What Happened?”
Rayyern din ya sake tambayar Dr. Sulaiman.

Jin hakanne kuma yasa Dr. Sulaiman girgiza kansa, cikin kuma kawar da tunanin dake ransa yace.

“No dama naga lokacin komawa lecture yayi ne.”

Agogon dake daure atsintsiyar hannunsa ya duba,  Ganin lokaci na tafiya ne ya sashi mikewa, batare kuma daya jira su Dr. Sulaiman din ba yayi gaba.

Kaitsaye hall din nasu duk suka  koma, tare da ci gaba dayin lecture.

Kamar kullum haka yau dinma 5:30 am dai-dai suka tashi daga lecture din, kasancewar kuma hazo ya bayyana agarin da kuma sanyi mai tsanani, shiyasa basu wani tsaya ba anatashi kowa ya kama hanyar masaukinsa.

Ahanyarsa ta dawowan ne kuma ya tsaya yayi musu takeaway, kamar dai yanda ya saba yi musu akowacce rana.

Cikin ikon Allah kuma yana isowa gida, aka fara yi musu ruwan dusan k'ank'ara.

Koda ya shigo cikin falon rigar suit d'insa da dusan k'ank'aran ya sauka akai ya cire, tare da ajiye ta akan kujera, Ahankali kuma yake karewa falon kallo.

Sauke idanunsa da yayi akan hulan Jannart din, dake yashe ak'asan carpet ne kuma, yasa shi fahimtar cewa ta d'an zauna afalon.

K'ofar d'akinta dake arufe gam ya kalla, kana cikin dan hanzari ya wuce d'akinsa, bayan ya ajiye ledan takeway din anan cikin falon.

Koda ya shiga bedroom kayan dake jikinsa ya rage, tare da daura towel akan waist d’insa, kaitsaye ya wuce bathroom yayi wanka had’e da d’auro alwala.

Koda ya fito daga toilet din har 6:20 tayi.

Ruwan dake jikinsa ya dan goggoge, bayan ya shafa mai ajikin nasa ne kuma, ya karasa gaban drawer’n sa, tare da ciro kayan da zai saka.

Kasancewar kuma ana sanyi sosai ne, ya sa shi saka wani dogon wandon jeans mai kauri, tare da long sleeve t shirt kana kuma ya daura babban sweater akan shigar tasa.

Bayan ya kammala kimtsa Kannasa ne kuma, ya d’auki key din motarsa ya fice.

Duk da cewar kuma har yanzu ba’a gama ruwan dusan kankaran ba, haka ya fita ya shiga mota zuwa masallaci, domin dama su y’an garin sun saba da irin yanayin.

Bayan an idar da sallan ne kuma ya zauna acikin masallacin, har saida akayi sallan Isha.

Wanda zuwa lokacin kuma sosai garin ya sake yin sanyi.
Hakanne ma yasa bai wani tsawaita addu’a ba ya nufo hanyar dawowa gida.

Duk da kuma cewar shidin yana cikin mota, amma hakan bai hanashi jin fitinannen sanyin dake tashi acikin garin ba.

Koda ya iso gida ko gama dai-dai-ta parking baiyi ba, da Dan sassarfa ya fito ya shige cikin falon.

Ajiyar zuciya ya dan sauke, kana ahankali kuma ya sauke idanunsa akan ledodin daya kawo, wanda suke nan kamar yanda ya ajiyesu, saboda babu alaman an tab’a.

Idanun nasa ya daga tare dakai dubansa izuwa kofarta.

Tsaida idanunsa akan kofar yayi baya ko kyaftawa, Yayinda shi kansa ya rasa me yake kallo, da tsammani.

Saidai kuma har acikin zuciyarsa abu d’aya yakeson sani, shine rashin cin abincin da baiga tayi ba,  wanda baisan dalili ba, cause kullum Idan ya kawo abincin kafun ya dawo daga masallaci yake Ganin taci nata.

Numfashi ya fesar kana ahankali kuma ya dauke idanunsa daga Kallon kofar nata,  batare kuma daya waiwayi abincin ba shima, kaitsaye ya wuce d’akinsa.

Koda ya shiga cikin dakin sweater din nasa ya cire,  bayan ya rage hasken wuta ne kuma, ya koma ya kwanta akan lallausan gadonsa.

Kamar yanda yake kwance akan gadon nasa kuwa, haka itama Jannart ke kwance, Yayinda ta kanannad'e Kanta acikin blanket.
Saboda sanyin da akeyi ne kuma yasa, tunda yamma da ta shigo cikin dakin bata sake fita ba.

Ko yanzu ma batajin zata fita saboda batajin yunwa, kasancewar taci abinci da rana sannan tasha fruits salat.

Atana kwancen kuma wayarta ce ke rike ahannunta,  tana Dan latsawa, game takeyi wanda da'alama kuma tana Jin dadin game din sosai.

Kasancewar ana sanyi sosai ne kuma, yasa tana rik'e da wayan ahaka har bacci ya dauketa batare da ta shirya masa ba.

*Rayyern.*

Ajiyar zuciya mai k'arfi ya kuma sauk'ewa akaro na barkatai,  kana cikin dan yanayin kasalan da yakejin kansa aciki ya lumshe idanunsa.

Ahankali yakejin mood d'insa na sanjawa, ga kuma tsikar jikinsa da yakejin yana tashi.

Sannu ahankali kuma idanunsa dake lumshe, suka soma yi masa imagining nata,  wanda hakan yasa take duk wata gab'a dake jikinsa ta amsa.

Ahankali yake tuno moment dinsu, da kuma yanda ta saka hannunta akan saman mararsa tana shafawa, Yayinda yan yatsun hannu, da kuma dumin tafin hannun nata ke ratsa cikin Dick d'in sa.

Da sauri ya bud'e idanunsa, saboda wani irin zubawa da yaji tsikar jikinsa nayi ya rasa wannan wanne irin masifeffen tunani ne da ki barinsa ya huta domin kusan kullum sai ya tuna wannan yanayin.

Daga gefe guda kuwa ga numfashinsa, da yakejin yana kokarin kwacewa,  wanda hakan yasa awahalce ya fusgo numfashin nasa.

Saidai kuma jin yanda mararsa ke motsawa ne, ya sashi saurin d'aura hannunsa, ya danne saman marar.

"Yah Salam."

Ya fad'i haka yana me rumtse idanunsa, tare da cizon lips d'insa, saboda dick d'insa dake amsawa.

Domin haka yakejin tamkar yanzu ne abun ke faruwa,  dalilin hakanne kuma yasa shi, soma motsa hannunsa dake kan saman marar nasa.

Ahankali yake shafawa tare da maida idanunsa ya lumshe.

Almost 17mn
Ya soma sauke wani irin
Breath mai kama da sexual erection sound, duk da ba masturbation yayi ba, amma sai yaji numfashinsa na fusga kaman zai kwace,  Yayinda duk jikinsa kuwa ya d'auki rawa da karkarwa.

Alaman tafiyan hannunta akan saman marar tasa kawai yakeji,  da sauri ya juya tare da kifa kansa acikin pillow.

Numfar fashi ya dinga saukewa akai akai, yana ahaka har bacci ya daukesa.

*Washegari*

Duk yau din haka ya tashi yana jin jikinsa wani iri, kasancewar Sam wannan moment din ya kasa barin cikin Brain d'insa.

Ahaka dai ya shirya ya wuce wajen lecture, bayan ya saka ankawo abinci kamar kowacce rana.

Still yauma bai wani ci abincin sosai ba magani kawai yasha ya kama hanyarsa ya tafi.

Jin alamun fitansa ne kuma yasa Jannart fitowa falon, abincin daya rage ta dauka taci, bayan ta tattare wajenne kuma ta dawo ta kunna kallo.

Haka dai tayi ta zama ita kadai, ba ita takoma d'akinta ba kuma har saida aka soma kiraye kirayen sallan magriba.

Shikuwa Rayyern ranan bai dawo gidan ba, saida yayi sallan Isha, still da takeaway ya dawo, bayan yaci nasa abincin ne kuma ya wuce d'akinsa.

Kasancewar yau din ya gaji sosai shiyasa, yana kwanciya bacci ya daukesa.

Jannart kuwa sai wajajen 9 ta fito taci abincin, bayan ta kammala kuma itama ta koma d'akinta.

*** **

*After 5days*

Da sannu rayuwa ta koma musu irin Wacce sukeyi Ada, saboda tun ranan da ya shigo dakin nata,  acikinsu babu wanda ya sake Ganin Dan uwansa har zuwa yau.
Sai dai akwai gagarun banbanci domin a yanzu wuni yakeyi tunaninta kamar zai zautar dashi, taurin kai kuma da kafiya ya hanashi yin mubaya'a.

Saidai akowacce rana yana ajiye mata abinci,  kamar yanda ta saba kuwa takan ci abincin, sauran ragowan kuwa sai ta kaishi kitchine.

Kasancewar kuma ranan yau ta kasance, Wednesday shiyasa su Rayyern din suka tashi da wuri.

Bayan ya biya restaurant ya saya musu abinci ne kuma, kaitsaye ya dawo gidan.

Yana shiga bedroom d’insa kuwa kiran Mamynsa na shigowa.

Adan kasalance ya d’aga wayar, kana cikin shagwab’a yace.

“Mamy barka da yamma.”

“Yauwa Rayyern barka dai ya jikin naka? duk dama naji Jananrt tace min yanzu kam ka warware.”

Mamyn ta fad’i haka cikin sakin rai, da kuma nuna kulawa agaresa.

Shikuwa jin abunda Mamyn ta fad’ane ya sashi, narkewa kamar karamin yaro yace.

“Mamy nifa nayi sauki sosai, Ina Ramadan da Baba Maud’o, Allah Mamy nayi kewar Baba Maud’o sosai, duk da cewar muna waya amma sai nakejin kewarsa sosai.”

Ajiyar zuciya Mamyn ta sauke, cikin kuma danne abunda ke cikin zuciyarta tace.

“Baba Maud’o yana lafiya Rayyern, wato mu baka kewar ganinmu sai shi ko.”

Murmushi ya d’anyi, kana Cikin kwantar da murya yace.

“A'a ba haka nake nufi ba Mamy.”

Itama Mamyn Murmushi tayi, Cikin kulawa kuma tace.

“Ka huta gajiya zamuyi waya anjima, dama na kira na sakejin ya lafiyar jikin naka ne.”

Kansa ya dan jinjina tare da cewa.

“To Mamy.”
Jin ta kashe wayarne kuma yasa shi. Dan lumshe ido, abayyane kuma cikin sanyin murya da alamun kamar fushi da shagaɓa yace.

“Almost 6days kenan bata ganni ba kuma bata nemeni ba, amma wai har ta iya fadawa kowa cewar na samu lafiya, bayan ko zuwa dubani ma batayi like tana fushi dani, kuma ni dai nasan ba abinda na mata, shagwab’abb’iya da wani d’an k’aramin bakinta awajen,."
Numfashi ya ɗan fesar tare da lumsh ido a fili yace.
 “Now da zan kwanta ciwo sai tafi kowa rudewa a duniya,  she’s saying Naan! Hamma Naanu!! Please Naan karka mutu, Dan Allah Naan ka bude idanunka,  wayyo Allah Ka taimakeni Naanuna!!!.”

Ya kare maganan cikin kwaikwayon maganan Jannart din.
Saboda har yanzu tana yi masa gizo acikin idanunsa.
Murmushi yayi shi dayansa.
Ahankali ya ajiye wayar tasa tare da wucewa toilet kaitsaye.

Jannart kuwa Acan d’akinta zaune take agaban dressing mirror, Yayinda jikinta ke sanye da bathrobe da alama kuma fitowarta daga wanka kenan.

Duk da cewar kuma ta gama kimtsa kanta, amma bata saka kaya ba.
Yar karamar wayarsa dake hannunta ta soma jujjuyawa, Yayinda acikin ranta take tunanin kiran Aunty Fauziya, saboda ba kadan ba tayi kewar matar.

Wayarta kiran iphone ta dauka tare da kunnawa, ta kwafi numbern Aunty Fauziyan, acikin karamar wayar tasa tare kuma dayin dialing call din.

Aunty fauziya dake zaune kuwa, Ganin kira ya shigo wayanta ne ya sata, duba screen din wayar new number , kuma ta k’asar Russia da ta ganine yasa, atakeyi tayi tunanin ko Jannart ne, hakan yasa ta d’aga da sauri, tare da kara wayan akan kunnenta.

Jannart dake zaune kuwa jin Aunty Fauziyan tayi picking call dinne, yasa tayi murmushi cikin sakin rai tace.

“Nayi kewarku sosai My Aunty.”

Murmushi itama Aunty Fauziyan tayi, cikin kuma jin dadin kiranta da Jannart din tayi tace.

“Wallahi Jannart muma munyi kewarki sosai, ya kuke keda mijin naki ya Mascow?”

“Alhamdulillah Aunty, duk muna lafiya yasu twins, da kuma mutanen wajen aiki, Allah duk nayi kewarsu inajin kaman na dawo.”

Jannart din ta fadi haka cikin sanyin murya.

Hakanne ko yasa Aunty Fauziyan sakin murmushi, cike da kulawa kuma tace.

“Haba Jannart keda kike tare da mijinki, Ina ke Ina wani kewar abokanan aiki, ai ki manta da wasu abokanan aiki kawai ki saurari mijinki, Kodai yanzun ma yana kusa ne?”

Kai ta d’an girgiza cikin sanyin murya kuma tace.

“A’a baya kusa, ya fita tun safe, amma bansani ba ko ya dawo.”

Ta kare maganan in don’t care manner, wanda hakan ke nuna kwata kwata batasan, kula da dawowarsa ko kuma fitansa ba.

“Jannart.”
Aunty Fauziyan D Sulaiman  ta kira sunanta cikin yanayin mamaki, kana bata jira ta amsa ta ba tace.

“Bakisan lokacin dawowan mijinki ba Jannart Why, Kodai kun samu matsala dashi ne?”

Shiru Jannart din tayi tare kuma da sunkuyar da kanta k’asa, saboda batasan me zata fad’awa Aunty Fauziyan ba.

“Jannart tambayanki nake ba kodai kun samu miss understanding ne, tell me karki damu saboda akowanni zaman aure, ana samun irin haka Dan haka karki boyemin komai.”

Ajiyar zuciya ta d’an sauke jin hakanne kuma ya sata, langwabar dakai cikin sanyin murya tace.

“A’a My Aunty ba fad’a mukayi ba, nida yau kwana na 6 ban sashi a idanuna ba tayaya zamuyi fad’a, Allah Aunty ba muyi fad’a ba.”

Baki Aunty Fauziya ta sake, cikin kuma mamakin abunda Jannart  din ta fad’a tace.

“Subahanallah, Haba Jannart ya zaki wofantar da mijinki haka, har tsawon kwana 6 batare da kinsan halin da yake ciki ba? kinsan me hakan da kika aikata yake nufi kuwa? you mean bakya kulawa da mijinki why, Meyasa Jannart bayan kuma kinsan yana da hakki akanki, Koda ace anyi auren naku ne acikin wani irin yanayi, amma shidin mijinki ne kuma yana da hakki akanki, Kodai bakisan da hakan ba?”.

Aunty Fauziyan ta tambaya cikin dan yanayin damuwa.

Jannart kuwa Kanta ta sadda k’asa, tare da soma wasa da hannunta, cikin sanyin murya tace.

“To ni Aunty....”

“To keme Jannart baki da wani excuse din da zaki bani, indai akan kulawa da mijinki ne, Meyasa zaki bari rayuwar aurenku ta zama haka? Wallahi ba haka ake rayuwar aure ba Jannart, mijinki mijinki ne ako ya yake, sannan shine komai naki ahalin yanzu, babu kuma wanda ya fisa kusan ci dake, haka kuma Aljannarki tana karkashin kafarsa, To meyasa kikeson yin wasa da damarki?”

Shiru Jannart din tayi saboda, bata da wani kalma da zata fada, wanda Aunty Fauziyan zata fahimta.

Aunty Fauziya kuwa sanin halin Jannart din, na sanyin rai da tayi ne yasa ta cigaba da cewa.

“Baki kyauta ba Jannart, Sam bai dace ba ace kin bar mijinki, har tsawon 6days babu kulawarki, kenan babu wani hakkinsa ko daya dake kanki, da kika sauke, na farko bakya zuwa Koda gaishesa ne, balle kuma ki dafa masa abinci ki basa yaci, kuma yau koda ace shi yayi miki laifi, kece akasansa saboda haka wajibi ne, ki basa hakuri kodan neman zaman lafiya, sannan duk wata macen kirki bata raba muhalli da Mijinta Jannart, bakyau Mace ta kauracewa mijinta, domin yin hakan kan jawo mata tsinuwa awajen mala’ikun Allah, me yasa to ke kikeson kasancewa a haka? Jannart miji fa ya wuce wasa, matsayinsa yana da girma sosai, kinyi ilimin boko dana addini ɗan dai-dai, kinsan komai kanki awaye yake, Meyasa bazaki zauna ki kula da mijinki ba, bacin kinsan cewar ak’asan da kuke, babu wani naku ku kad’ai kuke rayuwa, wanda kuma dole kuna da buk’atar kulawan juna, Dan Allah Jannart ki kula da mijinki kinji.”

Aunty Fauziyan ta k’are maganan cikin tausasawa, saboda tasani dole wani abun sai ta hanyar tausasawa ne, Jannart din zata fahimta, domin ba komaine za ace mutum ya sani ba, more especially kamar ita Jannart da ta taso, babu takamammen wanda zai kula da ita, babu wanda zai nusar da ita ya koya mata yanda ake zaman aure.

“Jannart.”
Aunty Fauziyan ta kuma kiran sunanta akaro na uku.

Asanyaye Jannart din ta amsa mata, kana cikin dan raunin murya tace.

“Naji Aunty Insha Allah zan kiyaye.”

Ajiyar zuciya Aunty Fauziyan ta sauke, tare da kara sassauta muryarta, kana cikin son bata karfin guiwa tace.

“Duk da nasan bawai auren soyayya kukayi ba Jannart, amma ki sani kulawa yana da matukar muhimmaci, sannan kyuatatawa na jawo soyayya, Koda kuwa ga makiyinka ne idan ka kyautata masa, sai yaji dadi aransa Koda kuwa bazai bud’e baki ya fada ba, balle kuma ace mijinki na aure, shine wanda ya kamata ace kin kyautatawa fiye da kowa, ki duba irin mijin da Allah ya

baki Jannart, bawai gama garin miji bane, mijine irin na nunawa sa'a, karki damu Koda ace shi bai baki kulawa ba, domin kece zaki nuna masa hakan,  kece zaki fara har shima ya dauka, please Jannart ki kula da mijinki dan Allah, saboda ayanzu baki da wanda ya fishi, kar na sakejin haka cewar kinbar mijinki babu kulawa, bakisan ci da shansa ba, bakisan ki sauke masa hakkinsa dake kanki ba, ki gyara karki sakeyin haka saboda miji ba abun wofantarwa bane."

Idanunta da suka ciko da hawaye ta d'an lumshe, Ahankali kuma Cikin sanyin murya tace.

"Kiyi hakuri Aunty Fauziya Insha Allah zan gyara."

Ajiyar zuciya Aunty Fauziyan ta sauk'e, tare da cewa.

"Shikenan yanzu kije ki kula da mijinki, sannan ako da yaushe ki kasance mai yawan ado, duk da nasanki da son ado, amma dole zan kara nana ta miki, Jannart ki kula da mijiki sosai, sannan kibar duk abunda kikeyi yanzu kije garesa, saboda na tabbatar cewa shima yana da buk'atar ki, Koda kuwa bazai bayyana hakan ba na sani tabbas yana bukatar ki kusa dashi yana kuma son ganinki Koda bai faɗa mikiba,  nasan yana mararin ganinki akusa dashi, ajiye wayan ki tafi maza."

Aunty Fauziyan ta kare maganan cikin serious.

"To."
Jannart din tace tare da zare wayan akunnenta, ahankali ta Dan murza Idanunta wanda suke dauke da hawaye.

Cikin sanyin yanayi da kuma mutuwar da jikinta yayi, ta karasa gaban drawern ta.

Wani doguwar riga marar nauyi ta ciro, tare da zurasa ajikinta, kasancewar kuma rigar bata da wadataccen fadi ne, yasa duk wani surar jikinta bayyana.
Musamman breast dinta wanda suka tashi suka tsaya, tamkar zasu tsone idon mai kallonsu.

Bayan ta zura rigar ajikinta ne kuma, ta saka hulan sanyi mai dan kauri akanta, tare da daukan wani boyfriend jacket marar nauyi ta daura akan kayan nata, saboda ayanda surar jikinta ya bayyana sosai, kunya bazai barta taje garesa ahaka ba.

Bayan ta fesa turaren oud ajikinta ne kuma, ta zura wasu takalma masu laushi ak'afafunta.

Babban wayar nata ta d'auka, Cikin nutsuwa da kuma tarin fad'uwar gaban da takeji, ta bud'e kofar dakin nata ta fice.

Yayinda acikin zuciyarta kuwa, take fargaban ace kowacce rana mala'ikun Allah tsine mata sukeyi.

Ahankali take k'arewa falon nasu kallo, Ganin ledodin restaurant da tayi akan table ne kuma, ya tabbatar mata da cewar ya dawo.
Saidai rashin ganinsa acikin falon yasa, ahankali takai dubanta jikin kofar d'akinsa.

Idanunta ta d'an lumshe ahankali, tare da hadiyan wani yawu daya tsaya mata amakoshi.

Acikin zuciyarta yake tunanin tsayawa ta jira fitowarsa, amma kuma tuna maganganun da Aunty Fauziyan ta gaya mata, yasa asanyaye ta nufi kofar dakin nasa.

Dai-dai lokacin shi kuwa Rayyern wanda ya sakeyin wanka, inda ya shirya kansa cikin wani lallausan yadi, wanda akayi masa dinkin riga da wando, ma'ana dai dinkin hausawa,  Kayan yayi masa kyau sosai.
Musamman da rigar ta kasance half jumper, tun zuwansu Mascow din kuma, wannan ne karo na farko, da ya saka kayan gargajiya.

Wayarsa dake kan gado ya d'auka, kasancewar kuma yunwa yakeji ne, yasa shi nufar hanyar fita daga d'akin.

Dai-dai yazo bakin kofar fita daga dakin, ita kuma Jannart ta daura hannunta akan handle din kofar, tare da turowa ahankali kuma batare da ta jira ba, ta sako k'afarta na dama cikin d'akin.

Karab sukayi karo da juna, Yayinda lallausan takalmin gashin kuliyan, dake k'afarta ya taka nasa k'afar.

Da sauri duk suka d'aga idanu Ahankali suka kalli junansu.
Kallo mai dauke da sakonni daban daban masu kashe zuciya.

Yayinda Rayyern kuwa Kallon cikin idanunta da yayi, yasa shi jin wani abu ya tsarga tun daga tafin k'afarsa, har izuwa gadon bayansa.

Tamkar wanda aka sawa maganadisu kuwa, haka yaji duk tsikar jikinsa na tashi, wanda sanadiyar hakan yasa shi sauke sassanyar Ajiyar zuciya.

Ahankali kuma Cikin wani irin bak'on yanayi, ya dan karyar da wuyansa, tare da zuba mata narkakkun idanuwansa, wanda lokaci daya suka soma sanja launi.

Jannart kuwa Ganin irin Kallon nasa da yakeyi mata ne, yasa ta lumshe Idanunta ahankali, tare kuma da shak'an daddad'an k'amshin dake fita ajikinsa.

Akasalance kuma Cikin salon shagwab'arta, da cool wanda ke narkar dashi tace.

"Naan Ina kwana..."

Idanunsa ya lumshe tare da fesar da wani irin numfashi, saboda saukar muryarta acikin kunnuwansa, yasa shi jin wani irin feeling.

Ahankali ya juya narkakkun idanunsa, wanda suke gab da rufewa, saboda mayen sha'awa, Cikin yanayin da yakejin kansa kuma ya dan matso kusa da ita, tare da bud'e bakinsa ahankali, in a golding voice yace.
"Hyhuuuuum". Sai kuma ya tsareta da maratattun idanunsa kana a hankali yasa hannunsa na hagu kan gefen kofar ta ciki.
Kana, kana hannunsa na dama kuma gyara riƙon da yayiwa chocolate ɗinsa yayi tare da bata ɗaya kana ya riƙe ɗaya ɗaura hannun yayi ya tokareshi ta woje ya zama tana tsakiyar hannayensa.
Wani irin maraitaccen numfashin yaja mai tafiya da nitsuwar jiki da zuciya.
kana ya feso mata sassayan iskar bakinsa bisa fuskarta wanda hakan ya sakar mata wata iriyar fitinenneyar kasalar datasa lumshe kwayar idanunta a hankali tare fara sauƙe numfashi kusancin su dake barazar fasa mata zuciya.
shi kuwa Dr Rayyern a hankali ya buɗe maraitattun kuma narkakkun idanunsa da sukafi kama dana ɗan codding yayi kana a hankali ya kuma matsota har ƙirjinsa na danne nata ƙirjin da tuni jikinta ya fara karkarwa.
Wata iriyar fitinenneyar kasala mai tafiya da nitsuwar jiki da kwalwace ta dirar masa, a hankali yayi ɗan sunkuyo kansa saitin fuskarta, cikin wani irin baƙon yanayi da bin umarnin zuciyarsa ya zaro tattausan tong ɗinsa wani irin yar-yar suka ji a lokacin ɗaya, dai lokacin daya sauƙe harshensa kan tsinin karan hanc...!

*Albishirinku! Ma'aurata, GA GARKUWAR KU nan tafe muku da tsarabobi na musamman gareku ma'aurata daga cibiyar mgnin mata mai taken  GARKUWAR MA'AURATA*

NI DAI AYSHA ALIYU GARKUWA.
Ina matukar mamakin wani irin lokaci da ya riske mu mai wahalallan fassara. Kullum dai magana daya ce, akan ma'aurata, fada, rashin jituwa, mutuwar aure, akan kuskure kalilan, rashin kula, rashin yi wa juna uziri. Toh wai duk me ya janyo hakan? Na zurfafa a tsananin tunani hakan ya tilasta min bincike mai tarin yawa wanda ya kai ni ga gano inda matsalar take? Shin yar'uwa ke macece amma kin san wacece mace ku? Kin san me ake kira mace kuwa? Mace ita ce matar da take zama iyali a wajan namiji ta zame masa bango, sanyin idaniyarsa, ta zame masa gata da farin cikin rayuwarsa ta zame masa ruwa abar kore ƙishinsa ta zame masa mayafi mai karesa daga gigitar kadaice, ta kuma dorar da mijinta kan turbar gaskiya, ta kashe masa jiki da salonta ta rikita shi da baiwa da ni'imar da Allah ya bata idan har ta san hanyar mayar da kanta sabuwa dal awajanta, wato kullun takasance masa tamkar amarya har ya kasa tantance daren amarcinsu da sauran dararen rakun rayuwar su.

Wannan ita ce mace. Ina da wata saukakkar hanyar da zaki zama abar so da kulawa da soyayya a wajan mijinki ta hanya mafi sauki, 09097853276 hanyar ita ce ki gwada amfani da kayana na gyara ki gani, ina mai tabbatar miki da in sha Allahu sai kin dara da murna sai kuma

kin gode min. Kayana kaya ne da aka yi shi da zallan itacanmu na gado marasa illa a cikin jikin dan adam musamman mace, kaya ne da suke taimakawa (sex hormones 😍) dinki.
Misali kina kallon India😘, hollywood, Asian film🥰 kina ganin yanda mazansu ke nunawa matansu tsananin soyayya kamar su ba su kyautar ransu!?
Saboda me hakan? Saboda suna sadaukar da lokacinsu wajan gyara jikinsu da kayan da ke tsattsafo da ni'ima cike da tsukewa, kayan nan kuma ana yinsu ne zallar magungunan gargajiya wanda ba su da illa domin hadine na ingantattun itatuwa da yayansu.
Ina baiwar Allahn da miji ke daure mata fuska babu hirar arziki?
Zo ki ji yar'uwa zan baki gumbata da zallar gari wanda aka yi su da nagartattun itacen da ke da matukar amfani a jikin mace. Gubar ciko, gumbar tsalle dole, gubar da ba'a baiwa mai kishiya, garin maɗi, garin mallaka, tsumin goron tula, tsumin tsartai, tsumin maratsi, pala-pala butar sirri, kwanon k'asaitacciyar mace, furar mata madararta gareki Hajia takenta sha yanzu mgni yanzu,
Ina mata masu fama da sanyi? Sanyin mara ki zo na hadaki da magani na na sanyi wanda yake wanke mara ya fitar da duk wata cuta da ke samun mazauni a wajan.
Ina da ciccibi mai kyau. Ina da hadin amare mai kyau wanda zai gyara yarinya ya kankaro mata kimarta akwai hadin mai jego wanda muke yinsa na asali inada kekkyawan Hadi maida tsohuwa yarinya.

Akwai daya bangaren wato *KAMSHI*
Kimarki gyaranki da kamshinki. Matan da suka gane suka san yanda za su kankaro da mutunci su ne masu amfani da kayan gyara da kuma sanyaya jikinsu da kamshi, ina da turaren wanka da na bandaki na daki na jiki da na kaya dana tsuguno kamshin turarena na dabam ne mai sanyaya zuciyar wanda ya shaka ina da kayan kamshi na amarya da na maijego da na uwargida da dukkan macen da take kokarin mayar da kanta mai daraja a idon kowa ta zamo sarauni a idon mijinta, akwai shu'umar humra, sayan na gari maida kuɗi gida, banda karanta yayin gyara Hajia.

Zaku iya samun kayyakina a duk garin da kike, zakiyi min mgn ta whatsApp number na 09097853276 domin yin zaɓinki, ko karin bayani, zaki tura kuɗin ta account na 0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU in mun gama mgna zan sa miki kaya a mota yazo duk garin da kike, in baki shirya saya yanzuba Please kada mu wahal da juna ki bari sai kin shirya kafin kiyi min mgn.

🤝🥰😘 Daga taku AYSHA ALIYU GARKUWA
*(GARKUWAR MA'AURATA)*

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:56 - 🥰🥰: Wani irin maraitaccen numfashin suka ja kana suka sauƙe a tare, Kerma da kerketa jikin Jannart ya fara wanda yasa ta fara kokawa da nnumfashindake gab da barin gaggan jikinta.
Shi kuwa Rayyern wani amintaccen lasa yayiwa tsinin hancinta, kana a hankali ya kauda

fuskarsa gefe kaɗan ya manna lips ɗinshi gefen kuncinta.
Tare da fara ƙoƙarin buɗe narkakkun idanunsa,
da sauri ya ɗan janye jikinsa baya kaɗan ganin yadda hawaye ke kwaranya a fuskarta wani na korar wani, tsoro da firgicin data faɗa ya bayyana ƙarara.

A hankali a kuma jere ya fara sauƙe numfarfashi.
Fuskanshi ya kauda gefe tare da taune laɓensa na ƙasa.
“Lfy lau.”
Yayi maganan cikin wani irin yanayi mai wahalar fassaruwa, tare kuma da zuba mata narkakkun idanunsa, way’anda suka haifar mata da kasala, lokaci daya kuma tsikar jikinta suka shiga mimmik’ewa.

Kasancewar ba zata iya jurewa Kallon cikin idanunsa bane kuma, yasa ahankali tayi kasa da kanta, tare kuma da fesar da wani irin numfashin da ta samu ya dai-dai-ta fitar numfashin ta, yayinda mamakinsa ke ratsata ganin yadda ya wani basar kamar ba shiba.

Duk sai taji ya cika mata idanu, Yayinda yayi mata kwarjini na gasken gaske, sanadiyar kayan dake jikinsa, way’anda sukayi matuk’ar yi masa kyau da tsare fuska da yayi yana mai lasan Chocolate din hannunsa.

Shikuwa Rayyern dake tsaye har yanzu kallonta yakeyi, baya ko k’yafta idanunsa dake kokarin lumshewa, sosai  yakejin wani irin abu na musamman na yawo acikin jikinsa wata iriyar fitinenneyar kasala yakeji tana lullubeshi lasan Chocolate ɗinsa yake tamkar zan cinye da ledan.

K’amshin jikinta dake ratsa cikin hancinsa ne kuma, ke kara kashe masa jiki, tare da narkar masa da zuciya.

Ahankali batare kuma da ta d’ago ta kalleshi ba, Cikin sanyin murya tace.

“Abbana yace na gaisheka.”

“Uhummm ngd.”
Ya fad’a kasa-kasa tare kuma da, ci gaba da tsare ta da idanunsa, yana meyi mata wani irin kallo, mai dauke da abubuwa daban-daban kana yana jujjuya tsinin harcensa akan Chocolatinsa.

Kallon da yasa duk takejin kanta arikice, haka kuma Kallon da yasa kirjinta soma bugawa da sauri-sauri.

Yayinda acikin zuciyarta kuwa  so take ta janye jikinta baya, daga kusancin da suka samu ita da shid’in, amma kuma kwata-kwata ta kasa yin hakan.
Saboda hakanan taji batason yin nesa, da k’amshin turarensa wanda yake gauraya da

numfashinta.

Idanunta ta kuma lumshewa, saboda jiyo sautin bugun zuciyarsa da tayi ne kuma, yasa ahankali tace.

“Kaci abinci?”

Yanayin yanda tayi maganan da rauni ne, yasa shi kasa amsa mata, saima idanunsa daya lumshe tare da karyar da wuyansa gefe sabida wani irin fitinennen abu da yaji yana rufeshi.

Jannart kuwa jin bai amsa mata bane yasa asanyaye ta sake cewa.

“Kaci abinci?”

Again shiru yayi bai amsa taba, saidai kuma ya bud’e idanunsa, inda ya zubawa kyawawan lips dinta idanu.

Itakuwa jin yayi shiru akaro na biyu ne, yasa ahankali ta d’ago Kanta ta kalleshi.
Hakan kuwa shi yasa idanunsu sarkewa dana juna.

Tamkar Wacce aka jonawa shokin haka taji jikinta, saboda Kallon nasa da tayi, duk da hakan kuwa da taji baisa ta iya janye Idanunta daga cikin narkakkun idanun nasa ba.

Saima kwaɓe fuska da tayi, tare da dan yin rau-rau da idanunta da suke fidda sheƙi na musamman alamun hawaye na tsastsafo wa, cikin yanayin kula mai had’e da rauni murya a sanyaye tace.

“To ba Inata maka magana kuma kayi shiru ba, Kaci abinci?”

Ta kai karshen maganan tana me Kallon, faffad’an chest d’insa, kasancewar bai ida sa aninayen gaban rigar duka bane, kuma yasa take iya hango hasken fatan kirjin nasa.

“Naan..”
Ta kuma kiran sunansa a dan tsorace, saboda kasa amsa mata da taga yayi sai take zaton ko ciwon ne, kana idanunta nuna mata suke kamar bai fidda numfashin ma, Shi kuwa Rayyern gaba ɗaya azabebbiyar kasala da bakon yanayi yakeji yana kashe dukkanin sassan jikinsa gaba ɗaya, haka yasa yake jin lips ɗinsa sun masa nauyi bare ya iya amsa mata, saima kallonta da yake tamkar yaga bakuwar halitta.

Idanun nasa dake kallonta ya rufe tare da fesar da numfashi lokacin da yaga hawayen idanunta sun kwaranyo, shi kadai yasan me yakeji aduk sanda tayi masa magana, da muryar rauni mai haɗe da shagwab’ar da ita batama san tanayiba, ba a iya jikinsa kawai ba, har dick d’insa motsawa take, yakanji sa awani yanayi na daban.

Labb’an bakinsa ya dan motsa kana ahankali yace.

“Baki banibaaa.”

Yanayin yanda taji sautin muryar tasa ne, kuma yasa ta d’agowa ta kalleshi.

Shikuwa batare daya bata daman ganin cikin idanunsa ba, ya d’an rab’a ta gefenta ya  fita zuwa falo yana mai tafiya cike da kasala.

Bayansa tabi da kallo, kana ahankali itama ta rufa masa baya,  Ganin ya zauna akan kujera ne kuma yasa ta wucewa kitchine.

Plate ta dauka tare da wani cup, wanda ta tari ruwan zafi acikinsa ta dispenser, bayan ta saka ruwan zafi acikin cup dinne kuma, ta bud’e roban zuma ta d’an zuba mai d’an dama aciki.

Bayan ta kammala ne kuma ta dawo falon hannunta rik’e da plate da kuma cup din ruwan zafi da zumar.

Yana nan zaune a inda tabarsa, saidai idanunsa alumshe suke, Yayinda ya daura kafafunsa akan table kana ya jingina kansa saman kujera.

K’arasowa inda yake din tayi, hade da durk’usawa ta zauna akan k’afafunta.
Spoon din dake cikin cup din ta dan motsa, kana ahankali kuma ta d’ago Kai ta kalleshi.

“Naan.”
Ta kira sunansa cikin tausasa murya.

Kanshi ya d’ago ya fuskanceta, tare da fesar da sassayan numfashin lumsassun idanunsa ya bud’e tare da sauke su akanta.
Itakuwa Ganin hakanne yasa ta miko masa, cup din tare dayi masa alama akan yasha.

Cup din da kuma y’an yatsun hannunta dake rike dashi, ya kalla kana ahankali ya kuma dawo da kallonsa gareta, saidai ayanzu Kallon da yake mata, ya banbanta da sauran, domin kallone mai dauke da alamar tambaya.

Fahimtar abunda yake nufi ne kuma yasa ta, kwantar da kanta asanyaye tace.

“Take it please zai taimaka wajen, rage maka ciwon ciki, kuma Abbana ne yace kana sha saboda yana magananin ciwon ciki.”

Ta kai karshen maganan tana me sake miko masa cup din.

Shikam idanu kawai ya zuba mata, aransa yana me mamakin wai, black tea ne zai rage masa ciwon ciki hmmm dan baisan da zuma a cikiba.

“Naan kasha mana please.”
Ta yi maganan saboda ganin har yanzu ita yake kallo.

Ahankali yasa hannu ya karb’i cup din, akokarinta na sakar masa cup dinne kuma, hannunsu ya hade awaje daya.
Da sauri ta zare nata hannun saboda koyaya, Idan wani sashi na daga jikinsa ya taba ta.
To haka zatana jin tsikar jikinta na tashi.

Plate din da ta kawo din ta dauka, tare da bud’e ledan Sabor de la vidda restaurant din daya kawo, ta zuba masa abincin acikin plate, hade da kawo masa gabansa ta ajiye, Ahankali kuma ta d’ago ta kalleshi.

Ganin idanunsa ba’a kanta suke bane, yasa ta komawa tadan zauna akasa kusa dashi, tare da zubawa yatsun k’afarsa idanu.

Duk abunda takeyi din kuma yana kallonta ta gefen idanunsa, Yayinda ahankali kuma yake sipping black tea din da takawo masa wanda yaji zaƙin zumar ya mishi daɗi toh dama ya Rayyern da zak’i.
Kasancewar tea din baida yawa, shiyasa in a few minute ya shanye, tare da ajiye cup din.

Ahankali ya dan kalleta ta gefen ido, tare kuma da daukan spoon ya soma cin abincin da ta ajiye masa.

Daga gefe guda kuwa anutse yake karewa, shigar dake jikinta kallo, musamman yanda dogon gashinta ya kwanta akan gadon bayanta.
Y’an yatsun hannunta da ta d’aura akan, carpet ya kalla kana ahankali kuma ya janye plate din abincin daga gabansa.

Kasancewar kuma tana Dan yawan satan kallonsa, shiyasa ganin ya ture plate din abincin gefe, yasa ta daukan sachet din maganinsa, dake kan table ta b’are magungunan tare da mik’a masa.

Babu musu kuwa ya karb’a hade da zuba, k’wayan maganin abakinsa, kana ya bi da ruwa.

Agogon dake daure atsintsiyar hannunsa ya kalla, Ganin 5:00 dai-dai ne kuma yasa shi mikewa tsaye, tare dasa hannu ya gyara aninayen gaban rigarsa.

Ganin hakanne kuma yasa ta d’ago, da kanta ta kalleshi cikin tausasa murya tace.

“Fita zakayi ne?”

Kansa ya gyad’a mata alaman “Eh.”
Batare kuma daya juyo ba ya nufi hanyar fita daga falon.

Itakuwa Jannart bayansa tabi da idanu, cikin sanyi hade kuma da tausasa murya tace.

“Adawo lafiya Allah Ya tsare.”

Saboda jin abunda ta fad’a d’inne kuma, ya sashi tsayawa da tafiyan nasa, Ahankali ya juyo ya sauke idanunsa akanta.
Domin Wannan shine karo na farko, da yaji tayi masa addu’a alokacin da zai fita.

Idanunsa ya lumshe tare kuma da sauke ajiyar zuciya, cikin kuma wani irin yanayin daya samu kansa ya amsa mata da.
“Amin.”
Kaitsaye kuma ya fice daga cikin falon, yana me Dan kad’a car key din dake hannunsa.

Jannart kuwa harsai da ya fice sannan ta janye Idanunta, daga kansa Ahankali ta sauke ajiyar zuciya, tare da jawo plate din abincin daya rage ta soma ci.

Hakanan duk sai takejin kanta wani iri, saboda nasihan da Aunty Fauziya D Sulaiman din tayi mata.
Wanda Ada ko sau daya bata tab’a jin, cewar ba akan dai-dai take ba, kasancewar batasan ya rayuwar aure yake ba, akullum kawai tana rayuwa ne kamar yanda, Rayyyern din ya nuna mata, rashin kulasa da kuma rashin shiga sabgoginsa sabida ita ta rayune akan a bata umarni tabi, yadda mutun keso haka take masa.

Ahaka dai ta kammala cin abincin, bayan ta kimtsa wajenne kuma, kaitsaye ta wuce bedroom d’insa.

Koda ta shiga bedroom din, komai nasa need yake babu wani datti.
New bedsheet ta shumfud’a masa, tare kuma da blanket mai taushi, kana ta kunna turare mai dadin kamshi acikin dakin.

Cikin yan mintuna kadan ta kyale masa dakin, ga kuma kamshi da yake tashi tako Ina.

Bayan ta kammala gyaran dakinne kuma, ta wuce toilet inda ta wanke masa shi tsab.

Koda ta fito daga toilet din, yalwataccen hasken dake cikin dakin ta kashe,  tare kuma da ficewa ta jawo kofar ta rufe.

Kaitsaye daga dakin nasa kuma kitchine ta nufa, atsanake ta soma wanke plate din da suka

b’ata.

Tana cikin wanke plate dinne kuma, karamar wayar daya bata din ta soma kara.

Ganin sunan Aunty Fauziya na yawo akan screen din wayarne, kuma yasa ta dagawa tare da kara wayan kan kunnenta.

Saidai kuma jin shiru ba’ayi magana bane, yasa ta gyara tsayuwarta tare dayin sallama.

Daga can b’angaren Aunty Fauziya ta sauke ajiyar zuciya, kana cikin kulawa tace.

“Allah yasa dai kinyi abunda na sakaki din, bawai kin tsaya nuna sanyin halinkin nan ba, Jannart nasanki da sanyi.”

Murmushi Jannart din tayi kana murya atausashe tace.

“Nayi duk abunda kikace My Aunty, yanzu ma Ina kitchine ne saboda ya fita.”

Murmushin Jin dadi Aunty Fauziyan tayi, cike dajin dadin daukar maganarta da Jannart din tayi tace.

“Masha Allah haka akeso ai, yanzu ki samu ki dafa masa abinci kafun ya dawo, kinsan maza dole sai ana kula da cikinsu.”

Shiru ta d’anyi na wasu mintuna kana asanyaye tace.

“My Aunty ai babu kayan abinci agidan, tunda mukazo ma ban tab’ayin girki ba, shi yakeyi mana order daga restaurant's.”

“Jannart ordern abinci kuma?”
Aunty Fauziyan ta tambaya da mamaki.

Jannart din kuwa jiki asanyaye, gudun kuma kar ace tayi wani laifin tace.

“Eh haka yakeyi kullum, saboda babu kayan provision agidan, kuma bawani cin abincin yakeyi sosai ba shiyasa, nafi tunanin kuma haka tsarinsa yake, saidai kafun mu taho nan din, lokacin da muke gida yakanci abinci sosai wasu lokutan.”

Ajiyar zuciya Aunty Fauziyan ta sauke kana cikin kulawa tace.

“To baga irinshi ba Jannart, tayaya kike tunanin zai iya jurewa cin abincin kasar da bata shi ba, wani abincin ma da zaki ganshi tamkar ruwa ne aka zuba masa ganyayyaki,  ya zama dole ki tashi ki kula da mijinki Jannart, maganar kayan provision kuma, kece zaki fad’a masa cewar ya

seyo kuna da buk'ata, duk da baizama Lallai ku samu abunda kukeso ba, amma dai ki dafa da kanki yafi ace sayowa kukayi,  nasan basu da wasu kayan abinci irin namu, amma ai kin iya sarrafa girkin zamani, sai kiyi kokari kina yi muku kuna ci, dan Allah Jannart ki kula sosai, dole sai kin tashi tsaye, kin tarairayi mijinki, saboda ahar kullum shine sama dake."

Sassanyar ajiyar zuciya Jannart din ta sauke, cikin gamsuwa da kalaman Aunty Fauziyan kuma tace.

"Shikenan My Aunty Insha Allah zanyi mishi magana, nagode sosai."

"Babu godiya atsakaninmu Jannart, fatana dai kawai shine ki zama daya daga cikin matan, da suka San daraja da kuma kimar mijinsu, yanzu ki k'arasa ayyukan da kikeyi,  watakila sai zuwa Gobe zan kuma kiranki."

"To My Aunty ahuta gajiya."
Jannart din ta fad'a

Cikin sauri Aunty Fauziyya tace.
"Yauwa kinga zan mance abinda yasa na kiraki ko.
Dama jiya muke mgn da Hajia Rabi'ah, kin san itama maigidanta yana Mascow to jiya da muka hadu wurin aiki take cemin, next week zata taho wurinsa".
Cikin jin dadi tace.
"Kai Alhamdulillah my Aunty in tazo zatazo wurina ko?".
Murmushi Fa'iziyya tayi tare da ci gaba da cewa.
"Akwai wasu kayyakine na gani a wurin AYSHA ALIYU GARKUWA, kayane irin namu na mata da kuma kayyakin ƙamshi toh nama saya miki, na bata 80k tayi miki haɗin mai kyau nasa tasa miki komai ɗan dai-dai,  in sha Allah zan bawa Hajia Rabi'ah, zata kawo miki".
Cikin tsananin jin daɗi tace.
"Allah sarki my Aunty ngd Matuƙa Allah ya biyaki da mafi kyawun sakamako".
Amin Ya Allah ta amsa cikin son yarinyar.
Daga nan sai sukayi sallama murmushi Jannart tayi
tare da zare wayar akunnenta.

D'an Jim tayi nay'an wasu mintuna, kana atsanake kuma ta cigaba da aikin da takeyi.

Bayan ta kammala wanke wanken ne kuma, ta dawo falo tare da kunna tv.

K'aramar wayar dake rike a hannun nata ta kunna, tare da yin dialing numbern Mamy.

Cikin sa'a bugu biyu kuwa Mamyn ta d'aga.

"Assalamu Alaikum Mamy barka da yamma ci."
Jannart din ta fada cikin girmamawa.

Mamy kuwa jin muryar Jannart dinne, yasa ta fadada fara'arta, tare da amsa mata sallaman, cike kuma dajin dadin kiranta da Jannart din tayi tace.

“Yauwa Jannart barkadai, ya kuke ya mai jiki ya kuma fama da sanyi?”

Murmushi mai sauti Jannart din tayi, kana anutse tace.

“Alhamdulillah Mamy, jikin kam yayi sauki sosai, saidai amma fa muna shan sanyi, Allah Mamy duk nayi kewarku sosai.”

“Muma haka Jannart munyi kewarki sosai, ko d'azu ma saida Ramadan yayi korafin wai ya gaji, zai biyoku Mascown zaizo kiyi mishi miyan kase, nace masa Lallai kuwa bazai tab'a cin miyan kase ba ashe, indai acikin Mascow ne.”

Dariya sosai Jannart din tayi,    tare da gyara zamanta, cike da kewarsu tace.

“Allah sarki Ramadan Idan muka dawo Insha Allah, zanyi mishi miyan kase, Mamy Ina Abba da Baba Maud'o.”

“Sunanan lafiya Jannart, shekaran jiya ma Baba Maud'o ke tambayanki, saboda yace Rayyern kam suna waya dashi sosai.”

“Allah sarki Baba Maud'o tunda muka tafi bamuyi magana ba, amma Insha Allah yau zan kira Ramadan sai ya had'amu mu gaisa.”

“Aikuwa da kin kyauta saboda yana ta tambayanki.”
Mamyn ta fad'a cikin kulawa.

Hira suka Dan tab'a da Mamyn kafun daga bisani sukayi sallama.

Mamyn na kashe wayar kuwa, Jannart tayi dialing numbern, Ramadan saidai jin wayar tasa bata shiga ne, yasa ta ajiye nata wayan tare da kwanciya akan kujera, kana ahankali ta maida idanunta ga tv.

Tananan cikin falon azaune kuwa, har saida aka soma kiraye kirayen sallan magriba, kafun ta tashi ta wuce daki.

Koda ta shiga dakin kayan dake jikinta ta cire, tare da wucewa toilet kaitsaye tayi wanka.
Koda ta fito daga wankan, mai da powder kawai ta shafa akan fuskarta, sai kuma oily lips stick.

Bayan ta gama shafan ne kuma, atsanake ta nufi wajen trolley dinta, bud'e trolleyn tayi tare da ciro wani riga da sket.

Mai kalan baki, Koda ta sanya kayan cib cib sukayi mata ajiki, Yayinda lafaffen cikinta ya bayyana.

Bayan ta saka d'aya daga cikin hijab dinta ne kuma, ta tada sallah, saboda zuwa lokacin tasan anshiga sallan magriba.

Koda ta idar da sallan kuwa bata tashi akan sallayan ba, har saida ta idar da sallan Isha.

Ahankali ta murd'a handle din kofar dakinta ta fito, zuwa falon.

Zama tayi akan kujera tare da lumshe Idanunta, cikin sanyi take sauraran karan tv'n dake tashi acikin falon.

Dai-dai lokacin Ya bud'o kofar falon ya shigo, hannunsa rike da ledodin Halal Restaurant.

Jin alamun shigowarsa ne kuma, yasa Jannart din bud'e Idanunta, Ahankali ta sauke ganinta akansa.

Kasancewar kuma shi dinma kallonta yakeyi ne, yasa idanunsu sarkewa acikin na juna.

D'anyin kasa da kanta tayi, Ahankali kuma ta mik'e tsaye, cikin sanyi,
ta nufi inda yake.

Ganin hakanne kuma yasa kashi zuba mata narkakkun idanunsa.

Jannart kuwa ahankali ta k'araso inda Rayyern din ke tsaye, cikin kuma yanayinta na sanyi, ta mika hannu ta karb'i ledan dake hannunsa.

Batare kuma da ta dago Kai ta kallesa ba, cikin sanyin murya tace.

"Sannu da dawowa."

Kansa ya d'an jinjina mata ahankali, Cikin yanayin kasalan da ganinta ya haifar masa kuma, ya karasa shigowa cikin falon.

Ganin hakan kuwa shiya saka Jannart din rufa masa baya.

Akan daya daga cikin kujerun falon ya zauna, tare da lumshe gajiyayyun idanunsa, kana akasalance kuma yake shak'an daddad'an k'amshin turaren dake tashi acikin falon.

Jannart kuwa atsanake ta ajiye ledan daya kawo din akan table, Kaitsaye kuma ta wuce kitchine.

Ta k’asan idanunsa yabi bayanta da kallo, Yayinda acikin zuciyarsa yakejin wani irin abu nayi masa yawo,  ga kuma kasalan daya saukar masa lokaci guda hannunsa yasa ya dafe kanshi yana mai sauke numfashi.

Jannart kuwa Koda ta shiga kitchine din, plate, cup and spoon ta d’auko, sai kuma fridge da ta bud’e ta d’auko drinks.

Atsanake ta nufo cikin falon, saidai kuma bata yarda ta saka Idanunta acikin nasa ba.

K’arasowa gabansa tayi, tare da jawo table ta ajiye  plate da kuma cup din awajen.

Ledodin restaurant din daya kawo ta bud’e, tare da zuba masa abincin acikin plate din.

D’agowa tayi ahankali ta kalleshi, musamman kyakkyawar fuskarsa da ta sakeyin haske, ga kuma yalwataccen sajensa da yake kwance lub lub.

Zara zaran eye lashes d’insa da suke alumshe ta kalla, ahankali kuma cikin tausasa murya tace.

“Naan ga abincin .”

Kansa ya d’an jinjina mata, hade kuma  da bud’e idanunsa, Cikin nutsuwa ya jawo plate din abincin gabansa ya soma ci.

Ganin hakanne kuma yasa ta zama ad’an nesa dashi, tare da sadda kanta k’asa, Ahankali take wasa da y’an yatsun hannunta, wanda ayanzu yin hakan ya zame mata jiki, saidai kuma azahirin gaskiya gaba, daya tunaninta ya tafi ne, izuwa wani waje na daban, saboda hakanan takejin maganganun Aunty Fauziya nayi mata yawo a kwakwalwarta.

Rayyern dake cin abinci kuwa, duk wani yanayinta yana lure dashi,  time to time kuma yake yawan kallonta, saboda ba kad’anba bak’in kayan da ta sanya yayi mata kyau.

Suna nan ahaka dai harya kammala cin abincin.

Ahankali ta d’ago Idanunta ta kalleshi, ganin yana goge bakinsa da tissue ne kuma, yasa ta fahimtar cewa ya koshi.

Kasancewar kuma ita ba wani yunwa takeji sosai ba, shiyasa ta soma tartare wajen.

Ganin Rayyern din na kokarin mikewa tsaye ne kuma, yasa cikin sauri ta d’ago da Idanunta ta kalleshi.

“Naan.”
Takira sunansa asanyaye cikin kuma Dan yanayin shagwab’ar, da ta sashi tsayawa da abunda yakeyi.

Atsanake ya juyo ya kalleta, Ganin ta sunkuyar da kanta kasa ne, kuma ya sashi komawa ya zauna akan kujera.

Again idanu ya zuba mata, tare da soma karantar yanayinta.

Jannart kuwa hakanan taji ta kasa fad’an abunda takeson fadad’in, saima zuciyarta da taji tana bugawa da k’arfi.

“Kinyi shiru tell me what happened?”

Ya fad’a cikin wata irin murya mai sanyi, da kuma tausasawa wanda hakan ne ya bata wani confidence.

D’ago da kanta tayi ta kalleshi araunace, cikin cool da kuma son fahimtar dashi tace.

“Please Naan ka kawo mana abubuwan buk’ata saboda inason na fara girki.”

Ta kare maganan tana me tsaresa da idanu, tare da fargaba akan zai amince ko a’a...!

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:56 - 🥰🥰: Idanu shima Rayyern din ya zuba mata, Ahankali kuma ya d’an nisa tare da gyara zamansa, atsanake yace.

“You’ll cooking why? Ko bakyason abincin restaurant din da nake kawo miki ne?”

Yayi tambayar Cikin kulawa, still kuma yana me kallonta.

Itakuwa Jannart Ganin irin Kallon da yakeyi mata ne, yasa tayi k’asa da kanta,  asanyaye tace.

“A'a kawai dai inason na fara girki ne.”

“Okay shima girkin yana cikin aikin da yasa Abba ce mu taho tarene?.”

Kai ta ɗan ɗago ta kalleshi ganin yadda ya tsareta da idone yasata yin ƙasa da kai.
“Abba yace mu taho tarene dan ki kula sani, so in Kuma na liƙa miki aikin girgi ai baki da lokacin kula dani, in dai da gaske kike kula da nidin zakiyi”.
Yayi mgnar cikin kauda kai dan shi kanshi mmkin kansa yake a kwanakin nan.
Ita kuwa Jannart a hankali tace.
“Toh ai shima kula da kaine”.
Da sauri yace.
“Toh shi na yafe ki bari sai mun koma gida, a nan dai cewa akayi ki kuladani da gadina ko”.
Ya ida mgnar murmushi ya tsubce mishi.
Ita kuwa shiru, tai
“Kin ganeko?”.
Ya fada atakaice tare kuma da tashi, kaitsaye ya nufi bedroom d’insa, saboda dama bai shigo cikin gidan ba, saida yayi sallan Isha.

Da idanu ta bishi har saida taga shigewarsa, cikin dakin kafun ta tashi tare dakai plate and takeaways din kitchine, itakam yoghurt kawai tasha, tare da wuce wa dakinta ta soma buga game.

Yana shiga bedroom nasa,
ya rage kayan jikinsa kana nufi saman gadonsa ya kwanta.

Idanunsa ya dan lumshe saboda wani irin daddad’an kamshi, daya bugi hancinsa, wanda yake tashi ajikin bedsheet din.

Sake gyara kwanciyarsa yayi, tare da jawo laptop d’insa ya soma duba, sakonnin da suka shigo email dinsa.

Yana kwance ahaka kuwa bacci ya daukesa.

Yayinda a b’angaren Jannart ma hakanne ya kasance, domin tana tsaka da latsa waya, bacci mai nauyi ya dauketa.
Batare dako kofar d’akinta ta rufe ba.

Washegari.

Kamar yanda suka saba haka yau dinma, da sassafe kafun gari ya gama yin haske yayi musu ordern abincin.

Koda ya gama shiryawa kuma, abincin ya d’anci kadan, batare kuma daya jira fitowar Jannart d’in ba, ya wuce Azimut hotel Olympic Mascow inda zasuyi meeting.

Yayinda Jannart kuwa sai bayan ya tafin ta iya fitowa taci nata abincin.

*After 3days*

Ahaka suka ci gaba da rayuwa, Yayinda take iya kokarin ta wajen  kulawa dashi, domin aduk sanda ya dawo takan fito ta bashi abinci yaci, sannan kuma akan Idanunta yake shan magungunan sa kana ta gyara masa ɗaki, a hankali wata iriyar sassayar shaƙuwa ta ɗan fara ratsa zuƙatansu.

Tun daga wancan ranan da sukayi maganan kayan abinci kuwa, bai sake dago mata maganar ba, har zuwa yau din kuma bai kawo kayan provision dinba.

Itama kuma ganin yayi shiru shiyasa bata sake ce masa komai agame da hakan ba, duk abunda ya kamata kuwa tana yi mishi.

Domin kullum bayan ya fita takan shiga ta gyara masa d’akinsa, tare da wanke masa toilet.

Saidai kuma dare nayi kowannensu yake kama gabansa.
Bata shiga d’akin nasa da dare ne kuma, gudun kada ya sake koranta kamar yanda yayi mata a wancan ranan duk da tana ganin sauye-sauye sa yawa daga garesa.

Ranar yau ta kasance Tuesday, kuma yaune zasu fara gwaji akan heart surgery, wannan dalilin yasa gaba d’aya, Doctors din a ankare suke.
Kowa ya shirya tsab tare da fatan samun nasara.

Kamar yanda ya saba kuma ordern abinci yayi musu, bayan ankawo yaci nasa ne kuma, ya d’auki briefcase d’insa ya wuce Hospital.

Koda ya karasa Hospital din already ya samu duka Doctors din, kasancewar shi kawai dama ake jira, shiyasa yana zuwa suka shiga theater room dan fara aikin.

Acan gida kuwa Jannart kwata kwata, ko fitowa yau din batayi ba, bacci tasha ta koshi, Koda ta tashi daga baccin kuwa game ta d’anyi awayanta, kana daga bisani bacci b’arawo ya sake d’aukarta.

Atak’aice dai haka ta k’are wunin ranan, batare da ta fito taci abincin da Rayyern din ya ajiye mata ba.

Asashin su Rayyern kuwa komai ya tafi musu yanda suke so, domin kuwa har sunyi surgery din, kuma komai yayi kyau, inda kowannensu ya fito da kyakkyawan result.

Bayan sun kammala duk wani abun da zasuyi ne kuma, kaitsaye ya nufo hanyar dawowa gida, saboda yau din duk agajiye yake jin kansa.

Kafun ya karaso gidanne kuma ya tsaya, a wani restaurant ya saya musu abinci.

Koda ya karaso gidan bayan ya gama dai-dai-ta parking din motarsa, anutse yake tafiya har ya k'araso cikin falon,  yana shigowa kuwa ya soma kokarin zare, suit din dake jikinsa, yana acikin hakanne kuma idanunsa suka sauka akan takeaway din daya ajiye mata tun safe, Wanda kwata kwata babu alaman an tab'ashi.

Idanunsa ya d'an kankance cike kuma da mamaki yake Kallon takeaway din.

Ahaka har ya karasa shigowa cikin falon.
Saboda ya tabbatar da abunda yake zargi ne kuma, ya sashi bud'e takeaway din, Aikuwa abincin yana nan babu alaman ko cokali daya anyi.

Ajiyar zuciya ya d'an sauk'e tare kuma da juyawa, ya kalli kofar dakinta dake kulle.

Ahankali kuma ya janye idanunsa daga Kallon dakin, ledan dake hannunsa ya ajiye, Kaitsaye kuma ya wuce bedroom d'insa.

Yana shiga ya soma rage kayan jikinsa, tare da wucewa toilet yayi wanka hadi da dauro alwala, kasancewar ankusa kiran sallan magriba.

Yana fitowa awankan kuwa mai kawai ya shafa, sai turare wanda shafasa ya zame masa d'abi'a.

Anutse ya zura wata army green jallabiya ajikinsa, wayarsa da kuma key din motarsa ya dauka, kaitsaye kuma ya fice daga falon, bayan ya saka wasu slippers a kafafunsa.

Koda ya fito falon zama yayi Ganin akwai dan sauran lokaci ne kuma, yasa shi zama ya d'anci abincin kad'an.

Bayan ya kammala ne kuma ya shiga, kitchine ya kuskure bakinsa,  batare da wani jinkiri ba kuma, ya juya kaitsaye ya fice daga cikin falon.

Cikin sa'a kuwa yana zuwa masallacin ana shiga sallan, hakan yasa da hanzari ya shiga jam'i.

Bayan sun idar da sallan kamar yanda ya saba, zama yayi a masallacin har saida suka sallame sallan Isha, Kafun ya kama hanyar dawowa gida.

Again Yana shigowa falon takeaway din abincin daya ajiye ya kalla, saidai ganin bataci abincin ba kamar yanda ya ajiye haka yazo ya samu,  ya sashi d'ago kansa fuskarsa d'auke da yanayin mamaki yake Kallon kofar dakinta.

Inda yake jiyo sautin muryarta na tashi, wanda da'alama kuma waya takeyi.

Ahankali ya dan matsa kusa da kofar nata, dai-dai lokacin kuwa yaji sautin muryarta na fadin.

“Okay My Aunty Insha Allah zan kiyaye, eh zan bashi number Hajia Rabi'ah wata ƙil zai yarda ya amso min su.”

Ajiyar zuciya ya dan sauke, saboda Jin muryar nata ya tabbatar masa da cewar tana lafiya.

Kasancewar babu abunda zaiyi acikin falonne kuma, yasa shi juyawa ya wuce bedroom d’insa.

Yana shiga kuwa ya zare jallabiyan dake jikinsa, tare da komawa ya kwanta akan gadonsa, had’e da lullub’awa jikinsa blanket, kana ya jawo system d’insa ya soma latsawa.

Yana nan ahaka har bacci ya daukesa.

Jannart kuwa har dare ya raba bata fito taci abincin ba, tun tana buga game awayarta kuwa, har bacci b’arawo ya dauketa.

Washegari.

Yau dinma tun kafun ya fita yayi musu order.
Kamar yanda ta saba ay’an kwanakin kuma, ita da kanta ta zuba masa abincin a plate yaci.
Saidai ita bai ga alaman zata ci ba, Dan komawa can gefe tayi ta zauna.

Ahaka harya kammala cin abincinsa ya tafi.

Ita kuwa Jannart Ganin ya tafi ne, yasa ta tattare wajen daya ci abincin.
Batare kuma da ita taci ba ta koma d’aki tayi kwanciyarta dan fruits take dan ci in taji yunwa kasancewar akwaisu a Fridge.

*some hours ago*

Ahankali ya daura hannayensa akan waist d’insa, tare kuma da fesar da wani irin numfashi.

Abincin safe da kuma na daren daya ajiye mata, wanda duk bata ci ba ya kuma kallo, Cikin yanayin tsananin mamakin kwana biyu da ta dauka, bata saka abinci acikinta ba, ya dago ya kalli kofar dakinta.

Yayinda acikin ransa yake tambayar kansa, abunda zai hanata cin abinci har na tsawon 2days.

Wani tunani da yazo cikin ransa ne kuma, yasa shi juyawa ya nufi bedroom d’insa.

Jannart dake dakinta kuwa, tana sane bawai kuma tana kin cin, abincin bane saboda wani abu

na daban, kawai dai tana yin hakanne saboda tana son, ya tuna da maganan kayan provision dinsu, ba ya ga haka kuma, ta gaji da cin kalan abubuwan da yake kawo mata din, shiyasa yanzun kawai take shan fruit.

Rayyern kuwa Koda ya shiga dakinsa, kwanciya yayi  tare da lumshe idanunsa.

Ahankali yake sauke ajiyar zuciya, Yayinda acikin ransa yakejin, rashin Jin dadin cin abincin da Jannart din batayi ba.
Wani abu daya sake tunawa ne kuma, yasa shi tab'e bakinsa tare da d'age kafad'unsa, cikin halin ko in kula yace.

“Wannan damuwarta ne, bataji yunwa bane.”

Daga can wani b'angare na zuciyarsa kuwa, sai yaji kaman abunda ya fada din ba dai-dai bane, domin har abada bazai tab'a manta irin yanda tayi kuka sosai akansa ba, ta tsaya dashi alokacin da yake halin buk'atar taimako, ta kula dashi sosai more especially akan lafiyarsa ya lura tunda yayi ciwo take bashi kula ta musamman mai cike da tausayawa ta kula dashi fiye da yadda Abbanshi, da Mamy da Ramadan kan kula dashi in ciwonsa ya tashi.

Yanaji ajikinsa bai kyautu yayi mata haka ba, kodan abubuwan da tayi masa.

Ahankali ya fesar da wani irin numfashi, tare da mikewa atsanake ya karasa gaban drawern sa.

Wani riga da wando ya ciro, tare da saka kayan ajikinsa, kaitsaye ya nufi hanyar fita daga dakin.

*Nigeria.*

Alhaji Idi Sale Dakata ne ke zaune, acikin tamfatsetsen falonsa, Yayinda Abba Kabir ke zaune acan gefensa.

Zugum haka suka zauna kowannensu da irin abunda, yake sak'awa acikin zuciyarsa.

Dai-dai lokacin kuma Momy ta shigo, ta iskesu acikin irin yanayin, Dan jim tayi tana me nazartarsu, domin da dukkan alamu ta fahimci cewar, wani magana suka tattauna atsakaninsu, wanda hakan yasa duk sukayi jigum.

Ganin mood din nasu ne kuma, yasa Momyn juyawa ta koma, batare da ta ce kala ba, saboda ma ta lura kwata kwata su Abba Kabir din basu ganta ba.

Acan Mascow kuwa Jannart ne ke kwance, Yayinda wayanta ke sakale akan kunnenta, tana waya da Riyyam nsra, wanda ya hadata da Mammy da kuma Zaytoon suka gaisa.

Rayyern kuwa Koda ya fito daga cikin dakin nasa, sosai yayi kyau cikin shigar dake jikinsa.
Inda ya daura babban jacket akan shigar tasa, saboda wani irin matsanancin sanyi da akeyi.

Dan jim yayi tare da Kallon ƙofar nata, acikin zuciyarsa yake tunanin me zai fada mata, sanin bashi da wani abun cewa ne kuma, yasa shi nufar dakin nata kai tsaye.

Ahankali ya tura kofar dakin ya shiga, bakinsa dauke da sallama.

Jin alamun bud'e kofar dakinne kuma, yasa Jannart dake zaune saurin juyowa suka had'a idanu dashi.

Wayar dake kunnenta ta zare, tare da tashi ta zauna tana me fuskantar shi.
Cikin kuma Dan yanayin mamakin ganinsa acikin dakin tace.

“Naan.”

Idanunsa ya zuba mata, saboda ganin yanda duk saman breast dinta ya bayyana, kasancewar wuyan rigar dake jikinta ya zame batare da tasan hakan ba.

Ahankali ya karasa shigowa cikin dakin, tare da karasawa gaban dressing mirrorn ta, inda yaga wani cup ajiye agefe.
Lek'a Cikin kofin yayi wanda yake dauke da zuma.

Juyowa yayi ya kalleta, hakan ne kuwa yasa da sauri tayi kasa da kanta tana murza yatsun hannunta.

“Meye kike wani sunkuyar dakai, sai kace kinga Dodo.”

Kanta ta girgiza masa alaman “A'a.”
Still batare kuma da ta dago Kanta ta kalleshi ba.

Shikuwa Rayyern idanunsa ya cigaba da tsura mata, Ahankali kuma ya matso kusa da ita, tare dasa hannunsa acikin aljihun wandon sa, cikin tsareta da idanu yace.

“Meyasa bakya cin abinci, tell me mekike ci Janna?”

Kanta ta girgiza masa alaman “Babu.”
Still kuma bata dago ta kalleshi ba, haka kuma bata motsa labb'an bakinta ba.

Shikuwa Rayyern Ganin hakan ne yasa shi, bata fuska cikin tsare gida yace.

“Almost 2days baki ci abinci ba, meyasa ahaka kikeson kina rayuwa, bakisan cewar rashin cin abinci, yana haifar da Ulcer ba?”.

Saurin dan satan kallonsa tayi, saboda Jin abunda ya fada din, kasancewar tasan halinsa shine ma gwani wajen Kin cin abinci.
Amma wai yanzu da bakinsa yake fadin hakan.

Fuska tadan kwabe ashagwab'e kuma cikin narkar da murya tace.

“Nifa banason abincin ne, bayamin dadi kuma nace maka ka saya mana kayan provision amma kaki..”

Ta kare maganan tana me tura bakinta gaba.

Wanda hakan yasa shi dan lumshe idanunsa, ahankali yace.

“To kenan idan bake kika dafa abincin ba, bazaki ci ba?”

Sake kwabe fuska tayi, still a raunace tace.

“Ni fa yanzu ma yunwa nakeji sosai, kuma ni banason wancan abincin.”

Idanunsa yadan zuba mata, Cikin yanayin nazartar ta yace.

“Okay wani kalan abinci kikeso?”

“Nigerian Dishes nakeso, ba irin way'anda kake kawowa ba.”

Ta fada tana me karyar da wuyanta gefe.

“Nigerian dishes? a Mascow dinne zaki samu Nigerian dishes? like bakisan awacce k'asa kike ba ko?”

Yayi maganan yana me kallonta, Domin har yanzu idanunsa na gane masa saman breast dinta dake waje da nimples ɗin ta da suke tsaye cas.

Jannart kuwa Jin abunda ya fad'a dinne, yasa ta kwab'e fuska tare da yin rau rau da Idanunta.

“Alright Oya taso mu tafi.”

Rayyern din ya fad'a, yana me duba agogon dake daure atsintsiyar hannunta.

Itakuwa jin abunda yace dinne yasa ta tashi ta tsaya.

Kallonta ya somayi daga sama har kasa, inda take sanya da dogon wandon pencil jeans, sai

kuma t-shirt mai fadin wuya, akanta kuwa hulan sanyi ne, sai kuma kafarta da ta sawa safa.

D’an soma Kallon dakin yayi, inda ya sauke idanunsa, akan wani shararan riga mai kaman abaya dake gefen gadonta.

Daukan rigan yayi tare da mika mata.

“Idan kinsa ki sameni a falo.”

Ya fadi haka yana me juyawa ya fice daga dakin.

Jannart kuwa jin hakanne yasa ta saka riga mai kaman abayan, tare da daukan wani karamin vail ta yane kanta dashi.

Cikin dan sauri ta saka wasu takalma sau ciki akafanta,  wayarta ta dauka batare kuma da b’ata lokaci ba, ta rufa masa baya.

Koda ta fito falon hanyan waje taga ya nufa, wanda hakan yasa ta d’an tsayawa cikin sanyi tace.

“Naan Ina zamuje?”

“Restaurant.”
Ya fada atakaice batare kuma daya juyo ya kalleta ba.

Itakuwa jin hakanne yasa ta gyara mayafin jikinta, cike dajin dadin fitar da zatayi a karo na forko tunda suka zo, ta rufa masa baya, Dan hakanan sai taji wani farinciki, saboda tun da suka zo Mascow din bata fita ba ko sau daya.

Koda suka karaso wajen motar tasa, cikin zumudi ta bud’e murfin motar ta shiga.

Shi kansa Rayyern ya lura da irin farincikin da take ciki, wanda hakan yasa shi jin wani irin abu a Cikin zuciyarsa.

Yana shiga cikin motar ya tada ita kaitsaye suka fice daga Cikin gidan.

Suna hawa kan titi ne kuma karamar wayar tasa dake hannunta ta soma kara,  Ganin sunan Riyyam-nsra na yawo akan screen din wayar ne kuma, yasa ta d’agawa tare da kara wayar akan kunnenta.

Daga can b’angaren Riyyam-nsra din yace.

“My Aunty dazu muna waya dake kika katse lafiya kuwa?”.

Murmushi tayi cikin kuma kasa boye farin cikinta tace.

“Sorry Riyyam Hamma ne yake kirana zamu fita shiyasa na katse.”

Murmushi Riyyam-nsra din yayi, cikin jin dadi yace.

“Ahh Lallai To sai kun dawo.”

Yana gama fadin haka ya kashe wayan.

Ita kuwa Jannart juyowa tayi ta ɗan kalleshi a hankali tace.
“Naan”.
Shima ɗin juyowan yayi ya ɗan kalleta, tare da cewa.
“Na'am Janna”.
Cikin yanayin sanyi tace.
“Uhum dama akwai sakon da aka iko min ne daga Nigeria”.
Da sauri yace.
“Saƙon me kuma A wurin waye?”.
Gyara zama tayi tare da cewa.
“Magungunan sanyine da turaruka Aunty na ta aiko min, sabida ciwona kuma da yanayin sanyin garin”.
A nitse yace.
“Toh zamu amsoshi”.
Wayarta ɗago tare da cewa.
“Sai dai in kira Aunty  Rabi'atu sai kuyi mgn ta gaya maka inda take, muje ko”.
Kai gyaɗa mata, yana mai kallon titin,
ita kuwa da sauri ta kira Hajia Rabi'ah kana ta bashi waya,
a mutunce suka gaisa kana tayi mishi kwatancen masauƙin.
Miƙa mata wayar yayi tare da cewa.
“Mu fara zuwa can dan muna kusa da inda suken.”.
Haka kuwa akayi tafiyar 13mnt sukayi suka riski gidan.
Mutunce aka tarbesu.
ganin kamar sauri sukeyine yasa ta ɗauko kayan ta bata, kana ta rakosu har wurin mota.
A sit ɗin baya ta ajiye katon ɗin tare da shiga gaba, kana yaja mota suka tafi.
Tafi kaɗan  suka iso wani babban wajen shak’atawa Victory park wuri mai masifar kyau da kayan k’awa.

Parking motar yayi ya fita, jim kadan kuma sai gashi ya dawo hannayensa rike da robobin ice cream.

Gyara zamansa yayi, tare da ɗan juyowa ya kalli fuskarta mai kewaye da yanayin ta na sanyin

rauni,
Mik'a mata yayi tare da cewa.
"Kina sha?!".
Da sauri ta gyaɗa mishi kanta,
Tare da miƙo hannunta ta kama rubar, a hankali ya d'an kauda idanunsa tare da sa yatsunshi kan nata ya manna a jikin robar mai masifar sanyi.
"Sheyyyhhhhh".
Taja wani irin dogon sauti sabida masifar sanyin da taji yana ratsa yatsunta.
Shi kuwa Rayyern wani irin yar-yar haka yaji tsikar jikinsa na zubawa sabida sautin da taja ya gigita masa kwanya,

"Ahshhhhy Naan sanyi".
Ta faɗa cikin wata iriyar sassayar murya".

Juyo da kanshi yayi ya fuskanceta tare da jingina kan nasa jikin kujera.
A hankali ya turo harshensa waje kad'an ya d'am laso lips ɗinshi, still bai sake mata hannunba, Cikin wata iriyar fitinenneyar murya yace.
"Kin cika raki sanyi nefa ba zafiba".
Yayi mgnar yana tsareta da narkakkun idanunsa.
Rau-rau tayi tare da kwaɓe fuska.
Ƙara matse hannunta yayi.
"Ahsssshyyy Naan zafeeeeeh!".
Ta kuma sakin ƙara da ɗan ƙarfi.
Bakinshi ya ɗan tura tare da cewa.
"Raki ki koyi juriya da kame bakin nan da iface-iface kada wata rana kiyi abin kunya,".ya ƙare mgnar tare da
Sake hannun nata  kana ya sa hannun kan siterin motar, sannan ya kifa kansa bisa tafukan hannunsa yayi shiru yana maijin wani irin masifeffen abu akanta ji yake tamkar ya ruggume ta ko zaiji sanyin abin.

Itama shiru tayi tana hurawa yatsunta dumin bakinta,
Shi kuwa Rayyern wasu tagwayen numfarfashin yake sauƙewa a hankali,
Kusan 56 second suka d'auka a haka
Kana ya gyara zamanshi Tare kuma da tada motar  suka kara gaba.

Itakuwa Jannart duk da tasan bata wani shan sanyi sosai, amma tana matukar son ice cream sosai.
Ga kuma yunwan da takeji, shiyasa batare da wani tsawaita tunani ba akan illar da zai iya mata ta soma shan ice cream din tanasha tana lumshe ido, shi kuwa Rayyern a fakaice yake kallonta.

Ahaka har suka isa wani  babban wurin cin abinci Russian pub restaurant wurine da akeji dashi a ƙasar wanda mutanen k'asashe ma banbanta ke zuwa shiyasa mafi akasari akwai abincin kasashe daban-daban ɗan wuri  yafi kowanne girma acikin garin na Mascow.

Suna isa kuwa ya bud’e murfin motar ya fito, Ganin hakanne kuma yasa Jannart din fitowa itama.

Kaitsaye suka nufi cikin restaurant  din.

Koda suka je Ab’angaren daya kasance na musamman suka zauna.

Daya daga cikin Waiters na restaurant din  ne ya kawo musu menu.

Rayyern kuwa Kasancewar baya bukatar abincin ne, yasa shi mikawa Jannart din menu.

Duk da cewar bata ga Nigerian dishes acikin jadawalin abincin ba, amma ta zab’i abunda take Ganin zata iya ci.

Take kuwa aka kawo mata abunda ta buk’a din.
Nan aka jera mata abubuwan da ta zaɓa,

Shi kuwa Rayyern gyara zamanshi yayi tare da d’an fesar da numfashin cikin zuba mata narkakkun idanunsa yace.
“Kici”.
Jin abinda yacene, da kuma yunwar dake zaƙularta yasa ta sa hannu ta dauki spoon tare da gyara zama kana ta fara ci.
Yanayi tana kallon can woje kasan cewar akwai glasss mai ruwan garai-garai.
Kana iya ganin waje.

Rayyern kuwa Ganin ta soma cin abincin ne, yasa shi mikewa.
“Naan!”.
Tace ganin ya juya zai tafi,
Juyowa yayi ya dan kalleta,
Kanshi ya jinjina ganin kallon tambayar ina zakaje takeyi masane yasashi cewa.
“Kici ina zuwa zan d’an shiga cikin Mall d'in nanne”.
Kai ta gyaɗa mishi cikin gamsuwa.
Shi kuwa  kaitsaye ya nufi mall din dake cikin restaurant din.

Jannart kuwa da idanu ta bisa, kana kuma taci gaba da cin abincinta yanayi tana d’an lallatsa wayarta.

Dai-dai lokacinne kuma Azeez ya shigo cikin restaurant din, yana shigowa Cikin wajen daya kasance VIP ya
Zauma kujerar dage can gefenta wanda shima da glasss a tsakaninsu,
Bayan an kawo mishi abinda yake buƙata ne kuma ya ɗan fara ci,

Loma biyu ana uku ya ɗan ɗago kansa dan jin alamun akwai mutun gefensa, ai kuwa idanunsa sauka akan ta.

Cikin wani irin tsananin mamaki, kaɗuwa, al'ajabi  ya zaro Idanunsa waje cike da tsananin mamaki hadi da firgici ya mik'e tsaye, jiki na rawa ya ya soma nufo inda take zaune.
Saboda yana son ya tabbatar da cewa, idanunsa bawai gizo sukeyi masa ba.

Aikuwa isowar sa wajen ya tabbatar masa da cewar, bawai gizo idanunsa keyi masa ba.

Wannan dalilin yasa cikin tashin hankali da kuma firgici da tarin mamaki yace.

"JANNART."

Da sauri Jannart din ta juyo saboda Jin muryar ɗan uwanta Yah Azeez d'in tayi acikin kunnuwanta.

Aikuwa tamkar ba zata haka taga Yayan nata tsaye akanta.
  Da wani irin sauri ta Mike tsaye baki na rawa tace.
"Laah Yah Azeez".
 batare da ta jirayi komai ba kuma ta fad'a jikinsa.

Tare da rungume sa kam kam cike da tsananin Jin dadi kuma tace.

"Yah Azeez."

Rungume ta sosai Yah Azeez din yayi sabida ganin abin yake tamkar a mafarki shiyasa ya ruggumeta gam dan ya tabbar ido biyune.

Dai-dai lokacin kuma Rayyern ya fito daga mall din,  fitowar tasa kuwa tayi dai-dai da rungumetada Azeez din yayi.
Atake kuwa idanunsa ya sauka akansu cikin wani irin....!

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:58 - 🥰🥰: Idanun nasa ya zazzaro waje cikin kuma yanayin tsantsar mamaki, yake Kallon Jannart din wanda take rungume akirjin wani Namiji wanda baimasan dashi ba.

Lokaci daya kuma cikin few second yaji wasu irin abubuwa na yawo acikin brain d'insa, zuciyarsa kuwa wani irin zafi takeyi tamkar Wacce aka hurawa wuta.

Ransa yakai kololuwar b’aci musamman tunawa da yayi, cewar akwai igiyar aurensa akanta wani irin abu mai masifar ɗaci yaji ya tokari ƙahon zuciyarsa.

Jannart kuwa da tsananin farinciki ya cika zuciyarta, sake rungume Yayan nata tayi, Yayinda takejin wani irin nutsuwa da dadi acikin zuciyarta.

Yah Azeez din kuwa ahankali ya tallab’o kanta, muryarsa adan raunace, da kuma tsananin mamakin ganinta ak’asar da yayi yace.

“Jannart kece? I can believe inajin har yanzu kaman mafarki nakeyi.”

Sake rungumeshi sosai Jannart din tayi, cike da matsanancin farincikin da take ciki kuma tace.

“Nice Yah Azeez bawai mafarki kakeyi ba, nayi kewarku sosai, Nayi kewarka Yah Azeez.”
Ta kare maganan cikin rawan murya, tare da jin wasu irin hawaye na kokarin, cika Idanunta.

Yah Azeez kuwa Ganin hakanne yasa shi, tallafo hab’arta tare da Kallon fuskarta, bakinsa dauke da tarin tambayoyi yace.

“Jannart Meya kawoki Mascow? Jannart ke dawaye kukazo? Meyasa kikabar gida Jannart Meyasa? Kowa yana cewa kin b’ata hankalin su Daddy duk atashe yake akanki? Jannart wa ya kawoki k’asarnan???”

Yah Azeez din yayi mata duka tambayoyin, cikin tsananin damuwa da kuma wani tarin fargaba, saboda bayason ya yarda da abunda zuciyarsa ke fada masa, cewar Jannart din guduwa tayi ko ta biyo saurayine.

Dai-dai lokacin kuma Rayyern dake tsaye, wanda zuwa yanzu ya gama cika fam, zuciyarsa tafasa take sosai, Yayinda ransa kuwa yayi masifar b’aci idanunsa har rufewa sukeyi, ahasale kuma cikin takaici ya soma takowa zuwa inda suke.

Jannart kuwa jin tambayoyin da Yah Azeez din keyi mata ne, yasa ta dago idanunsa da suka cika da k’walla ta kalleshi,  bud’e bakinta da niyar yin magana da tayi, yayi dai-dai da isowar Rayyern wajen.

Ransa amatukar b’ace yasa hannunsa d’aya ya damko Jannart din, tare da janye ta ajikin Azeez, ahasale kuma cikin fad’a, da b’acin rai ya saka hannunsa d'aya akan kirjin Azeez ya turesa gefe.

Cikin bayyana tsananin b’acin ransa, ya watsawa Azeez din wani irin mugun kallon da yasa hantar cikin Azeez kad'awa.
Taune lip d'insa na k'asa yayi tare da nuna masa yatsa afad’ace yace.

“You’re very stupid man, waye kai da zaka zo ka rike min matata haka? I say Who are you?” Ya k’are mgnar da karfi cike da hautsinewar tunani.
Idanu Yah Azeez ya zubawa Rayyern din, wanda yafi yi masa kama balarabe, saidai jin yayi Hausa ne yasa shi kankance idanunsa, shima ransa ad’an b’ace yace.

“Bakai zaka tambayeni ni waye ba, ni zan tambayeka ko kai waye, akan meye zaka zo ka tureni haka? Kasan ko ita din wacece awajena, waye kai meye kai sannan akan meya zaka janye ta daga gareni, meye alak’arka da ita da har kake cewa matarka wanne ubanne ya aura maka ita!?”.

Wani irin buguwa Jannart taji zuciyarta tayi, saboda ita sai ayanzu ne ma take tunawa, da cewar babu wanda yasan inda take.

A matuk’ar tsorace ta dawo da kallonta ga Yah Azeez, wanda yake jifahta da Kallon tuhuma, Yayinda shi kuwa Rayyern gaba daya ma yanayin fuskarsa ta sanja, idanunsan nan sunyi jajur, haka ma fuskarsa dake bayyana alamun bacin rai.

Wani irin tsorone taji ya kamata, wanda hakan yasa ta rumtse Idanunta.

Rayyern kuwa wani irin hautsinennen kallo ya watsawa Azeez, din Cikin yanayin bacin rai kuma yaja wani irin dogon tsuka, tare da bangaje Azeez din.

“Tamyata kakeyi akan matata mallakina dana biya sadaki aka ɗauka mana aure da cikakkun shaidu kamar yadda musulunci ya tsara, akan matata sirrina kake cemin haka Stupid kawai.” Ya fad’a in don’t care manner.

Batare dako Kallon Azeez din ya sake ba, ya damke hannun Jannart, tare da janta cikin zafin Rai suka nufi hanyar fita daga restaurant din.

Ganin hakanne kuma yasa Azeez rufa musu baya, cikin tsananin mamaki da rudu yake cewa.

“Hey you stop, ina zaka kaita meye hadinka da ita, da har kakeson guduwa da ita?!!!!”

Yah Azeez din ya fad’a da d’an k’arfi, adai-dai lokacin suka fito daga restaurant din.

Jannart kuwa Ganin idanun Rayyern din sun rufe da b’acin rai ne, yasa ta soma dan jujjuya kanta, cikin muryarta dake fitar da sautin kuka take cewa.

“Naan please leave me, Dan Allah ka tsaya kaji please Naan ka tsaya nayi maka bayani pleaseeeeeee....”

Ta kare maganan cikin tsananin damuwa, tare kuma da dan waiwayawa tana Kallon Yah Azeez dake biyosu.

Sam Rayyern kam kamar ba dashi ma Jannart din take ba, kwata kwata yaki sauraranta, hasalima ji yake tamkar ya fara buga wasan, kwallo da ita awajen tsabar takaici.

Dai-dai lokacin suka iso bakin motarsa, gefen me zaman banza ya bud'e, batare da tunanin ko zataji ciwo ba, ransa amatukar bace ya cillata cikin motar, tare da maida murfin motar ya rufe gib.

Cikin fusata ya juyo ya shige cikin motar shima, tare da yi mata key ahasale ya cillata kan titi.

Ganin hakanne kuma yasa ran Aziz sake b'aci, afusace shima ya tafi da gudu ya shiga tasa motar Dan rufa musu baya, saidai kafun ma ya tada nasa motar har sun hau kan titi.

Tuni kuma wasu motoci sunsha gabansa, wanda hakan yasa motar su Rayyern din yi masa nisa, kasancewar kuma dare ne shiyasa cinkoson ta d'anyi yawa, saidai duk da haka bai dauke idanunsa daga kan, motar Rayyern dinba saboda bayaso su b'ace masa.

Rayyern kuwa wani irin gudu yake shararawa akan titin, tamkar wanda zai tashi sama,  wanda kuma daga gani kasan zuciyarsa cike take da bacin rai.

Hakanne kuma yasa ko Kallon Jannart din baiyi ba, wanda taji ciwo a hannunta sanadiyar wurgata acikin motar da yayi.

Jannart kuwa gaba daya duk ta rud'e, Yayinda hawaye ke gangara akan fuskarta.
Cikin tsananin damuwa da kuma magiya take cewa.

“PLEASE Naan dan Allah ka tsaya, kaji D'an uwa.........”

“Shut up, ki rufemin baki ko na tattaki acikin motar nan zaki tsaya da aurena a kanki kina ruggume ko wani Tom and Jerry d'in!!!  In ruggumar kikeso ki gaya min Mana in ruggumeki ko na hanaki ruggumeni ne!!!!”.

Ya katseta ta hanyar fadin haka atsawace.

Tsawar da ya haifar mata da kad'awan yayan hanji, da kuma wani irin fad'uwar gaba, saboda tunda take dashi yaune kawai, taji yayi irin wannan tsawan, ga kuma wata irin murya da yayi mata magana dashi, mai saka mutum firgicewa.

Numfashinta dake kokarin k'wacewa, saboda tsawan da yayi mata din ta fusgo, lokaci daya kuma taji wani irin matsanancin kuka, na taso mata.

Hakanne kuma yasa ta manna kanta da jikin glass din window'n motar, asanyaye ta saki wani marayan kuka, wanda  ita kanta batasan kukan na meye bane, na tsoron Rayyern dinne ko

kuma na jimamin ganin Yah Azeez dinta ne, itama bata sani ba.

Kasancewar kuma glass din windown b'angaren da take zaune, yana d'an sauk'e ne yasa duk wani snow da akeyi, yake busata Yayinda dusan kankara keta saukowa ajikinta.

Rayyern kuwa duk da yana iya jiyo sautin tashin kukanta, amma haka yayi banza da ita, saima gudu daya ci gaba dayi tamkar wanda zai tashi sama.

Suna ahaka dinne kuma taga ya kama wata hanya ta daban, ba hanyar da suka biyo ba, domin duk da bata tab'a fitowa ba tunda suka zo, amma tasan inda suke bi yanzun ba hanyar gidansu bane.

Yah Azeez da har yanzu ke biye dasu kuwa, gaba daya awahalce yake tukin, saboda yanda motoci sukayi yawa agabansa, kasancewar tuni su Rayyern din sunyi masa nisa.

Rayyern dake driving kuwa fahimtar Azeez din na biyosu ne, yasa shi shiga wata kwana mai yawan go slow, tafiya sukayi na tsawon 30mn kafun suka iso, gaban wani makeken hotel d'in izmailovo alfa hotel, wanda aka k'awatasa da furanni masu matuk'ar kyau.

Parking motar Rayyern yayi, batare daya jira wani abu ba kuma ya bud'e murfin motar ya fito.

Kaitsaye b'angaren da Jannart din ke zaune ya nufo, bud'e murfin motar yayi, tare da finciko hannunta ya fito da ita daga cikin motar.

Ransa ab'ace yake sosai shiyasa bai damu, dako dusan k'ank'aran dake saukowa yana sauka akansu ba.
Musamman ita Jannart da bawani kayan kirki bane ajikinta, wanda tun acikin motan dusan k'ank'aran ya bata mata jiki.

Kaitsaye wani park dake cikin hotel din suka nufa, suna isa wajen kuwa Rayyern din ya rike hannunta gam, tare da sunkuyawa ya durk'usar da, ita ak'asan wasu shuken shuken flowers suka zauna bisa kujera.

Batare kuma daya damu da irin yanda dusan k'ank'aran ke dukansu,
Still har yanzu kuma yana rike da hannunta.
Saidai yanzun tafin hannayensu ne ke had'e.

Dai-dai lokacin kuwa Yah Azeez ya shigo cikin hotel din, ganin motar mutumin dake tare da Jannart din da yayi a fake ne, kuma yasa shi saurin yin parking nasa motar shima, cikin hanxari kuma ya fito tare da nufan cikin hotel din Kaitsaye, saboda shi atunaninsa sun shiga cikin hotel dinne.

Rayyern kuwa da yake Kallon Azeez din, ganin ya shiga cikin hotel dinne, yasa shi yin kwafa

tare da sake jawo Jannart din, kaitsaye ya nufi wajen motarsa.
Bayan sun shiga ne kuma yaja motar suka kara gaba.

Idanunta ta rumtse da karfi, tare kuma da matse jikinta waje daya, sosai jikinta yake karkarawa wanda hakan yasa numfashinta wani irin fusga sabida abubuwan sun had’e mata ga sanyin da tasha, ga na garin ga tsoro hakan yasa numfashin ya fara sauya salon fira.
Har yakai ga sautin fitan numfashin nata, na ratsa cikin kunnuwansa.

Juyowa yayi ya dan kalleta, tare kuma da watsa mata Harara, cikin  zafin zuciya ya cigaba da tuk’a motar, yana shara gudu tamkar mai tashi sama.

Acan hotel kuwa Yah Azeez Kaitsaye receiption na hotel din ya nufa, saidai koda ya tambaya ko akwai mutanen da suka shigo yanzu, ce masa akayi babu.

Wannan dalilin yasa asanyaye ya fito daga cikin hotel din, yana fitowa kuwa idanunsa suka sauka, akan wajen daya bar motar Rayyern din.

Ganin babu motar awajenne kuma yasa shi dafe kansa, cikin takaici yace.

“Oh My God I lost them, who be this guy? Waye shi meye hadinsa da Jannart, nasani Jannart ba mutumiyar banza bace, saboda haka babu yanda za’ayi ace, tana da alak’a da mutumin da baisan koshi waye ba.”

Tsuka yaja tare dasa hannu ya  buga sterring motarsa, cike da takaicin rasa su da yayi yace.

“Ina fatan sake ganinki Jannart, wancan guy din kuwa ko waye shi, saina koya masa hankali, koma meye ne ya faru asanadiyarka ne Junaid, saboda Kai da kuma banzan halinka ne, Jannart take cikin duk wannan yanayin, huuhhhhhhh.”

Ya fesar da wani irin numfashi mai zafi.

Asanyaye kuma cikin takaici ya koma cikin motarsa ya zauna.

Acan b’angaren Jannart kuwa zuwa yanzu, karfin hali kawai takeyi wajen kwato numfashinta, saboda wani irin sanyin da takeji, yana ratsa har cikin k’ashi da b’argonta.
Wannan dalilin yasa ta kankame jikinta waje daya.

Dai-dai lokacin kuma Rayyern din yayi parking motar, acikin wasu jerin motoci dake gaban wani had’add’en garden d’in Hermitage garden Mascow, wanda aka wadatasa da yalwan haske tako ta ina.

Ahankali ya zare sit belt din dake jikinsa, tare kuma da juyawa ya kalli bayansa,  Ganin kuma

babu wata mota dake bin bayansu ne, yasa shi bude murfin motar ya fito.

Still zagayawa gefenta yayi ya fito da ita, duk da cewar yanajin irin karkarwar da hannunta daya rike keyi, amma haka ya share tare da hade fuskar sa domin shi kansa bai san iya azabar fushin da ke ransaba wanda bai san na menene ba, ko kallonta kuwa baiyi ba sabida wani irin zafi da tafasa da zuciyarshi keyi ko gyabta idonsa yayi ganinta yake ruggume jikin Azeez, kaitsaye ya nufi cikin Garden din.

Suna shiga cikin kuwa ya sake hannunta, tare da nufan wani privet sit ya zauna.

Ahankali kuma ya juya yana me watsa mata Harara, saboda wani takaicin da yakeji,  abanza ta jawo masa b'uya tamkar  wani marar gaskiya ko b'arawo.

Jannart kuwa da duk jikinta ke karkarwa, Ganin irin Kallon da Rayyern din ke watsa mata ne, yasa ta kame jikinta waje d'aya, tare da rumtse Idanunta, saboda wani irin sanyi da takeji.

A kujeran dake facing nasa ta zauna, tare da sake kankame jikinta waje daya, hakanan ta samu kanta da wani irin tsoronsa, wanda ita kanta batasan kona meye ba.

D'aya daga cikin waiter na wajenne ya k'araso, tare da Dan rusunawa ya tambayesu me za'a kawo musu.

“Coffee.”
Rayyern ya bashi amsa atak'aice, Yayinda kasa kasa kuma yake hararan Jannart din, wanda daga inda yake din yana iya jiyo yanda, numfashinta ke fusga tamkar Wacce zata wacce tayi tsare.

Bakinsa ya d'an tab'e tare da kawar da kansa gefe, domin acan cikin zuciyarsa har yanzu, wani irin b'acin rai yakeji.

Cikin abunda bai wuce 5mn ba, waiter din ya kawo musu coffee two cup, wanda yake ta faman tururi saboda zafin da yake dashi.

D'an d'ago Kanta tayi ahankali ta saci kallonshi, Ganin kuma ba ita yake kallo bane yasa ta, d'aukan coffee din da sauri ta Kai bakinta.

Idanunta ta d'an lumshe tare da sauke ajiyar zuciya, domin duk da cewar coffee din akwai zafi sosai, amma hakan bai hanata kaiwa cikin bakinta ba.
Saidai kuma saboda tsananin sanyin da akeyi, yasa zafin Coffee din bai kona mata baki ba, madadin haka saima wani irin nutsuwa da taji yana saukar mata, Yayinda dumin Coffee din ke dumama mata hanjin cikinta.

Jin dadin hakanne kuma yasa ta shanye coffee din lokaci guda, domin dama bawai wani yawa

ne dashi ba.

Ajiye cup din nata tayi ahankali tare kuma da turo dan karamin bakinta gaba, cikin rauni da kuma yanayin tsoronsa dake damunta, ta turo d'an k'aramin bakinta gaba.
Still Ahankali kuma ta soma motsa labb'an bakinta, wanda da'alama wani abu takeson fad'a, amma kuma ta kasa saidai Kallon Rayyern din da takeyi kasa kasa.

Rayyern kuwa duk abunda takeyi yana lura da ita sarai, bawai kuma Dan idanunsa basa kanta bane, shi yake nufin baya kallonta, a'a kawai dai da idanun zuciyarsa yake kallonta, kuma duk hankalinsa yana kanta ne.

Jannart ko Ganin da gaske idanunsa ba'a kanta suke bane, yasa ta jawo d'ayan kofin Coffee din, wanda aka ajiye dominsa, batare da wani tunani ba ta kafa kofin abakinta, bata ciresa ba kuwa saida ta shanye coffee din tas.

Sai alokacinne kuma ya juyo ya kalleta, da sauri ta ajiye kofin dake hannunta, gudun kada yayi mata masifa ne kuma, yasa tayu rau-rau da ido tare da narke fuska.
Sai kuwa ta rumtse Idanunta, like masifan Idan yayi mata akan idanunta zai sauk'a.

Rayyern kuwa Ganin hakanne yasa shi, had'e fuska cikin muryar dakiya yace.

“Da kika shanye naki Coffee din, kika dawo kan nawa baki nayi? Kin iya shan abuna kice kina so in ruggumeki ne bazaki iya bako”.

Kanta tad'an girgiza Ahankali kuma Cikin yanayin tsoron kada, ya sake daka mata tsawa irin yanda yayi mata d'azu ta girgiza masa Kai alaman “A'a.”

Shikuwa harara ya watsa mata tare, da d'agawa waiter hannu kana yayi masa alama, akan ak'aro musu wani Coffee din.

Ita dai Jannart jin baiyi mata tsawan bane, yasa asanyaye ta bud'e Idanunta, tare da hade yan yatsunta waje daya, ta soma murzasu dan saboda sanyi, har ji take tamkar ba ahannunta suke ba.

Kamar yanda Rayyern din ya buk'ata kuwa, wani Coffee din aka sake kawo musu.

Tura mata kofi daya yayi gabanta, Yayinda shi kuma ya d'auki nasa ya soma sipping ahankali.

Jannart dake masifar jin sanyi kuwa, batajin zata iya sipping coffee din da kad'an kad'an, hakan yasa ta sake Kai cup din bakinta, bata ciresa ba kuma saida ta shanye duka Coffe din.
Wanda daga zamanta zuwa yanzu tasha 3cup kenan.

Har yanzu kuwa jarababben sanyin da takeji, yaki barinta saima kara shiga jikinta da yakeyi,

kasancewar Cafe din da suke ciki, duk akewaye yake da shuke shuke, da yake cikin garden yake haka wajen yake da shuke-shuke, wannan dalilin yasa wajen yake da sanyi sosai.

Shiyasa har yanzu jikin Jannart din yaki daina b'ari, haka take ta karkarwa tamkar Wacce aka jonawa Shocking.

Rayyern ahankali ya ajiye cup din dake hannunsa, tare kuma da d'ago kansa ya kalleta.
Rawar sanyi takeyi sosai, domin hatta hakwaranta suma karkarwan sanyi sukeyi, kayan dake jikinta ya dan soma karewa kallo, wanda gaba daya duk dusan kankara ya b'atasu, musamman Y'ar abayan dake saman kayan nata, hatta gashin kanta ma dusan k'ank'arane.

Kawar da kansa gefe yayi, tare da mikewa tsaye ya sake had'e fuskarsa sosai, rigar sweater'n dake jikinsa ya zare.
Tare da takowa ahankali ya dawo bayanta, cikin tsare gida da hade fuska, ya yafa mata sweater din nasa ajikinta.
Wanda yasan hakan zai taimaka mata wajen rage sanyin.
Dai-dai ya juyo ne kuma idanunsa suka sauk'a, akan motar Azeez wanda tazo ta gilma ta wajen, ya hango motar ne kuma saboda duka wajen glass ne, wanda yake ciki zai iya hango komai dake waje.

"Oh my God wannan wanni irin mayene? Meyasa yake ta bibiyarmu? Why why???"

Ya k'are maganan cikin wani sabon b'acin rai, da kuma haushin ta da yakeji saboda itace ta jawo komai, domin da tun farko taci abincin daya kawo mata din, da yanzu basu fito har Suna wasan tsere da wani daban ba.

Ahasale ya sake kamo hannunta, batare kuma da ya bari ta gama mikewa tsaye ba, ya soma janta bayan ya ajiye kudin Coffee din da suka sha, akan table din kaitsaye suka fice daga wajen.

Ita dai Jannart binsa kawai takeyi tamkar rak'umi da akala.
Suna shiga cikin mota kuwa yayi reverse, tare dayin yanke yabi wata hanyar na daban, wanda kuma yayi hakanne saboda, gudun kada su sake had'uwa da Azeez, wanda shi kwata kwata baisan waye shiba.

Tafiya kad'an sukayi ba wani mai tsawo ba, suka iso gaban wani makeken hotel.
Mascow Marriott Grand hotel, wanda kuma da dukkan alama hotel ne na musamman, da ko acikin garin ba kowane ke zuwa ba dan hotel ne daya amsa sunansa.

Bud'e murfin motar yayi tare da fitowa, Ganin hakanne kuma yasa Jannart dake, duk'unk'une cikin sweaternsa, bud'e murfin motar itama ta fito.

Ganin da yayi tana d'an waige waige ne kuma, yasa shi kama hannunta da karfi.

Haka suka nufi cikin hotel din yana gaba tana biye dashi abaya.
Koda suka k'arasa receiption d'aki ya kama musu, parlor and 1bedroom.
Bayan an basu key dinne kuma suka wuce sama.

Suna shiga cikin y...!

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:58 - 🥰🥰: Kamar jira yakeyi kuwa suna shiga cikin dakin, ya sake hannunta tare da turata gefe, Cikin yanayin b'acin rai da murtuk'e fuska yace.

“Waye shi? Waye wancan  gardin da kika rungume, tell me wayeshi wanni d'an iska ne, da har kike had'a jikinki da nashi? Akanme zaki manna masa ƙirjinki mallakina a ƙirjinsa?”.

Ya k'are maganan cikin masifar tsawa Cikin fushi kuma da b'acin rai.

Jin ya kira Yah Azeez din da d'an iskane kuma, ya sata soma girgiza kanta, lokaci daya kuma cikin muryata da ta raunana sosai tace.

“Shifa ba d'an iska bane.”

“Ohhhh.”
Ya fada yana me kura mata idanu, tare kuma dasa hannayensa ya kama waist d'insa, cikin fushi yace.

“Da kikaje kika rungumesa, ya kwantar dake acikin jikinsa sadakin nawa ya biya aka d'aura muku aure? Waye shaidun ku!?”.
Da sauri ta fara jujjuya mishi kai hawaye na kwaranyo mata sam ta gaza cewa komai.

Shi kuwa Rayyern cikin takaici murya a sark'afe yace.
“Janna da aurena fa ya ruggumeki hakan shine ba iskanci ba kenan da aurena fa a kanki kefa matatace kika manna masa ƙirjinki a nasa Janna hakan dai-dai neeh.”
Ya kare mgnar tamkar zaiyi kuka.

Saurin girgiza masa kai tayi, kana Cikin yanayin tsoro tsoro tace.

“Allah ba d'an iska bane Yayanah ne.”

“Karya kikeyi taya ya ya zama yayanki, a ina kuma yaushe har kike kiransa yayanki, kina da aure amma saboda rainin na barki kina abinda kikaga dama kinje kina runguman wani k’aton banza! Sabida na barki ko?”.

Ya kare maganan atsawace wanda har saida taji yay’an hanjin ta sun kad’a.

Hakanne kuma yasa cikin raunin da yafi kama da shogob'owa a wurin mai kallonta da sakalci tace.

“K’aton banza kuma?
shifa ba k’aton banza bane, Allah Yaya nane Yah Azeez ne Babanmu d’aya dashi, shine yayanmu na biyu fa dama yayi karatunsa anan kuma anan yake aiki, Allah ba karya bane kuma ma ka tambayesa kaji...”

Ta kare maganan da sigar dake bayyana tsananin yarintarta.

Rayyern kuwa Harara ya watsa mata, cikin kuma tsareta da idanu yace.

“Da Allah rufemin baki ke kina da Yayane.”

Idanunta ta d’an zazzaro tare da kwato numfashinta, murya na rawa tace.

“Mekake nufi ni bani da Yaya kenan? ka tambaya mana kaji Babanmu d’aya dashi.”

Ta fad’a tana me turo bakinta gaba.

Shikuwa Rayyern cikin halin ko in kula yace.

“Shutup dama ke kina da Babane? Waye baban naki?”

Saurin d’agowa tayi ta kalleshi, lokaci d’aya kuma taji numfashinta na kokarin k’wacewa, saboda abunda ya fad’a d’in yasa, taji numfashinta na slowdown.

Cikin yanayin rauni da kuma shagwab’ar dake damunta, kana cikin muryar kukan da yazo mata tace.

“Kamar ya zaka ce bani da Baba, wallahi ni dai inada Babana...”
Ta kare maganan tana me sakar masa kuka.

Ganin hakanne kuma yasa Rayyern din had’e fuska, tare da gyara tsayuwarsa cikin murtuk’e fuska, da kuma razanannen tsawa yace.

“Kirufemin baki duk uba baya juran ganin ana cutar da d’iyarsa naki da kike zaton mahaifinkine akwai ayar tambaya a kansa na raunin jink’ai na iyaye.”

Da sauri ta rufe bakinta tare da had’iye kukan nata, wanda hakan yasa numfashinta wani irin fusga, har saida taji kanta na juyawa luuuu Kamar zata fad’i.

Wani irin fusga ta soma yi da kirjinta, dan jawo numfashin nata dake kokarin kwacewa.

Shikuwa Rayyern saboda tsananin b’acin rai ko lura da hakan ma baiyi ba, juyawa yayi afusace ya nufi bedroom din dake cikin falon.

Shikansa ayau din baisan meya b’ata masa rai har haka ba, bai kuma san Meyasa zuciyarsa ke tafarfasa ba ya dai san tun ranar da yaga yadda Junaid na mata dukan mutuwa a gaban wanda take cewa mahaifinta bai kulaba yake da yak’in bai zama uban bad’ini ba kana in ya tuno yadda akayi aurensa da kalaman Barrister Kabir a lokuta ma-ban-ban-ta yakanji kansa na juyawa tabbas yasan akwai wani abu a k’asan tubalin wancan ahlin da take jin iyayenta ne.

Jannart kuwa Ganin ya wuce bedroom ne yasa ta, zama akan d’aya daga cikin kujerun falon, da sauri take maida numfashi, tare da rumtse idanunta.

Rayyern kuwa yana shiga bedroom din kayan dake jikinsa ya rage, tare da wucewa bathroom yayi wanka.

Bayan ya fito awankanne kuma ya sake maida kayan daya cire din, batare kuma daya sake bi takan al’amuranta ba, ya hau saman bed ya kwanta.

Har yanzu kuwa jin zuciyarsa yakeyi babu dadi, b’acin rai tsantsane kawai ke tafiya masa ya zama dole su kwana a hotel sabida gudun kar har yanzu wancan na bibiyarsu.....

Jannart.
Ahankali take sake matse jikinta waje daya, saboda wani irin masifaffen sanyin da takeji, wanda yake kara sawa numfashinta na seizing.

D’agowa tayi ta kalli agogon dake sak’ale ajikin bangon d’akin,  wanda yake nuna mata k’arfe d’aya na dare.

Sake matse jikinta tayi tare da karyar da wuyanta gefe, tana me tunanin yanda zatayi ta kwana acikin falon.
Musamman ga yanda numfashinta keyi yanzun, tamkar wanda zai d’auke gaba d’aya, da alama kuma asthma dinta ne Keson tashi.

Tana nan ahakane kuma taji ringtone na tashi, acikin aljihun rigarsa dake jikinta, da alama dai wayarsa ya bari acikin aljihun rigar.

Jin ringtone din yaki dai nawa Ne kuma, yasa ta sa hannu ta zaro wayartasa tare da ajiyesu akan table.

Kwata kwata ta kasa Koda kwanciya saboda, da zaran ta kwanta sai taji kamar numfashin nata zai bar jikinta.

After 10mn

Zuwa yanzu gaba d'aya ta fara shidewa saboda, yanda numfashin nata ke fita, yana yin sama da kasa, kirjinta kuwa sai duka yakeyi tamkar zai rabe biyu.

Acan b'angaren Azeez kuwa yawo yasha sosai, Ganin babu alamar zai sake ganinsu ne kuma, yasa shi hakura da neman nasu ya koma gida.
Saidai duk hankalinsa atashe yake.

Hakan yasa shi soma kiran Daddynsu amma kwata kwata, wayan Dadyn baya shiga.

Duk da cewar yasan yanzun dare ne, amma kwata kwata bazai iya hakura da abunda ya gani yau din ba, Lallai ya zama dole yakira gida ya sanar musu.

Samun wayar Daddyn nasu da yayi akashe ne kuma, yasa shi kiran wayan Abba Kabir, cikin sa'a kuwa wayar ya shiga.

Bugu biyu kuwa Barrister Kabir din ya d'auki wayar, tare da karawa akan kunnensa.

Azeez kuwa jin Abba Kabir ya d'aga wayarne, yasa batare daya jira wani abu ba, cikin tsananin rudani hadi da damuwar dake damunsa yace.

"Abba Naga JANNART."

Wani irin bugawa Barrister Kabir yaji zuciyarsa tayi, cikin tsananin tashin hankalin daya shiga yace.

"Innalillahi wa' Ilaihirraju'un Azeez wani irin magana kakeyi ne haka?"

"Magana nakeyi akan Jannart Abba, wallahi yau da idanuna naga Jannart a Mascow, Abba Jannart ba bata tayi ba, na ganta da idanuna kuma itama ta ganni, har na rungumeta kuma munyi magana da ita."

Yah Azeez din ya fada Cikin confidence.

Abba Kabir din kuwa gumin da suka keto masa ya share, cikin sabon tashin hankalin da yakejin

kansa aciki yace.

“Azeez ba Jannart bace, ba Jannart ka gani ba Azeez watakila idanunka gizo sukayi maka, amma ba ita bace.”

Cike da tsananin mamaki Azeez ya murtsuka idanunsa, saboda Jin abunda Abban nasu ya fad’a, lokaci daya kuma ya girgiza kansa, with full confidence yace.

“Abba ba karya nakeyi maka ba, ba kuma gizo idanuna sukeyi minba, Wallahi wallahi Jannart na gani ba wata ba, Abba taya kake tunanin zan kasa gane Jannart aduk inda na ganta, Jannart ce Abba wallahi ita nagani tare da wani saurayi, wani wanda bansan shiba, bana son zuciyata ta zargi Jannart, nasan ba halinta bane bare nayi tunanin ko wani saurayi ta biyo, kuma amma a yanayin dana ganta, batayi kama da irin wanda za’ace an saceta ba, naganta cikin kwanciyar hankali da jin dadi, Abba Ina cikin matuk’ar rud’ani, akan meya kawo Jannart Mascow..”

Shiru Barrister Kabir yayi, still kuma gumi ne ke sake keto masa, ya shiga tashin hankali kwarai. Wacce amsa zai bawa Azeez? Shine abunda ke dukan kwakwalwarsa...

Acan b’angaren su Jannart din kuwa,  duk yanda Rayyern yaso bacci ya daukesa abun yaci tura, domin da zaran ya rufe idanunsa, To hoton Jannart da wannan gayenne keyi masa yawo acikin idanunsa.

Doguwar tsuka ya kuma ja alokacin da ya sake jiyo, ringtone din wayarsa akaro na biyar, wanda yake tashi daga can cikin falon.

Ahankali ya zuro da k’afafunsa k’asa, saboda baisan wanene mai kiran nasa da wannan lokacin ba,  bud’e kofar dakin yayi tare da kutsa kansa cikin falon, Ganin wutan falon akunne ne kuma, yasa da mamaki ya karaso cikin falon.

Dai-dai yazo tsakiyar falonne kuma, kunnuwansa suka jiye masa yanda sautin, numfashin Jannart din ke fita, tamkar Wacce zata shid’e, domin da dukkan alama numfashinne ya k’wace mata.

Da sauri ya juyo ya kalleta, tare kuma da maida dubansa ga way’ansa Wacce take ta k’ara.

Screen din wayar ya kalla, ganin kuma sunan Barrister Kabir ne, ke yawo akan wayar yasa shi sake dawo da kallonsa ga Jannart din,  cikin wani irin yanayi yake kallonta.

Saidai kuma ganin kiran wayan na shirin katsewa ne, yasa shi daukar wayar tare da karawa akan kunnensa.

Daga can b’angaren kuwa Barrister Kabir din, jin Rayyern ya d’aga wayarne yasa cikin tashin hankali yace.

“Rayyern wani ya ganku yau?”
Yanayin yanda Barrister Kabir din yayi, maganar kamar adan tsorace ne kuma yasa Rayyern din gyara tsayuwarsa.

“Eh wani ya ganmu wani wanda bansan ko waye ba, ita kuma harda rungumeshi tayi, bansan dalilin ta nayin hakan ba.”

Rayyern din ya fad’a yana me kura mata idanu, fuskarsa kuwa ahad’e take, daga jin yanayin muryarsa kuma kasan cewa, ransa amatukar bace yake har yanzu.

Abba Kabir kuwa jin abunda Rayyern din ya fad’a ne, yasa shi dan yin shiru, kana kuma asanyaye yace.

“Azeez ne Tabbas Azeez da gaske yake yaga Jannart, nasan Kai baka sanshi ba amma ita ta sanshi, saboda yayanta ne d’an Alhaji Idi Sale Dakata ne.”

Fuska Rayyern din ya dan ya mutsa, still cikin rashin sakewa yace.

“Oh haka ta fad’a but I don’t trust her, cause naga tayi hugging nasa.”
Haka nan yaji yana ta maimaita gayawa Barrister Kabir yaga ta ruggumeshi like yana kai kararta ne garesa.

Ajiyar zuciya Barrister Kabir ya sauke, fahimtar wani abu dake sukar zuciyar Rayyern din da yayi ne kuma yasa shi, Dan tausasa murya kana asanyaye gane azabebben kishine ke cinsa yace.

“I’m sorry Rayyern yayanta ne da gaske kamar yanda ta fada ma, yanzu Ina Jannart din take.”

Kalonsa ya maida ga Jannart din, cikin kuma haushin ta da yakeji yace.

“Gatanan wai fushi takeyi dani dan na hanata ruggumeshi sai wani numfashi takeyi sama-sama.”

Ya fad’i maganan in don’t care manner.

Abba Kabir kuwa jin hakanne yasa, cikin tashin hankali yace.

“What Rayyern numfashi sama-sama kuma? Please check her tana da problem fa.”

Abba Kabir din ya fadi haka cikin gaggawa.

Wanda jin hakanne kuma yasa Rayyern kashe wayan, da sauri ya k’arasa kanta, saboda ganin

yanda take ta mimmik’ewa.

“Ke.”
Ya fad’a yana me d’an zungurinta da k’afansa.

Ko kallonsa baiga tayi ba balle yasaka ran zata amsa masa, saidai har yanzu numfashin nata bai daina k’wacewa ba.

Ganin hakanne kuma yasa shi d’an rank’wafowa kanta, idanunsa ya d’an kura mata Ganin abun nata like serious ne ya sashi cewa.

“Hey what’s wrong with you Janna?”

Kanta ta d’an soma girgizawa, Ahankali kuma Cikin sheshshekan numfashi ta kamo hannunsa wanda ya dafe saman kujera dashi.

D’aura hannun nasa tayi akan chest dinta, cikin wani irin yanayin dake nuna galabaitar ta, murya na rawa tace.

“Pl...Please Na... Naan zan mutu numfashina, ka taimakeni Naan mutuwa zanyi, numfashina zaibar jikina, help....... help......me”.

Ta karasa maganan cikin shakewar murya, lokaci daya kuma Idanunta suka soma juyewa.

Idanunsa ya zuba mata cike da mamaki, hadi da kuma tashin hankali yake kallonta.

Murya na dan rawa yace.

“Janna open your eyes and tell me what’s wrong? Tell me Janna meyeke damunki fad’amin kinji faɗa wa Naan ɗinki?.”

Yayi maganan yana me daura hannunsa akan wuyanta.

Jannart kuwa duk ta fara ficewa a hayyacinta, Yayinda hawaye ke bin gefen fuskarta yana kwarara, tanason gaya masa cewar Asthma dinta ne ya tashi, amma ta kasa saboda numfashinta dake seizing.

“Naaaaaannnnnnnnn Numfashinaaaaaaaaaa.....”

Da k’yar ta fadi hakan afusge, lokaci daya kuma numfashin nata yayi low, take kuma Idanunta suka lumshe.

Cikin hanzari mamaki, tsoro, rawan jiki, da kuma tashin hankali Rayyern din yasanya duka

hannayensa ya kama kafad’unta, hankalinsa amatukar tashe yace.

“Janna! Jaannaa!! please open your eyes, Janna are you okay? Janna weckup please..”

Ya kare maganan yana me jijjigata, hankalinsa atashe Ganin bata ko motsa bane, kuma yasa shi d’aukarta tare da rungumota jikinsa.

Tamkar wata Y’ar tsana haka ya d’auketa, Cikin hanzari kasancewar kuma key din motarsa yana cikin falonne, yasa yana dauka baijirayi komai ba, kaitsaye ya nufi hanyar fita daga falon.

Koda ya fito gudu ya fara Yayinda Jannart din ke cikin jikinsa,  kasancewar kuma Acan sama d’akin nasu yake ne, shiyasa dole saiyayi tafiya mai nisa kafun ya sauko.

Hakan kuwa shiyasa duk inda yazo wucewa sai ankalleshi, Yayinda ma’akaitan hotel din ke tambayansa ko lafiya.

“She’s patient.”
Shine kawai abunda yake fad’a musu.

Ahaka har ya sauko kasa, inda yayi parking motarsa.

Ak’agauce yayi  bud’e murfin motar  ya shiga, agefensa ya kwantar da ita.
Tare da yiwa motar key a 360 ya ja motar yayi gaba.

Gudu yake sosai akan titin kasancewar kuma, dare yayi sosai shiasa babu yawan ababen hawa akan titin.

Wannan dalilin yasa cikin mintuna kad’an ya iso harabar babban asibitin, wanda ya kasance shine mafi kusa dasu.

Yana zuwa kuwa ko gama dai-dai-ta parking din motar baiyi ba, ya fito tare da ita ajikinsa.
Kaitsaye ya nufi cikin asibitin.

Ganinsa da Doctors sukayi ne kuma, yasa kaitsaye suka kawo gadon marassa lafiya,  aka d’aura Jannart din akai.

Kaitsaye aka wuce da ita emergency, dan bata taimakon gaggawa, kasancewar tuni numfashinta yayi nasa gun.
Dole kuma sai an saka mata oxygen.

Kasancewar kuma Hospital din na d’aya daga cikin, inviglators din da suke koyar dasu abubuwa ne kuma musulmine, yasa aka yiwa Jannart din tarba mai kyau.

Domin Koda aka tashi shigar da ita Emergency din, tare da Rayyern aka shiga.

Gaba d’aya ya kasa ta b’uka komai, saidai idanu daya zubawa kan fuskarta, wanda aka sakawa Oxygen.

Yayinda sauran Doctors din kuwa, suka shiga checking dinta, saboda akwai hanyoyin da zasubi wajen Ganin hakikanin abunda ke damunta.

Shikuwa Rayyern Ganin hakanne yasa shi zaro wayarsa, tare da fita daga Emergency din.

Numbern Dr. Sulaiman ya kira saidai kwata kwata baya shiga.

Hakanne kuma yasa shi kiran layin Ramadan.

Cikin sa’a bugu biyu kuwa Ramadan din ya d’auki wayar.

“Ramadan.”
Rayyern ya kira sunansa cikin yanayin damuwa, batare daya bari Ramadan din yace wani abu ba kuma yace.

“Please Ramadan Jannart bata da lafiya, kwanaki da aka kawota Hospital namu meyake damunta?”
Yayi mgnar cikin ruɗu sabida bai san tanada matsalar numfashi ba.

“Subahanallah Hamma Rayyern meyake damunta yanzun? Ina take yanzu?”

Ramadan din ya fada cikin tashin hankali.

“Stop Ramadan ka amsamin tambayata.”

Rayyern din ya fada cikin zakuwa.

“I’m sorry Hamma Rayyern bani na kula da issues din nata ba, Dr. Sulaiman ne, kuma bansan meye problem din nata ba, but ka tambayi Dr. Sulaiman?”

“Way’ansa akashe Ramadan are you in Hospital?”

“Yeah.”
Ramadan din ya bada amsa, saboda dama yana Cikin Hospital din, kasancewar yau din night duty ne dashi.

Ajiyar zuciya Rayyern ya sauke, tare kuma da gyara tsayuwarsa cikin gaggawa yace.

“Okay kayi checking folder dinta, date folder 24/2/2020 please Ramadan hurry up.”

“Okay I will.”
Ramadan din ya fada tare da kashe wayan.
Kaitsaye kuma ya tashi ya nufi inda suke ajiyan folders dinsu.

Rayyern kuma tsayuwa yayi tare da zubaw fuskar Jannart din idanu, kasancewar daga inda yake tsaye din yana iya hango fuskarta ta jikin wani glass.

Jin wayarsa na kara ne kuma yasa shi, saurin dagawa tare da kara wayar akan kunnensa.

Ramadan kuwa jin Rayyern din ya d’aga ne, yasa shi cewa.

“Hamma Rayyern banga foldern Jannart ba fa, babu nata kwata kwata saidai ga wani nan, da nagani amma sunan da aka rubutu, shine Jannart Abdulkarim Sale Dakata.”

“What Abdulkarim Sale Dakata!!”

Rayyern din ya fad’a cikin mamaki, da kuma wani irin tunani da yaji ya tsaya masa Acikin zuciyarsa.

Saidai kuma ganin babu lokaci ne yasa, shi cewa.

“Meye problem din mai folder din? Sannan shekarunta nawa?”.

“22. Asthma.”
Ramadan ya fad’a yana me jujjuya folder din, dake hannunsa.

Rayyern kuwa jin hakanne yasa shi, kashe wayan tare da juyawa ya nufi cikin emergency room din.

Koda ya shiga kuwa ya samu har sun Gano matsalarta,  Cikin ikon Allah kuma har sun shawo kan matsalar nata.

Domin numfashinta ya dai-dai-ta sun kuma yi mata duk wani abu daya dace.

Saidai har yanzu basu cire mata oxygen dinba.

Ahaka aka kaita har zuwa dakin hutu.

Agefenta ya zauna tare da zuba mata ido,
A hankali ya lumshe idanunsa tare dasa hannunsa bisa hannunta dake gefensa,

Wani irin sassayan numfashi ya fesar lokacin daya haɗe tafin hannunnsu wuri ɗaya.
dai-dai lokacin ne kuma wayarsa ta soma kara, alaman shigowar kira.

Kallon screen din wayar yayi, Ganin kuma sunan Barrister Kabir ne ke yawo akan wayar, yasa shi d’aga kiran.

Yana karawa akan kunnensa Daga can b’angaren Barrister Kabir yace.

“Rayyern ya Jannart din, fatan tana lafiya?”

Shiru Rayyern din ya d’anyi, kamar bazai amsa ba can kuma, cikin dakiya yace.

“Barrister Waye Abdulkarim Sale Dakata?....!

*GARKUWAR taku ce dai MA'AURATA, da masu shirin aure, da masu jego, da yan gayu masu son k’amshi kece raini, da gyaran da zaike maimaita muku dararen forkon kuruciya*

Ko kunsan Jikinmu na da sinadaran hormones da suke taimakawa dan’adam akan komai musamman lokacin da mace take mu’amalar aure da mijinta. Mafi akasari wannan hormones din ne ke samun matsala ko su yi sanyi koma su daina aiki kwata-kwata shi ne dalilin da zai sa mace tace bata jin sha’awa ko bata san dadin aure ba. Albishirinku ina da kayan da ke taimakawa wannan sinadaran du dawo aiki tukuru don karkato miki da kimarki wajan mai gida sannan su taimakawa wannan sinadaran hormones dinki su dinka secreting din ni’ima wadatacciya da zata taimaka miki ki gamsu mijinki ya gamsu fiye da tunaninki. Note: Kayana ba sa tsinka ruwan ni’ima suna dai taimakawa hormones dinki ne su tsattsafo da ni’imar musamman wacca cutar sanyi ko dattin mahaifa ya dankarar da su ya hana su yin aikinsu yanda ya kamata. Haka zalika idan kina da kyau ki kara da wanka. Zaki iya amfani da magani na na gargajiya wanda zai gyara miki sex hormones din kullum ki kasance cikin humidify wato cikin damshi mai albarka kamar yanda ake son mace. Yana gyara miki mara.

Sai kamshi. Hajiyata daure ki fara amfani da turarena ki ji irin salon kamshin sa salo ne da zai daidaita ki da mijinki ya kankaro miki da kimarki a wajansa. Siyan na gari mayar da kudi gida.

Ga masu buƙata ga number' wayata wanda nake whatsApp dashi 09097853276 kimin mgn ta whatsApp in har kin tabbatar kin shirya saya mu dai-dai ta, kayana ba ƙanana bane, shiyasa bana harkan karanta, muddin kinsan baki shirya sayaba Please kada kiyi min mgn ki bari sai kin shirya kuɗinki a hannu, ba ina nufin kayana bana talaka bane, no akwai ƙananan set na masu karamin karfi, banson aimin mgn a ɓatamin lokacin aiyukana a shirme baki shiryaba. Shine karantan da bana so.
0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU. In kin shirya ga number ta ga kuma account number ta wanda in mun gama mgn zaki turo kudin ki, kana insa miki kaya a mota, duk ƙasar

da kike kayana zaije gareki, amman fa in kinada dalilin zuwan nasune🤝🏻sayan na gari meda kudi gida.

GARKUWAR MA'AURATA

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:58 - 🥰🥰: Wata iriyar bugawa zuciyar Barrister Kabir tayi, wanda har saida Rayyern din yaji sautin kakkarfar Ajiyar zuciyan daya sauk'e.

Ahankali kuma Cikin sanyi dason b'oye babbar damuwarsa yace.

"Barrister Abdulkarim Saleh Dakata yayana ne, sannan kuma k'anin Alhaji Idi Saleh Dakata ne, mu ukun duka acikin mahaifiya d'aya muka fito, haka ma kuma babanmu d'aya, amma Dr. Rayyern me yasa kayi min wannan tambayar?"

Barrister Kabir din ya tambaya, cike kuma dason jin amsar abunda ya tambayan.

Rayyern kuwa jin abunda Barrister Kabir din ya fad'a ne, yasa shi juyawa ahankali ya sauk'e idanunsa akan Jannart dake kwance, Wacce take shak'an numfashi ta Oxygen.
Yanayin yanda take kwance flat ne kuma yasa, Idan ba mutum ya kula da cewar tana shak'an numfashi ta oxygen ba, to direct zakayi tunanin matacciya ce, Dan babu wani abu na jikinta dake motsawa sai zuciyarta.
Murza tafin hannunta dake cikin nasa yayi tare, da ɗan ɗago hannun nata sama ya manna shi kan tattausan sajensa.
Ahankali kuma ya janye kallonsa daga gareta, tare da rumtse idanunsa, cikin dakiya ya gyara tsayuwarsa kana yace.

"I'm sorry to say Barrister ba dangartakar ku dashi nakeson sani ba, inason sanin matsayinsa da kuma alak'arsa da Matata Jannart ne?."

Wani irin dogon numfashi hadi da ajiyar zuciya, Barrister Kabir ya sauke, lokaci daya kuma duk idanunsa suka ciko da hawaye dan abubuwa biyu da suka zo masa lokacin daya kalmar matata da Rayyern ya kira Jannart da ita shine karsashinsa, son jin alak'anta da Barrister Abdulkareem Saleh Dakata kuwa shine mafi rinjayen rauninsa a rayuwar duniya, haka kuma damuwa mai tarin yawa ta bayyana akan fuskarsa, domin tambayar da Rayyern din yayi masa, ya tono masa wani rauni da kuma mikin dake kwance a zuciyarsa.

Asanyaye kuma cikin son kawar da maganan yace.

“Rayyern mubar wannan maganan, yanzu ka fad’amin wanni hali Jannart take ciki?”
Ya k’are maganan cikin raunin muryar da tasa, zuciyar Rayyern karaya, saboda ayanda yaji ak’asan muryar Barrister Kabir din, tsananin damuwa ne da kuma wani abu mai kama da fargaba.

Idanunsa dake alumshe ya d’an bud’e, kana cikin yin k’asa da murya yace.

“Zataji sauki da yardar Allah, saboda na kawota hospital dan yanzu haka ma oxygen ne ahancinta.”

Still ajiyar zuciya mai karfi Barrister Kabir din ya sauke, cikin tarin yanayin damuwa kuma yace.

“Allah Ya bata lafiya, kayi hakuri Rayyern Dan Allah ka kulamin da amanata, Jannart tana da buk’atar kulawarka ako da yaushe, Jannart marainiyace kada ka manta kuma duk wanda ya kula da maraya , Allah zai kula dashi sannan zaiyi masa Garkuwa aranar tashin Alk’iyama, Dan Allah Rayyern ka kula sosai, saboda tana da cronic asthma, nasan baka san da hakan ba, amma dole saika kiyaye wajen rabata ta'ammali da abu mai sanyi.”

Idanu Rayyern din ya kuma alumshewa kana ahankali, kuma cikin sanyi yace.

“Insha Allah zan kula da hakan, soon kuma zata samu sauki.”

“Allah yasa haka Rayyern, sannan kayi hakuri da ganinku da Azeez yayi, ya kuma tashi hankalinsa akanku ne, saboda yana d’aya daga cikin mutanen da suke kamar kashin bayan farin cikin Jannart, yana nuna tsananin kulawarsa agareta, shiyasa itama Jannart din da ta gansa, ta kasa hakuri har saida taje garesa.”

Kai Rayyern din ya dan jinjina, batare kuma daya sake cewa komai ba, ya maida idanunsa ya lumshe.

Barrister Kabir kuwa ci gaba da cewa yayi.

“Tabbas plan dinmu yaso lalacewa saboda ganinku da Azeez din yayi, amma Allah ya rufa mana asiri, saboda Koda Azeez ya kira wayan Alhaji Idi Sale Dakata, dan sanar dashi cewar yaga Jannart, wayar bata shigaba Wannan dalilin ne kuma, yasa Azeez din ya kirani, sanin bani da wata hujja ta karya da zan iya fad’a masa, Wacce zai gamsu da ita ne kuma, yasa na sanardashi gaskiya da kuma hakikanin abunda ke faruwa, saidai na fad’a masa cewar akan matsalar dake tsakaninta da Junaid ne yasa aka b’oyeta.”

Ajiyar zuciya Rayyern din yayi, tare da fesar da wani iska daga bakinsa.
Cikin kuma d’an yanayin rashin gamsuwa yace.

“Amma kana ga fad’a masa hakan bazai zamo matsala, ko sanadin rugujewar komai ba?”

“Bazai zama ba Rayyern, nasan Azeez nasan waye shi bazai tab’a fallasa abunda na fad’a masa ba, duk da na b’oye masa wasu abubuwan, amma nasan shikansa bayason irin cutarwar, da d’an uwansa Junaid ke nunawa ga k’anwar tasu, saboda haka karka damu Azeez zai iyayin komai dan bawa Jannart kariya, musamman ayanzu dana gargad’esa da kar ya fad’awa kowa, ya kuma yi min alk’awarin cewa bazai tab’a fad’ad’in ba zuwa gaba kuma zan sanar dashi dukkan abinda bai saniba.”

Again numfashi Rayyern din ya fesar, cikin kuma maida kallonsa ga Jannart din dake kwance yace.

“Shikenan ba damuwa.”

Shima Barrister Kabir din Ajiyar zuciya ya sauke kana anutse, cikin maida hawayen dake kwance acikin idanunsa yace.

“Rayyern akwai lokacin da zaka san waye Abdulkarim Saleh Dakata da alak’arsa da matarka, saidai kuma ba yanzu ba, amma kamar yanda Kaga Azeez haka shima yake, domin duk wani suffa da kamanninsa Azez ne ya d’auka,  domin sometimes Idan Jannart tana tambaya na, akan kamannin Baffan nata Abdulkarim Saleh Dakata, saboda bata sanshi ba nakan ce, ta kalli Azeez domin idan taga Azeez kamar photo copy d’insa ta gani, saboda tsananin kamar da sukeyi....”

Ya k’are maganan cikin wata irin muryar, dake bayyana alaman kuka, wanda hakanne kuma yasa shi, tsagaitawa da maganan.

Rayyern kuwa jin hakanne yasa shi, d’anyin shiru acikin zuciyarsa yana me mamakin abunda, zaisa Barrister Kabir din awannan yanayin, Lallai Tabbas yasan cewa akwai wani abu, da Barrister Kabir din yake b’oyewa, more especially yanzu da yayi masa tambaya, akan Abdulkarim Saleh Dakata, meyene To wannan abun?

Itace tambayar da bashi da amsarta.

Ganin shirun yayi yawa ne kuma yasa shi cewa.

“Allah ya jik’ansa da rahama, yasa can yafi masa nan.”

“Ameen summa Ameen nagode matuk’a Rayyern.”

Barrister Kabir din ya fad’a cikin wani sabon sheshshek’an daya zo masa, Jin da yayi kuka mai sauti na shirin k’wace masa ne kuma, yasa shi ajiye wayan batare kuma daya katse kiran ba.

Araunace ya kifa kansa akan pillown dake hannunsa, cikin tarin damuwa da kuma ciwon da

yakeji aransa, ya saki kuka mai tsuma zuciya.

Dai-dai lokacin kuma Aunty Dijat dake tsaka da bacci ta farka, tare da bud'e Idanunta arazane, saboda sautin kukan mijin nata da taji.

Ganinsa da tayi azaune yana kukanne kuma, yasa ta matsowa inda yake tare dasa hannunta ta dafa shoulder d'insa.

Tabbas tasan abunda yakesa mijinta kuka, alokuta daban daban, musamman ma dai Idan tagansa a irin wannan yanayin.

Araunace kuma cikin sanyin da jikinta yayi tace.

“Abban Hafeez.”

Jin muryar matar tasa acikin kunnuwansa ne, yasa shi dagowa ya kalleta lokaci daya kuma, ya maida kansa ya d'ora acinyarta.

Cikin muryarsa dake fitar da Amon kuka yace.

“Dijat zanyi rashi biyu asanadin rashi d'aya, nayi rashi d'aya acikin shekaru 22 da suka wuce, sannan kuma sanadin wancan rashin, zan sakeyin wani rashin anan kusa, Dijat Ina kukane saboda inason y'an uwana, banason rasa su, amma ya zanyi Dijat nasani dole zamu rabu, k'addara da jarrabawar Ubangiji zata rabamu,  inajin nauyin wannan abun azuciyata kullum.”

Ajiyar zuciya Aunty Dijat din ta sauke, cikin kuma so da tausayin mijinta tace.

“Kayi hakuri Barrister Tabbas kowacce rayuwa da irin k'addararta, amma Insha Allah babu wanda zaka sake rasawa.”

“Dole zan rasa Dijat nina sani lallai dole zan rasa, rashin da nayi shekaru 22 da suka wuce, shi zaisa na sakeyin wani rashin ayanzu. Maraicin Jannart nake dubawa Dijat, Maraicin Jannart maraicine da yake cike da abubuwa masu tarin yawa,  haka kuma maraicine da yake buk'atar tausayawa da jin k'ai,  Ina matuk'ar tausayin Jannart....”

Ya kare maganan still cikin kuka, wanda hakan yasa Aunty Dijat soma shafa bayansa ahankali, kuma cikin lallashi take tausasa sa.

Rayyern kuwa dake Jin duk wani abu dake faruwa acikin wayar, idanunsa ya rumtse da k'arfi, saboda wani irin masifaffen raunin da yaji ya lullub'esa haka nan yaji wani irin tausayin Jannart da Barrister Kabir keta nanata maraicinta.

Tabbas bazai iya jurewa jin abubuwan da suke fad'ad'in ba, wanda hakanne kuma ya sashi zare

wayar daga kunnensa, tare da katse k’iran gaba d’aya.

Ahankali kuma cikin dogon tunanin daya fad’a, ya juyawa tare da zubawa Jannart din dake kwance idanu hannunta ya manna kan bakinsa tare da lika mata wani sassayan kiss.

Filla filla kuma haka yakejin maganganun Barrister Kabir na dawowa kunnuwansa.
Babu kuma abunda yafi tsaya masa arai, kamar Maraicin Jannart din, da yaji Barrister Kabir din nata ambata.

Asanyaye cikin kuma tsananin tausayinta da yaji ya dirar masa azuciya, ya ronk’ofo jikin.

Lallausan tafin hannunsa ya d’aura akan goshinta, wanda yaga yana ta tsatstsafo da gumi, ahankali ya share mata gumin, tare kuma dasa Y’ar yatsarsa ya gyara mata, dogon gashinta wanda ya d’an rufe mata gefen fuskar ta.

Still kuma duk abunda yakeyi din idanunsa, nakan kyakkyawar fuskarta wacce tayi fayau, ga kuma zara zaran gashin Idanunta wanda suka baje, suka kuma k’arawa fuskarta ta kyau.

Akaron farko yakejin wani irin matsanancin tausayi, da rauninta na ratsa cikin zuciyarsa.

“Maraicin Jannart nake dubawa, Maraicin Jannart yana matuk’ar buk’atar kulawa, da kuma tausayawa.”

Way’an nan  kalaman sukeyi masa yawo acikin k’wak’walwa, wanda har saida hakan yasa shi jin wani nauyi azuciyarsa.

Wannan dalilin yasa asanyaye ya d’an sukuyo da kansa gareta, wanda hakan yasa numfashinsa soma sauk’a akan kyakkyawar fuskarta.

Ahankali kuma cikin tausasa murya yace.

“Allah ya baki lafiya My Janna.”
ya kare maganan nasa da tausayawa.

Ahankali kuma ya jawo kujera ya zauna akusa da ita, cikin dan yanayin sanyi ya kamo hannunta na dama ya rik’e acikin nasa.
Wanda hakan yasa tafukan hannayensu had’ewa awaje d’aya.

Wani irin d’umin dad’in da yaji ne kuma yasa shi, kwantar da kansa agefenta, tare kuma da d’aukan hannun nata, ya d’aura ak’asan hab’arsa.

Idanunsa ya lumshe  anutse kuma yake shak’an, daddad’an k’amshin turaren dake tashi ajikinta.

Almost 5mn suna nan ahaka, Yayinda Jannart din keta baccinta cikin nutsuwa.

Shikuwa Rayyern ahankali yake d'an yawo da bayan hannun nata akan fuskarsa, har dai ya gangaro zuwa kan lallausan sajensa.

Idanunsa ya kuma lumshewa adai-dai lokacin, da ya kawo hannun nata saitin bakinsa, ba tare da zato ko tsammani ba kuma, saiji yayi ya d'aura mata sassayan kiss akan bayan hannun nata a karo na biyu.

Jin abunda yayi dinne kuma yasa shi sake lumshe idanunsa, ahankali ya janye hannun nata zuwa kan hab'arsa.

Itakam Jannart duk batasan ma meya keyi ba, saboda baccinta kawai takeyi.

To shima Rayyern din dai ahaka bacci ya d'aukesa, yana rungume da hannunta, yayinda kansa kuwa ke manne ajikin gadon nata.

Bacci sukeyi sosai saboda dama tuni dare ya raba, musamman ita Jannart wanda akayiwa allurar bacci, saboda ta sanadiyar baccinne numfashi da kuma bugun zuciyarta zasu dai-dai-ta.

*5:00am.*

Ahankali take d'an motsa jikinta, wanda takejin yayi mata nauyi sosai, cikin sanyi da kuma kalasar dake damunta, ta bud'e Idanunta wanda sukafi kama dana y'an maye.

Da sauri tasa hannu ta dafe saman marar ta, da takejin ya cika saboda tsananin fitsarin da takeji, wanda kuma shine ya tasheta daga baccin da takeyi.

Ahankali ta d'an juya Idanunta gefe, inda ta sauke ganinta akansa.
Bacci yakeyi atsanake still kuma hannunta na cikin nasa, wanda ya rik'e gam tare da d'aura kansa akai.

Idanu ta d'an zuba mishi hade dajan dogon numfashi, saboda har yanzu akwai oxygen akan hancin ta, saidai tuni numfashinta ya dai-dai-ta.

Ahankali tasa d'ayan hannunta ta tab'a oxygen  din, cikin kuma wani irin yanayin dake nuna bata wani hayyacinta sosai, saboda alluran baccin da bai gama saketa ba.

“Naaaaaannnnn!!!”

Ta kira sunansa cikin sassayan murya, tare dajan dogon numfashi.
Still kuma Idanunta na ci gaba da rufewa, kamar wata y'ar maye.

“Naaaannn!!!”
Ta sake kiran sunansa asanyaye.

Rayyern kuwa acan cikin baccin nasa, ya d’anji sautin muryarta sama sama, hakan kuwa shi yasa ya bud’e idanunsa.

Ganin idanunsa abud’e ne kuma, cikin yanayin mayen baccin da baigama sake shiba yace.

“Janna, kin tashi ya jikin naki?”

Idanunta dake bud’ewa da rufewa ta d’an juya, kana asakalce cikin kuma yanayin marassa lafiya tace.

“Da sauki, please Naan kacire min wannan abun numfashina ya dai-dai-ta.”

Tayi maganan tana me nuna oxygen din.

Shikuwa Rayyern jin hakanne yasa shi, d’an rank’wafowa kanta tare dasa hannusa ya dafa saman kirjinta  atsanake yaji numfashin nata na tafiya.

Wanda hakanne kuma yasa shi gangaro da hannun nasa, saman mak’oshinta saboda yanason yaji  bugun zuciyarta.

Akokarinsa nayin hakanne kuma, lalausan tafin hannunsa ya sauk’a asaman breast dinta, batare daya sani ba.
Wani irin masifeffen abu yaji yana bin dukkan jijiyoyin jikinsa, wanda haka yasa ya
D’an d’ago da sauri  ya kalleta, kana cikin tausasa murya dason shagwab’ata yace da narkewa da shima yayi yace.

“Bugun zuciyarki bai gama dai-dai-ta ba Janna, ki d’anyi hakuri kinji.”

Kai ta d’an jinjina masa kana cikin kasala ta zare oxygen din akan hancinta, ashagwab’e kuma tace.

“Naan zanyi fitsari.”

“To.”
Ya fad’a tare da k’arasa zare mata oxygen din, dai dai ta yunk’ura zata tashi ne kuma, Rayyern din ya saka hannayensa duka ya tallafota,tare da zaunar da ita akan gadon.

Saidai kuma yana zaunar da ita, yaga ta tafi luuuuu zata kwanta, alamun tana cikin magagin bacci.

Da sauri ya tallafota ta fad'a jikinsa, idanu ya d'an zuba mata ganin yanda jikinta ke rawa ne kuma, yasa shi rungumeta tsam ajikinta.

Pat-pat haka zuciyarshi take harbawa.
"Yah salam".
Ya faɗi a cikin zuciyarsa domin yaune karo na forko da yayi mata irin wannan ruggumar murya a narke can ƙasan maƙoshinsa.
"Janna."
Ya kira sunanta cikin dan tausasa murya.

Jannart kuwa jinta ajikinsa ne yasa ta sake narkewa, tare da lumshe Idanunta.

Cike da sabon shagwab'a tace.

"Naan zanyi fitsari."

"To muje na kaiki toilet tunda naga kaman baccin bai gama sakeki ba."

D'an k'aramin bakinta ta turo gaba, tare da cewa.

"A'a zan iya zuwa da kaina."

"Bazaki iya zuwaba Janna muje na kaiki."
Ya fad'a cikin serious, tare da kamo hannunta ta sauko daga kan gadon.

Bisa jagorancinsa kuma suka nufi toilet din dake cikin dakin.

Shiya bud'e mata k'ofar toilet din ta shiga, har ta saka k'afarta acikin toilet din kuma saita dakata, tare da juyowa ta kalleshi da maraitattun idanunta.

Gane abunda take nufi ne kuma yasa shi, d'auke kansa gefe tare da cewa.

"To kiyi fitsarin mana."

Bakinta ta d'an turo gaba, cike da salon shagwab'a tace.

"a'a nidai ka fita."

Idanunsa ya d'an jujjuya saboda Jin abunda ta fad'a, Ahankali kuma yace.

"Ok ashe abun babu dadi kenan."

Da sauri tayi k’asa da kanta, saboda gane abunda yake nufi.

Shikuwa Rayyern kansa kawai ya girgiza, batare kuma daya sake cewa komai ba, ya juya tare da sakar mata kofar ya fice daga cikin toilet din.

Ganin hakan da tayi ne kuma yasa ta, tsugunnawa tayi fitsarin, Koda ta gama alwala tayi, saboda tasan zuwa yanzu lokacin sallan asuba yayi.

Bayan ta idar da alwalanne kuma, ta Mike asanyaye ta murda handle din kofar ta fito.

Tana fitowa dinne kuma sukayi karo dashi, saboda dama bai bar jikin kofar ba.

Da sauri tayi baya baya kaman zata fad’i, Ganin hakanne kuma yasa Rayyern din rik’ota, tare da jawota ya zaunar da ita akan gadon.

Idanunsa ya dan zuba mata, Ganin hakanne kuma yasa ta lumshe nata idanun, tare da bud’e bakinta ahankali tace.

“Naan Zanyi sallah.”

Dan karamin bakin nata dake matsowa ahankali ya kalla, Cikin kulawa yace.

“Janna anan babu sallaya, kuma kinga ko hijab babu, amma kijira bari na duba Dr. Imran tunda shi Musulmi ne, nasan baza’a rasa sallaya ba, amma samun hijab kam zaiyi wuya.”

Kai ta d’an langwab’ar kana ahankali tace.
“To ai mayafina ma zaiyi sallah idan na nad’ashi ya rufe duk gashina, kuma kayana baya nuna jiki.”

Yanayin yanda ta k’are maganan tana lumshe Idanunta ne, kuma yasa shi jinjina kai.

Saidai batare daya sake cewa komai ba, ya shige cikin toilet din dake cikin dakin.

Al'wala ya dauro, bayan ya fito daga toilet dinne kuma, ya dan kalleta tare da cewa.

“Bari naje nayi sallah, Idan na dawo sai kiyi naki sallan.”

Kai ta jinjina masa tare da maida jikinta ta kwanta, akan gado shikuwa Rayyern ficewa daga cikin dakin yayi.

Kaitsaye kuma Dan madaidaicin masallacin dake cikin Hospital din ya nufa.

Koda yaje ya samu har an idar da sallah, hakan yasa shi kad’ai yayi nasa sallan.

Bayan ya idar da sallan ne kuma, direct ya wuce office din Dr. Imran.

Yana isa bakin office din kuwa, suka hadu da Dr. Imran din.
Cikin mutum tawa sukayi musabaha, kana fuska asake Dr. Imran din yace.

“Ya jikin Madam din, yanzu nake rayawa araina cewar zanje na duba ta.”

Murmushi Rayyern din yayi, tare da cewa.

“Alhamdulillah jikinta yayi sauki sosai, yanzu ma ta tashi wai tanason tayi sallah ne.”

Murmushin Jin dadi Dr. Imran din yayi, kana cikin farinciki yace.

“Masha Allah ai indai ma numfashinta ya dai-dai-ta, to zaku iya tafiya gida babu wani matsala, yanzu muje na duba jikin nata mugani.”

“To.”
Dr. Rayyern din yace tare da juyawa, suka nufi dakin da Jannart din take.

Suna shiga kuwa suka sameta akwance, saidai kuma ganinsu da tayi ne yasa ta tashi zaune.

“Mrs Rayyern sannu ya jikin naki?”
Dr. Imran ya fad’a yana me kokarin, d’auke oxygen din dake kan gadon.

Jannart kuwa jin sunan da ya kira ta dashi ne, yasa tayi kasa da kanta Ahankali kuma cikin sanyi tace.

“Da sauki sosai.”

“Masha Allah haka akeso ai, Allah ya kara afuwa, yanzu babu wani abu dake yi miki ciwo kenan?”

Kanta ta gyad’a alaman “Eh”

Hakanne kuwa yasa Dr. Imran juyowa ya kalli Rayyern.

“Doctor zaka iya daukanta ku tafi gida babu matsala, saidai kaman yanda kasanine mai asthma dole sai anayi ana kiyayewa, sannan ka tafi da way’annan alluran guda 5 kullum, guda d’add’aya zaka na yi mata.”

Kai Dr Rayyern din ya jinjina tare da karb’an alluran, ya rik’e.

Jannart kuwa jin ance allurai za’ana yi mata ne, yasa ta juyo ta kalleshi, araunace da kuma yanayin tsoro tace.

“Naan allurai za’ana min kuma”.

Ido ya d’an zuba mata tare da gyaɗa mata kai.

Cikin yanayin sanyi tace.

“Abba na ya hana amin  allura kawai abani magani.”

Idanunsa ya d’an zuba mata Ganin kuma da gaske batason alluranne, yasa shi gyara tsayuwarsa tare da cewa.

“Janna dole ai miki alluran sune zasu taimaka miki ai wajen samun sauki, ko bakyason ki rabu da asthma dinne?”

Still rau-rau tayi da idanu, tare da soma kunkuni acikin zuciyarta, saboda harga Allah ita batason allura dama a dole Dr Lukman keyi mata data samu Abbanta ya hana kuma ta huta.

Dr. Imran kuwa ganin suna magana da wani, yaren da baisani bane yasa shi, sakin murmushi tare da mikawa Rayyern din takardar sallama.

Rayyern kuwa bayan ya karb’i takardar, hannun Jannart din ya kamo.

Cikin yin k’asa da murya yace.

“Muje ko.”

Babu musu kuwa ta kama hannun nasa, saboda har yanzu jikinta babu kwari, sannan kuma idanunta basu daina rufewa ba saboda bacci.

Ahaka dai suka fito daga cikin Hospital din.

Inda Dr. Imran ya rakosu har bakin mota.
Saida yaga tashin motarsu kuma, kafun ya koma cikin asibitin nasa.

Su kuwa su Rayyern Koda suka dau hanya, shagwab’a sosai Jannart din take tayi, tare kuma da wasu irin sambatu wanda shi baisan ma na meye ba.

Saidai duk abunda takeyi yana kallonta, ta gefen idanunsa, yanayin yanda take abubuwan nata ne kuma, yasa shi fahimtar cewa har yanzu alluran da akayi mata dinne bai gama sake ta ba, shine kuma ke sawa tana sambatu, kasancewar bata samu isashshen bacci ba.

Kaitsaye gida suka nufa, suna zuwa kuwa ya yi parking motar, tare da fitowa ya zagayo b'angaren Jannart din ya fito da ita.

Yana rike da hannunta haka suka nufi cikin gidan.

Koda suka kawo bakin kofar falon, hannunsa ya d'aura akan security door din, tare da danna wasu numbers, almost 4 minute glass din ya nuna masa reguest.
Ganin yadda take layine, yasashi gyara tsayuwar sa tare da manna bayanta da k'irjinsa kana ya d'an zuro kanshi ta kan habarta na dama.
Hannunta ya kamo ahankali ya daura akan glass din,  take kuwa duk na'urorin wajen suka amsa, inda sunanta ya bayyana b'aro b'aro ajikin d'an na'urar.

Idanunta ta d'an zaro tana Kallon abun.

Dai-dai lokacin kuma na'urar ta rubuta, Accepted.

Zare hannunta daga kan na'urar yayi, Ahankali kuma yace.

"Sake d'aura hannunki."

"To."
Tace tare da d'aura hannun nata, take kuwa saiga kofar ta bud'e.

Kallonsa tayi da mamaki,  shikuwa Rayyern gefenta ya rab'a tare da wucewa Cikin falon.

Ganin hakanne kuma yasa itama ta rufa masa baya.

Koda suka shiga falon zama tayi akan kujera, Yayinda shi kuwa ya wuce bedroom dinta, ya d'auko mata hijab da sallaya.

Koda ya dawo anan cikin falon ya shumfud'a mata sallayan, tare kuma da mika mata Hijab din.

Kana ya koma gefe ya zauna, itakuwa Jannart ganin hakanne yasa, Ahankali ta tashi tsaye, tare dasa hijab din ta tada sallah.

Shikuwa Rayyern wayarsa ya d'auka, yayi musu ordern abinci.
Bayan ya gama order ne kuma ya ajiye wayar, tare da maida kansa ya jingina da jikin kujera, Ahankali yake Kallon fararen tafin k'afarta, kasancewar tana zaman tahiya ne.

Jannart kuwa tana gama tahiyan ta sallame sallan, tare da jingina ta kwanta akan sallayan.
Ahankali kuma ta lullub'e duk jikinta, da hijab din nata, tare da maida Idanunta ta lumshe.

“Ya jikin naki?”

Ya tambaya yana me Kallon kyakkyawar fuskarta.

“Da sauki.”
Ta amsa masa batare da ta bud’e Idanunta ba.
Saboda wani irin bacci takeji yana fusgarta.

Dai-dai lokacin kuma aka soma knocking kofar falon, Ahankali ya  mike tare da k’arasawa ya bud’e kofar falon.

Kamar yanda ya tsammata kuwa abincin da yayi order ne ya iso,  bayan ya k’arbi abincinne kuma ya dawo falon.

Akasalance ta Dan bude Idanunta ta kalleshi, cikin sanyi da kuma kasala tace.

“Naan zanyi bacci.”

D’an rank’wafowa Kanta yayi ahankali, kuma cikin tausasa murya yace.

“Okay amma tashi kici abinci, Idan nayi miki allura saiki kwanta kinji...”

Bakinta ta turo gaba, tare da Dan yi masa kallon wannan mugunta zaimin mai kama da shagwab’a tace.

“Allura da sanyin safiyan nan, Naan kayi haƙuri dan Allah sai anjima  bayana ma ciwo yake.”

Ta kare maganan tana me daura hannunta, akan hips dinta.

Rayyern kuwa Ganin hakanne yasa wani, irin sihirtaccen Murmushi kwace masa, ahankali kuma ya zauna akusa da ita.

“Don’t worry alluran ai ba abaya akeyinta ba, a hannune malama.”

Ya fad’i hakan yana me danne dariyar dake ransa, tare kuma da soma bud’e ledodin restaurant din dake hannunsa.

Jannart kuwa jin hakanne yasa ta tashi ta zauna, cikin sigar shagwab’a tace.

“Ayyah Naan ni hannun nawa ma ai ciwo yake, duk karkarwa ma yake bazai iya tsayuwa waje daya ba, kuma ni banason allura ya karyemin ajiki.”

Takare maganan tana me d’an yin mui-mui da k’aramin bakinta.

Rayyern kam dariyarta gaba d’aya duk ta kamasa amma saiya danne, saboda tunda yake bai tab’a ganin mai tsoron allura irinta ba.

D’agowa yayi ya kalleta.

“Da wani idanunta kamar na y’an shaye shaye.”

Ya fad’i hakan acikin zuciyarsa.

Azahiri kuwa takeaway din abincin ya turo gabanta, tare da zuba mata narkakkun idanunsa.

Cikin kulawa yace.

“Oya eat idan kuma ba haka ba, To ya zama lallai dole sai anyi miki allurai guda biyu kuma in sossoka miki su da k’arfi.”

Da sauri ta zazzaro Idanunta, lokaci daya kuma ta k’wabe fuska tamkar zatayi kuka,  badan taso ba kuwa haka ta dauki spoon ta soma tsakalan abincin.

Rayyern kuwa Idanu ya zuba mata, tare da harde hannuwansa akirjinsa.

Ganin hakanne kuma yasa ta d’an tuttura abincin bisa dole badan taso ba.

Bayan ta danci kadan ne kuma ta ture abincin gefe, tare da kwaɓe fuska cikin murya kaman zatayi kuka tace.

“Ni nakoshi.”

“Yauwa to sai allura kuma ko?”

Rayyern din ya fad’a yana me  gyara zamansa, tare da d’auko daya daga cikin alluran.

Da sauri ta matsa nesa dashi, cikin dan yanayin roko, hawaye har yana fita daga Idanunta tace.

“Please Naan, Dan Allah kar kamin alluran yanzu, ka bari sainayi bacci na tashi kaji, please kaji Naan...”

Ta kare maganan tana me yarfa yan yatsun hanunta, cike da tsananin tsoro.

Idanu Rayyern din ya zuba mata, aransa yana me matuk’ar mamakin irin yanda Jannart din, take matuk’ar tsoron allura.

Fahimtar yanda duk take atsorace ne kuma, yasa shi dan tausasa murya.
Cikin kulawa yace.

“Kwantar da hankalinku Naji bazanyi miki allura ba, tashi kije ki kwanta.”

Ajiyar zuciya mai karfi ta sauke, saboda Jin abunda ya fad’a d’inne kuma yasa, ta Dan lumshe Idanunta tare kuma da matsowa kusa dashi, murya araunace tace.

“ai bazan iya tashi ba, anan zan kwanta, jikina duk babu karfi.”

“Kinason sanyi ya sake kamaki ne? Ko kinason na miki allura, maza tashi muje daki.”

Ya fad’a yana me mik’a mata hannunsa.

Da sauri ta kama hannun nasa ta Mike tsaye, saidai tana tashi din taji jiri na neman kada ita, wanda hakan yasa da sauri Rayyern din ya tallafota, tare da kwantar da ita ajikinsa.

Batare kuma daya jirayi wani abu ba, kaitsaye ya nufi bedroom d’insa da ita.

Ita kuwa ganin sun nufi bedroom din nasa ne, yasa ta karya fuska tare da d’agowa ta kallesa. Ashagwab’e tace.

“Naan dakinka kuma? ka kaini bedroom dina mana....”

“Shiiii ni bazan iya kaiki bedroom dinki ba, kinji nauyinki kuwa saikace na buhun masara, taya yama mai nauyi kaman na doki, zai dauki mai nauyi kaman na buhun masara.”

Ya fad’i maganan yana me matse hannunta dake cikin nasa.

Da sauri ta kalleshi, saboda ta tabbatar abubuwan da tayi masa ne yake ramawa.

Bakinta ta turo gaba cike da shagwab’a kuma, ta d'an muntsineshi wai ko zaiji zafi ya sauk’eta.

Duk da yajita amma bai kulata ba, ahaka har suka k’araso cikin d’akin nasa.

Suna shiga ya direta abakin gado, tare da komawa ya zauna yana meda numfashi, kamar wanda yayi aikin karfi.

Wanda kuma yanayin hakanne kawai son rai, bawai Dan tana da nauyi ba, Dan hasalima Koda ya dauketa ji yayi kamar ya daga Y’ar shekara 13 ne.

Itakuwa Jannart ganin hakanne yasa ta, sake shagwab’ewa tare da zamewa ta kwanta akan

gadon.

Kamshi da kuma laushi da taushin gadon nasa ne kuma, suka sa tana kwanciya bacci ya dauketa.

Yanayin yanda yaji saukan numfashinta, alaman tayi bacci ne kuma yasa shi tashi, ya gyara mata kwanciyarta tare da rufa mata blanket.

Kaitsaye kuma ya fita daga d'akin.
Inda ya koma falo yaci abinci.

Bayan ya gama cin abincinne kuma ya sake dawowa dakin, kasancewar yau din weekend ne babu aiki.

Ahankali ya d'an zauna abakin gadon.

Dai-dai lokacin ita kuma ta Dan bud'e Idanunta, cikin magagin baccin da take ciki hadi da shagwab'a tace.

"Naaan ni zan koma dakina."

"To Malama ki koma dakin naki mana."

Rayyern din ya fada yana me kallonta, tare da zamewa ya kwanta akan gadon.
Wanda kuma duk abubuwan da takeyi din yasan ba a hayyacinta take ba.

Itakuwa Jannart acikin magagin nata, Ganin ya kwanta akan gadonne yasa ta cewa.

"Ni gaskiya bazan kwanta dakai akan gado daya ba."

"To ki sauka kasa mana, kona rikeki ne?"

Rayyern din ya fad'a yana me gyara kwanciyarsa.

Itakuwa Jannart jin hakan yasa ta soma kokarin tashi, ashagwab'e kuma cikin yanayi mai kama da mayen da take ciki ta fad'a Kan...!

😂😂😂😂😂😂😂💃🤸🏻‍♀️🤝🏻💃😘😘😍😍😘😘🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️

*GARKUWAR taku ce dai MA'AURATA, da masu shirin aure, da masu jego, da yan gayu masu son k'amshi kece raini, da gyaran da zaike  maimaita muku dararen forkon kuruciya*

Ko kunsan Jikinmu na da sinadaran hormones da suke taimakawa dan'adam akan komai musamman lokacin da mace take mu'amalar aure da mijinta. Mafi akasari wannan hormones din ne ke samun matsala ko su yi sanyi koma su daina aiki kwata-kwata shi ne dalilin da zai sa mace tace bata jin sha'awa ko bata san dadin aure ba. Albishirinku ina da kayan da ke taimakawa wannan sinadaran du dawo aiki tukuru don karkato miki da kimarki wajan mai gida sannan su taimakawa wannan sinadaran hormones dinki su dinka secreting din ni'ima wadatacciya da zata taimaka miki ki gamsu mijinki ya gamsu fiye da tunaninki. Note: Kayana ba sa tsinka ruwan ni'ima suna dai taimakawa hormones dinki ne su tsattsafo da ni'imar musamman wacca cutar sanyi ko dattin mahaifa ya dankarar da su ya hana su yin aikinsu yanda ya kamata. Haka zalika idan kina da kyau ki kara da wanka. Zaki iya amfani da magani na na gargajiya wanda zai gyara miki sex hormones din kullum ki kasance cikin humidify wato cikin damshi mai albarka kamar yanda ake son mace. Yana gyara miki mara.

Sai kamshi. Hajiyata daure ki fara amfani da turarena ki ji irin salon kamshin sa salo ne da zai daidaita ki da mijinki ya kankaro miki da kimarki a wajansa. Siyan na gari mayar da kudi gida.

Ga masu buƙata ga number' wayata wanda nake whatsApp dashi 09097853276 kimin mgn ta whatsApp in har kin tabbatar kin shirya saya mu dai-dai ta, kayana ba ƙanana bane, shiyasa bana harkan karanta, muddin kinsan baki shirya sayaba Please kada kiyi min mgn ki bari sai kin shirya kuɗinki a hannu,  ba ina nufin kayana bana talaka bane, no akwai ƙananan set na masu karamin karfi, banson aimin mgn a ɓatamin lokacin aiyukana a shirme baki shiryaba. Shine karantan da bana so.
0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU. In kin shirya ga number ta ga kuma account number ta wanda in mun gama mgn zaki turo kudin ki, kana insa miki kaya a mota, duk ƙasar da kike kayana zaije gareki, amman fa in kinada dalilin zuwan nasune🤝🏻sayan na gari meda kudi  gida.

GARKUWAR MA'AURATA

By
*GARKUWAR FULANI*

22/12/2021, 19:59 - 🥰🥰: Motsa kafafunshi ya danyi baya kaɗan domin ji da yayi bugun zuciyarsa na tsananta.

"Ruwa zan sha."
Ta fad'a cikin wata muryar shagwab'a.

Idanunsa ya d'an lumshe saboda wani fitinannen, kamshinta daya bugi hancinsa.

D’an matsawa gefe yayi, batare kuma daya ce mata komai ba, ya rab’a ta gefenta, wanda har hakan yasa jikinsa d’an gogan nata jikin,  kaitsaye kitchine din ya wuce.

Yana shiga kuwa ya bud’e murfin fridge, goran ruwa guda biyu ya d’auko, kana ya dawo cikin falon, Tana nan tsaye ayanda ya barta, saidai ta kuma rik’e hab’arta.

K’arasowa wajen nata yayi, tare da mik’o mata goran ruwan, cikin silent voice yace.

“Take it, then go to sleep now, ko na jimiki ciwo ne?”

Yanayin yanda yayi maganan nasa ne cikin tauyawa da tausasawa, yasa duk taji tsikar jikinta na mimmik’ewa, Ahankali ta girgiza masa Kai, kana cikin sanyin murya tace.

“Zafi nakeji.”

Ta k’are maganar tana me nuna masa gefen lips dinta, da ya d’anyi ja.

Idanunsa ya d’an tsurawa Lips din nata, saboda yanda yaga Suna shek’i, d’an kawar da idanun nasa kuma yayi Ahankali,  kana cikin sanyi yace.

“Babu ciwo awajen, zuwa anjima zai daina zafi sannu ko sorry ban san dake a wurin bane.”

Yayi maganan yana me Kallon wuyanta.

Ita kuwa Jannart jin abunda ya fad’ane ya sata karb’an bottle water’n, da yake mik’o mata tare da juyawa, cikin sanyi ta nufi bedroom dinta.

Da idanunsa ya bita, har saida ya ga ta shiga cikin bedroom dinta, kafun ya juya shima ya nufi nasa bedroom din.

Yana shiga ya sawa kofar key,  maganinsa ya b’alla yasha, kana ya koma ya kwanta.

Koda ya lumshe idanunsa still k’amshin turaren nata yakeji, acikin hancinsa,  dan gyara kwanciyarsa yayi, batare kuma daya baya wani tunani daman shigowa, cikin kwakwalwarsa ba bacci ya d’aukesa.

Haka itama Jannart tana shan ruwan, kwanciya tayi cikin mintuna kad’an kuwa bacci ya dauketa.

Acan b’angaren Ramadan kuwa Koda suka gama waya, da Hamman nasa Whatsapp dinsa ya shiga, Ganin Riyyam  da yayi a online ne, kuma yasa suka fara chat, ananne kuma ya turawa Riyyam  din numbern Rayyern, Wacce yake amfani da ita anan Mascow din.

Washegari.

Yau ya kama Sunday, tunda Rayyern ya bar gidan kuwa bai dawo ba,  domin can cikin garin ya shiga, Saboda akwai wasu Frnd's d'insa da sukayi karatu tare, yaje sun danyi wani taro.

Jannart kuwa yauma ad'aki ta wuni, saboda duk kwana biyun da ciwon Mara take wuni shiyasa fitan ma, bai wani dameta ba duda bata jin hakan don al'adarta zata zo tayi mmkin hakan daya fara mata yanzu.

***

After five days ago.

Ahaka sukeyin rayuwarsu ta yau da kullum, komai na tafiyawa Rayyern yanda yake so, saidai zuwa yanzu gaba daya abubuwa sunyi masa yawa.

Haka ma Ab'angaren Jannart rayuwarta take ita d'aya, tun daga daren ranar kuwa bata sake saka Rayyern din a Idanunta ba.
Iyaka ya ajiye mata abinci tazo taci.
Da hakanne kuma kowannensu yake sanin, lafiyar d'an uwansa ta haka suke sanin zaman juna.

Acan gida Nigeria kuwa, abubuwa duk suna tafiya yanda ya kamata, musamman a company babu wani mishkilan da ake samu dan Rayyern yana aikinsa da kyau ta yanar gizo-gizo kana ga amintattun ma'aikata, haka asibitin ma Ramadan yana iyaka kokarinsa sosai.

Ko yanzu dawowansu daga masallaci kenan, shida Abban nasa.
Bayan sun shigo cikin falon ne kuma, Ramadan din ya nufi sama.

"Ramadan."
Abba ya k'ira sunansa.

Jin kiran Abban ne kuma yasa  Ramadan juyowa, tare da dawowa ya zauna acikin falon.

Kallonsa Abban yayi kana Cikin sakin fuska yace.

"Karna manta ban Gaya maka ba, dazu iyayen Rayhanna sun kirani, sun kuma shaidamin cewar, sun baka auren yarsu, kamar yanda muka buk'ata, sannan kuma sun bamu lokaci, amma Idan son samu ne ayi bikin kafun watan Ramadan yazo."

Idanu Ramadan ya dago ya kalli Abban nasa, cikin tsananin jin dadi da farinciki yace.

"Alhamdulillah Allah Nagode ma."

Yayi maganar cikin manta cewar, agaban Mamy da kuma Abban yake.

Mamy dake gefe kuwa murmushi tayi, saboda ta sani dama Ramadan din yana son aure.

Ramadan kuwa cikin zumudi ya kalli Abban nasa, tare da cewa.

“To Abba yanzu yaushe za’akai kudin sa rana da kayan lefe?”

Kallonsa Abban yayi, baice komai ba saidai aransa yana mamakin, yanda Ramadan din ke tsananin son Aure.

Ramadan kuwa Ganin irin Kallon da, Abban keyi masa ne ya sashi mikewa da sauri, cikin kunya ya haura sama.

Ganin hakanne kuma yasa Abba yin dariya, kana ya mik’e ya wuce part d’insa, inda yabar Mamyn zaune itama tana dariya.

Tana nan zaune kuwa Ramadan din ya sauko, cikin shirinsa tsab, inda yayi kyau acikin riga da wandon jumpern  dake jikinsa.

Kallonsa Mamy tayi, gaba daya farincikinsa abayyane yake, fuskarta dauke da murmushi tace.

“To yau kuma sai ina?”

Murmushi yayi, tare da Dan matsowa cikin yin kasa da murya yace.

“Ayyah Mamy am zanje gidansu Swe....” saurin gimtse bakinsa yayi, saboda ya kusa yin b’aran b’arama.

Mamy kuwa dariya tayi saboda Sarai, ta fahimci abunda yake nufi.

Kanta kawai ta girgiza, shikuwa cikin sauri ya juya ya nufi waje.

Yana shiga mota Ari ya bud’e masa gate, kaitsaye ya cilla hancin motar tasa waje, direct kuwa gidansu Rayhannan sa ya nufa, yana mejin wani irin shauk’i acikin zuciyarsa.

Koda ya isa gidan nasu tarba na mutumci ya samu daga wajen mahaifiyar Rayhannan,   bayan Rayhannan ta fito ne kuma ya tsura mata idanu, baya ko k’yaftawa, kasancewar ta mai kunya ne kuma yasa ta sadda kanta k’asa.

Asanyaye tace.

“Please ka daina kallona hakanan.”

Murmushi yayi tare da gyara zamansa, cikin jin dadi yace.

“Tayaya zaki hana mutun kallon Matarsa? Ke dinfa yanzu gab kike da zama tawa.”

Murmushi tayi tare dasa hannu ta rufe fuskarta.

Haka dai suka sha hirarsu kafun daga bisani yayi mata sallama ya tafi.

Daga gidansu Rayhannan  kuwa gida ya dawo.

Yana zuwa kuwa ya samu Baba Maud’o zaune abakin gate.

Da sauri ya k’araso wajen Baba Maud’on, cikin sakin fuska da dokin da har yanzu bai gama sake shiba yace.

“Baba Maud’o an bani Rayhanna, d’azun Abba yake fadamin.”

Murmushi Baba Maud’o yayi tare kuma da Kallon Rayyern din, jikin taya shi murna yace.

“K’warai kuwa Ramadan nasani, Abbanku ya fad’amin na tayaka murna sosai.”

Murmushi mai kama da Dariya Ramadan din yayi, tare da juyowa ya fuskanci Baba Maud’o, kana ransa asake yace.

“Baba Maud’o na kasa b’oye farinciki na, hankalina ya kwanta, yanzu bani da wani sauran fargaba,  kana min addu’a please Baba Maud’o, Allah yasa albarka acikin had’innan.”

Murmushi Baba Maud’o yayi wanda har saida sautin ta, ya fito fili cikin sakin fuska yace.

“Insha Allah Ramadan, addu’a kuma kullum inayinta, Allah yasa matarka ce ya kuma kawar da duk wani fitina.”

“Ameen Ameen.”

Ramadan din ya amsa, tare da mikewa kaitsaye ya nufi cikin gidan nasu, kasancewar dare yayi kuma bacci yakeji.

Washegari.

*Mascow*

Ahankali yake driving motar da yanayinsa, dake bayyana tsananin gajiyar da yake d'auke da ita da yunwa.

Kaitsaye gida ya nufa, dai-dai ya hau wani titi ne kuma, wayarsa dake gefe ta soma kara alamun shigowar kira,  share wayar yayi, kamar bazai d'aga ba kuma sai ya d'auki wayar, Ganin sunan Abbansa ne kuma ya sashi d'aga wayar da sauri.

Tare dayin Sallama.

Daga can b'angaren Abba ya amsa.

Shikuwa Rayyern din cikin sanyi yace.

“Abba yasu Mamy da Baba Maud'o.”

Abba dake zaune afalo gyara zama yayi, tare da cewa.

“Duk Suna lafiya, Mamynka tace agaisheka, ya Jannart take?”

sake gyara zaman wayar akan kunnensa yayi, kana cikin nutsuwa yace.

“Lafiyanta Qalau.”

Kai Abban ya jinjina tare da cewa.

“Masha Allah To bata wayan mugaisa.”

Jin abunda Abban ya fad'ane kuma yasa shi, danna Horn din motarsa, cikin dan ladabtar da murya yace.

“Abba bana gida, amma yanzu nake kokarin komawa.”

Daga can b'angaren kuwa jin Karan Horn din mota ne, yasa Abban yarda da abunda Rayyern din yace, cikin jaddadawa yace.

“Shikenan babu damuwa, Idan ka koma saika had'ani da ita.”

“To Abba Allah Yasa kada na manta.”

Jin abunda Rayyern din ya fad'ane kuma, yasa Abban yin shiru, Cikin d'an yanayin bacin rai yace.

“Rayyern!”

Da sauri ya amsa da
“Na’am Abba.” domin jin yadda Abban ya kirashi ba wasa

“Rayyyern!!”
Abban ya kuma kiranshi a dake.
“Na’am Abba.”
Still Rayyern din ya sake amsawa cikin fargaban umarnin da za'a bashi ko fada

Abban kuwa ransa ab’ace yace.

“Rayyern ni kake cewa, Allah yasa kada ka manta hadani da matarka?”.
Da sauri ya jujjuya kansa tamkar yana gaban Abban.
Shi kuwa Abba cikin dakile murya yaci gaba da cewa.
“Bansan Wacce irin rayuwa kakeso kayi da yarinyar nan ba, Wacce irin rayuwace haka Rayyern, Jannart matarka ce fa, wallahi wallahi Allah saiya tambayeka, akan hakkinta, baka kyautawa Rayuwarta Rayyern, akan ka afarayin aiki da kasuwanci da karatune? ko kaine kawai ma’aikaci a duka duniyar nan? Meye ka d’auki kanka da bazaka kula da matarka ba? kasani ko yau ka mutu Allah zai kama ka, da rashin sauke nauyinta dake kanka, kuma kasani ban baka ita ka tafi da ita don kayi ta wofantar da ita ba, tayaya zakana irin wannan sakacin, kullum Kai baka gida, baka da lokacinta kenan?”.

Lips d’insa ya d’an taune, cikin sanyin murya yace.

“Abba kayi hakuri...”

“Nayi hakuri dame Rayyern?”.
Cikin girmamawa yace.
“Abba kayi haƙuri akan komai ma na tuba”.
Cikin fada Abban yace. “Bani zaka bawa hakuri ba kasan Wacce zaka bawa hakuri, yarinya tana zaune ak’ark’ashinka amma baka San abunda ya dace ba, tunda ta tafi batayi waya da kowa ba, ka kulleta awaje daya, sannan yanzu Ina maka magana, kana cewa wai Allah yasa kada ka manta, shikenan yayi maka kyau Allah yasa ka manta ɗin!!!”.

Abban ya fadi maganan atsawace, kuma cikin fushi lokaci daya kuma ya katse kiran.

Da sauri Rayyern yabi wayar da kallo, lokaci daya kuma yaji duk zuciyarsa babu dadi, ajiye wayar agefensa yayi, domin dai-dai lokacin ya iso gida.

Yana gama dai-dai-ta parking, ya bud’e murfin motar ya fito.

Hannunsa rik’e da waya da kuma, ledodin takeaway din da yayi musu ya nufi cikin falon gidan.

Yana shiga kuwa ya zauna akan daya daga cikin kujerun falon.

Wayarsa ya dauka ya sake dialing numbern Abban.

Har saida wayan ta kusa katsewa kuwa, kafun Abban ya d'auka.

Jin Abban ya d'auki wayarne kuma yasashi, kwantar da murya cikin sanyi yace.

“Dan Allah Abba kayi hakuri, zanyi yanda kake buk'ata.”

Daga can b'angaren Abba azafafe yace.

“Hakurin me kake bani ne  Rayyern?.”

Rayyern din kuwa sanin halin Abban nasu, Idan har yayi fushi ne yasa shi, sake yin k'asa da murya cikin tausasa harshe yace.

“Naji Abba kayi hakuri Dan Allah! In sha Allah zan kiyaye zanyi yadda kukeso”.

Idanunta ta bud'e da sauri, saboda jin muryarsa da tayi, da dukkan alama kuma tasan waya yakeyi.

Saurin tashi daga kwancen da  take tayi, tare da Kai dubanta ga kofar dakin nata.

Duk yau zaman gidan bayayi mata dadi, saboda kadaici, ga kuma wani irin masifaffen kewa daya cika zuciyarta, tana matuk'ar son tayi magana da Abba Kabir dinta, wannan dalilin yasa ta yanke cewar, Idan ya shigo yau din zata rok'esa aron waya.

Da sauri ta zuro da k'afafunta k'asa, batare kuma da ta damu da shigar riga da wandon dake jikinta ba, kaitsaye ta nufi falon, kanta sanye da hulan sanyi, sai kuma wani bedroom shoe mai kyau.
Riga da wandon dake jikin nata kuwa, bak'aramin bayyana shape dinta sukayi ba, duk da cewar Suna da kauri, amma sunyi mata kyau sosai, Dan saita fito kamar irin y'an matan turawa dinnan, domin saboda tsabar zaman waje d'aya, har wani yellow da ja skin dinta yayi tsabar fari.

Ahankali ta bud'e kofar dakin ta fito.

Tana fitowa kuwa yana sauke idanunsa akanta.

Saurin yin kasa da kanta tayi, tare da karasowa cikin falon.

Shikuwa tun fitowarta ya kasa d'auke idanunsa, daga kallonta saidai fuskarnan tasa  babu

alaman Murmushi.

Ahankali ta zauna akan carpet, tare da nannad'e k'afafunta.

Rayyern din kuwa Ganin ta zauna ak'asan san ne, yasa shi gyara zamansa, tare da kwantar da murya cikin ladabi yace.

“Abba gatanan na shigo cikin gidan.”

Yana gama fadin hakan ya mik'a mata wayan.

Ai kuwa kaman jira take har hannayenta, na rawa  wajen amsar wayar.

Tana karawa akan kunnenta, tayi Sallama.

Abban ne ya amsa mata, cikin kulawa da kuma sakin rai yace.

“Jannart ya kike ya gida, fatan komai da komai lafiya.”

Ajiyar zuciya ta sauke cikin tsananin jin dadi, tace.

“Lafiya k'alau Abba yasu Mamy, Ramadan da Baba Maud'o.”

“Duk Suna lafiya, gama Mamyn naku anan kusa bari na bata.”

Cikin jin dadi Jannart din ta jinjina kai, Jin Mamy ta karb'i wayanne kuma yasa ta karyar da wuya, cikin muryar shagwab'a tace.

“Ina wuni Mamy.”

“Lafiya kalau Jannart dinmu, wallahi munyi kewarki sosai, fatan dai kina nan lafiya.”

Mamyn ta tambayeta cike da kulawa, hadi kuma dajin dadin samun Jannart din.

“Nima nayi kewarku sosai Mamy, nayi kewarku sosai da sosai garin ba dadi sam Mamy, Ina Ramadan?”

“Ramadan yana can wajen aiki, kullum saiya tambayeki.”

Mamyn ta fad'a tana nazartar kalmar Garin ba dadi sam da Jannart ɗin ta fadi, shadar zaman doya da manja sukeyi kenan.

Jannart kuwa Kai ta kwantar kana cikin sanyi, tace.

“Ayya Mamy kice ina gaishe sa, Idan kunyi waya da Riyyam nsra ma kice ina gaishesa.”

“To Jannart Insha Allah zasuji, amma Ina dai babu wata matsala kam?”

Kai Jannart din ta d’an sunkuyar, cikin tausasa murya tace.

“Eh Mamy babu komai.”

“Masha Allah haka akeso ai, amma dai kina kulawa da sanyi, Dan naji ance sanyin garin daban yake dana kowacce k’asa.”

“To Mamy.”
Jannart din ta amsa,  daga hakane kuma sukayi sallama da Mamyn, sosai Jannart taji dadin wayar da sukeyin, musamman taji zuciyarta tayi sanyi.

Acikin kaso 50 na damuwarta duka sun kau, dama matsalarta kewa ne kawai.

Ahankali ta zare wayar akan kunnenta, tare da mik’o masa.

Idanunsa dake alumshe ya bud’e tare kuma dasa hannu ya karb’i wayar.

Itakuwa Jannart maida kanta k’asa tayi, tare da sauke idanunta akan yatsun k’afarsa, wanda taga yana d’an motsa su Ahankali.

Idanu tad’an zubawa yatsun nasa, bakinta kuwa Ahankali yake motsi da alama, wani abu take son fad’a.

Rayyern dake zaune asamanta kuwa, Akasalance ya Kai dubansa gareta, karab kuwa idanunsa suka sauk’a akan saman kirjinta,  kasancewar rigar da ta saka din mai d’an fad’in wuya ne, shi yasa saman kyawawan breast dinta suka bayyana.

Janye idanunsa gefe yayi, tare da maida kansa ya kwantar ajikin kujera.

Itakuwa Jannart d’agowa tayi ta kalleshi, Ahankali ta d’an had’e hannayenta waje d’aya.

Cikin daddad’an murya da kuma sanyin yanayi, mai kama da rok’o tace.

“Ummmm... Dan Allah kakiramin Abbana!!!”

Ta k’are maganan cikin seizing voice, lokaci daya kuma Idanunta suka kawo ruwa.

Yanayin yanda yaji sauti da Amon muryar nata ne, kuma ya saka shi bud’e idanunsa, tare da

Kallon cute face dinta.

Ahankali ya mik’o mata wayar,   ba tare kuma daya ce komai ba, ya maida kansa.

Itakuwa Jannart cikin jin dadi ta mik’e tsaye, da wayartasa ahannunta kaitsaye ta nufi dakinta.

Tana shiga kuwa tayi dialing numbern Abba Kabir.
Cikin sa’a kuwa bugu biyu wayar ta shiga.

Rayyern kuwa Ganin ta shiga daki ne, ya sashi tashi shima ya wuce nasa d’akin, bayan yayi al'wala ne kuma ya wuce masallaci.

Jannart Kuwa tanajin Abba Kabir ya d’aga kiran, ta kara wayar akan kunnenta, lokaci daya taji tamkar zatayi kuka, cike da matsanancin kewa, batare da ta iya amsa sallaman da yayi mata ba tace.

“Nayi kewarka sosai Abbana.”

Daga can b’angaren Abba Kabir kuwa, Jin muryar Jannart d’insa ya sashi lumshe ido, shima cike da tsananin kewa hadi da jin dadin, kiransa da tayi yace.

“Muma haka Jannart dina, munyi kewarki sosai, ya Mascow din, fatan duk kuma nan lafiya.”

“Lafiya K’alau Abbana, yasu Aunty Dijat dasu Hafeez, Allah nayi kewarsu sosai, har ma da Daddy na.”

Ta kare maganan cikin shagwab’a.

“Duk suna nan lafiya Jannart, suma kuma sunyi kewarki, Ina Rayyern din?”

Abba Kabir din ya tambaya, Dan waigawa bayanta tayi, kamar Wacce takesa ran ganinsa sai kuma tace.

“Yana lafiya Abba.”

Kai Abba Kabir din ya jinjina,  cike da jin dadin jin muryoyin juna, haka suka sha  hirarsu,  bayan sun kammala wayar ne kuma ta tashi tayi Sallah.

Shikuwa Rayyern bashi ya dawo gidan ba, saida yayi sallan Isha, Koda ya shigo cikin falon, zama yayi akan sofa tare da d’aukan, abincin daya shigo dashi ya danci kad’an.

Bayan ya kammala cin abincinne kuma ya mik’e tsaye, direct dakinsa ya wuce, yana shiga ya

soma rage kayan dake jikinsa.

Wani fari kal din towel ya d’aura akan waist d’insa, tare da nufar toilet kaitsaye.

Duk da cewar yana jin gajiya sosai ajikinsa, amma hakan bai hanashi yin wanka anutse ba, yana fitowa daga wankan direct gaban dressing mirror d’insa ya nufa.

Wani d’an k’aramin towel ya d’auka, tare da soma goge jikinsa dake jik’e da ruwa, sosai gargasan jikin nasa suka kwanta lub,  ga wani hasken fatarsa daya sake bayyana.

Body lotion kawai ya shafa ajikin nasa, sai kuma turarensa mai dadin kamshi, bayan ya gama shafa mai dinne kuma, ya saka wani wandon boxer ajikinsa.

Duk da sanyin da ake yi kuwa, haka ya nufi kan gadonsa ya kwanta, batare da ya saka riga ko rufe kyakkyawar surar jikinsa ba.

Kwanciyar rub da ciki yayi tare da jawo laptop dinsa, ya soma dannawa.

Acan b’angaren Jannart kuwa, Koda ta idar da sallan nata, kwanciya tayi akan gado, zuciyarta cike da nishadi, saboda duk wani damuwan dake zuciyarta ya kau, yau tayi waya da Abbanta da kuma su Mamy, taji komai yayi mata wasai.

Gyara kwanciyarta tayi, juyawan da zatayi ne kuma Idanunta suka sauk’a, akan wayar Rayyern da ta ajiye akan bedside drawer dinta wayar na kawo haske alamun kira.

Da sauri ta d’an dafe goshinta, saboda ita gaba daya ma ta manta da batun wayar.
Sanin da tayi cewar zai buk’aci wayarne, kuma yasa ta tashi daga kwancen, wasu takalman ta saka tare da miƙa hannu zata jawo wayar.
Garin hakane ta amsa kiran.
Juyo fuskar wayar tayi da niyar taga wake kira sai taga ashema ta amsa kiran.
Sabon number ne, da sauri ta kalli rubutun dake ƙasan number Ethiopia ta faɗa cikin nazari, alamun daga can kiran yake.
Kiran na gab da sinkewa ta amsa da addu'ar ko Riyyam-nsra ne,
Da sauri ta kara wayar a kunne jin muryar Riyyam-nsra yana cewa.
“Asssalamu alaikum, Hamma Rayyern”.
Cikin sakin fuska da jin daɗin tace.
“Wa alaikassalam Riyyim”.

“Lahh My Aunty”.
Riyyam-nsra ya faɗi cikin jin daɗi da so da mutuntaka.
“Na'am Riyyam-nsra yasu Mammy da Zaytoon.”

“Duk suna lfy, mu Aunty nayi kewarku, kullum ina son in kiraku bani da number ku Hamma

Radaman ɗan wulaƙanci sai yau ya turo min”.
Hanyar fita ta nufa tare da cewa.
“Allah sarki autan Mammy i miss u so much wlh”.
Cikin jin daɗi yace.
“wlh na fiku kewa gaba ɗaya yanzu Ethiopia ta daina min daɗi ma yaseen”.
Ya ƙare mgnar yana shiga falon Mammynsa.
Ita kuwa Jannart
murd’a handle din kofar tayi ta buɗe kana ta fito kaitsaye ta nufi dakinsa.
Suna masu ci gaba da mgn da Riyyam-nsra.

Ahankali ta murd’a handle din k’ofar d’akin nasa, tare dasa K’afarta ciki.
Cikin wani irin yanayi t...!

By
*GARKUWAR FULANI*
22/12/2021, 19:59 - 🥰🥰: Akan Barrister Kabir, Wanda shigowansa kenan cikin falon, duk da kuwa yaji abunda suke fadad’in amma saiya yi kamar bai ji komai ba.

Ganinsa da sukeyi dinne kuma yasa Dr Lukman da kuma Alhaji Abdu Tababa yin shiru, tare da soma kallon kallo atsakaninsu, Wanda kuma hakan alamace dake nuna zallan rashin gaskiyarsu.
Alhaji Bala tambari kuwa wani irin kallon ƙasa-ƙ’asa yakeyiwa Barrister Kabir ɗin mai kunshe da alamomi masu tarin yawa.

Alhaji Idi Sale daka ta kuwa wani kallo ya shiga yiwa k’anin nasa, irin kallonnan mai d’auke da ma’anoni daban daban.
Saidai kuma gudun kada Barrister Kabir din ya zargi wani abu, yasa Alhaji Idi Sale dakatan ya d’anyi gyaran murya yace.

“Barrister kazo adai-dai domin kuwa magana muke akan yanda zamu fad’ad’a kasuwancinmu, musamman company’s dinmu, way’anda ayanzu shareholders dinmu suka soma janyewa, badan komai ba kuma saidan sabon Companyn Mainasara  wanda ayanzu mafi yawan y’an kasuwa dake cikin jihar Kano, dama na sauran garuruwa, harda mak’otanmu, suka zuba hannayen jarinsu acikin companyn, Wanda hakan kuma bak’aramin tawaya ya kawo ga namu companyn ba.”

Ya k’arasa maganan a dai-dai lokacin da Barrister Kabir ya gama, k’arasowa cikin falon tare da neman waje ya zauna, akan d’aya daga cikin kujerun falon.

Ajiyar zuciya Barrister Kabir ya sauke, kafun ahankali ya d’ago ya soma kallon kowannensu d’aya bayan d’aya.

“Hakan yana da kyau tabbas, domin ni kaina nafahimci cewar, shareholders din companies dinmu sun soma ja baya, musamman kamfanoninmu na kayan masarufi.”

Ya ida maganar yana me kallon Dr Lukman da yake sharce gumin daya kwanta agoshinsa, Wanda kuma Gumi ne na tsananin rashin gaskiya da tashin hankali domin haka nan yake jin fargaba in ya kalli ƙwayar idon Barrister Kabir ɗin.

Alhaji Idi Sale Dakata kuwa, hannunsa yasa ahankali ya dafe zuciyarsa, cikin wani yanayi mai wuyar nazarta yace.

“Shin ka samu wani labari adangane da b’atan Jannart kuwa?”

Yanayin yanda yayi tambayar ne, yasa Barrister Kabir d’ago Kansa ya kalli Yayan nasa.

Tsawon mintuna biyu kafun ya girgiza Kansa, kana cikin nazartar fuskar yayan nasa yace.

“Babu wani labari akan b’atan Jannart, amma dai nasan y’an sanda na bayyane da kuma ss suna nan suna aikinsu akan hakan.”

“Allah yasa aganta, domin kuwa mahaifinta yana cikin tashin hankali da alhinin rashinta, kuma ganinta ne kadai zaisa ya warke daga wannan ciwon daya kamashi.”

Engineer Alkali Baba ya fad’i hakan, yana me kallon Alhaji Idi Sale Dakata.

Barrister Kabir kuwa Kansa ya sunkuyar, tare da sakin wani b’oyayyen murmushi.

Acikin ransa kuwa cewa yayi.

“Lallai watarana Gaskiya za tayi halinta tabbas, watarana fuskokin da suke dauke da murmushi ayanzu, sune wanda zasu kasance cikin bakin ciki da danasani mara amfani da tarin kunya.”

Da alama kuma su Alhaji Idi Sale Dakata’n, sun manta cewar da Lawyer suke tare, Wanda ko yaya aka fadi maganar daba gaskiya ba zai iya gane ta hanyar nazartan ko wanne harafi da ƙididdigansa filla-filla.

Daga haka kuwa Shirune ya biyo baya atsakaninsu, inda kowannensu ya kasance da abunda yake sakawa acikin zuciyarsa.

Musamman Alhaji Idi Sale Dakata, Wanda zuciyarsa ke ci gaba da tsara plan din dake yawo

acikin tunaninsa, shi kad'ai yasa tsarinsa haka kuma shi kad'ai yasan inda ya dosa.
Abubuwa uku dake cikin zuciyarsa lallai tabbas saiya cimmasu, koda kuwa hakan yana nufin rasa wasu rayukan.

Yayinda Dr Lukman kuwa babu wani abu dake sukar zuciyarsa akullum, face nasara da kuma d'aukaka had'i da cigaban da Dr Rayyern Bashir Muhammad Mainasara ke samu, musamman akan aikin likitancinsa.
Tabbas wuta ne keci a zuciyar Dr Lukman, Wanda ayanzu bashi da wani buri da ya wuce, kawar da Dr Rayyern a doron k'asa kamar yanda ya alk'awarta wa kansa, cewar watarana tabbas za'a wayi gari babu Dr. Rayyern Bashir Muhammad Mainasara.

Shi kuwa Barrister Kabir abunda ke cikin zuciyarsa, ingantaccene wanda ya tabbata watarana sai ya faru, matukar yana raye to Tabbas saiya Bayyana b'oyayyen sirrin da aka bunne tsawon shekaru.

*Ethopia*

Riyyam nsra.
Munafukan idanunsa da sukayi ja sosai ya lumshe, tare da sake gyara kwanciyarsa, kana ahkanli kuma ya sake tura hannunsa cikin mararsa.

Batare da an d'au koda minti daya ba kuma, ya sake bude idanun nasa inda ya sauke ganinsa, akan wata kyakkyawar yarinya wacce hoton videon ta ya cika gaban wayarsa.

Sosai yake kallon yanda yarinyar ke motsa duk wata gab'a najikinta da sunan wai rawa.

"Shonah!"
Ya karanta sunan da yarinyar ke amfani dashi, wacce kuma da dukkan alama musulmace, saidai wayewa da kuma rudin shaidan hadi da sharri da illan dake cikin TIKTOK yasa ta koma tamkar y'ar arna marassa tarbiya da al'k'ibballah.

Sake gyara kwanciyarsa yayi, tare da kurawa breast dinta idanu, kasancewar shatinsu ya fito ta cikin t-shirt din dake jikinta.
Duk da cewar yau yafara ganinta a TIKTOK din, amma tayi masa sosai, domin all videos dinta duk na banza ne, Dan ko sau d'aya babu inda ta saka kayan kirki wanda duk tawagar ibilasan TIKTOK d'in kanyi haka wai dan a samu Follower dan yin tutiya da al'ummar da zasuyi ta ingiza su ga hanyar halaka mai fad'i musu gsky suyi mishi taken Allah ka aika munafukinmu can nesa... Sun mance daga bakin magautanka ko mahasadanka kake saurin gane kurenka har ka gyarashi in kana da shi ɗin in kuwa hasadace kawai tasa a sukeka ko a ɓatanci gareka to ai su mahasada gishirine na ci gaban rayuwan ɗan Adam, domin idan Ubangiji yayi nufin ɗaukaka wani bawa nasa to a harsunan magautanka mahasadansa zai ɗaukaka shi!

Bio dinta daya karanta ne kuma yasa shi, following dinta saboda yaga tasa tutar Nigeria, Wanda

kuma hakan alamace dake nuna cewar y'ar Nigeria ce.

Take kuwa yaga tayi following dinsa back, before 10 second kuma saiga DM dinta ya shigo wayarsa sabida ganin sunanshi yayi following nata kawai ya isheta abin al'fahari domin sanuwarsa da shuhurarsa ya wuce zaton mai zato.

Idanunsa yad'an zazzaro take kuma yasaki wani irin shu'umin murmushi, ko kusa baikawo aransa cewar zatayi accepting nasa haka ba dan shi kansa yaga kanta yana hayak'i shaidan na kad'a mata tana juyawa da bin linzaminsa.

Shiga cikin DM din nata yayi, inda ta rubuta masa sak'o kamar haka.

"Hey handsome how are you?".
Inda akarshen rubutun tasa masa wani d'an banzan Emoji dake nuna kwarewarta a iskanci.

Ganin emojin ne kuma yasa Riyyam sake sakin murmushi, cike da shauki ya rubuta. "Sexy." tare da tura mata, Dan yasan zata fahimci abunda yake nufi dan yasan mafi akasari duk kanwar jace, tabbas akwai na gari a TIKTOK amman basu da yawan watsastsun more especially in akayi duba da shigar mutun da kalamansa sabida mafi aksarinsu tawagar TIKTOK sun zama tamkar rainon karnuka.

Aikuwa take tafahimta.

"You want?"

Ya karanta sakon da ta turo masa, inda jikinsa na b'ari yayi mata reply da.

"Yeah I want."

Emojin murmushi ta turo masa, take kuma saiga wasu bad videos dinta sun shigo wayar tasa, tare da message na "Where are you living?"

"Oh My God she's hot"

Riyyam din ya fada da d'an karfi, tare da zaro harshensa ya lashi labb'ansa, tare da kurawa videon da yake kallo din idanu.

Yanda yaga yarinyar naked ya masifar tayar masa da hankali, take yaji yanason yin video call da ita.

Hakan yasa cikin gaggawa ya tura mata number dinsa, tare da sawa ta turo masa nata.

Da hanzari yayi dialing numbern nata to face time.

Dai-dai lokacin kuwa Zaitoon ta turo kofar dakin nasa, bakinta dauke da sallama.

Amatukar zabure ya kifa wayartasa, tare da juyowa yana kallon Zaitoon din, da munafukan idanunsa na rashin gaskia.

Itama Zaitoon din kallonsa tayi, ganin da tayi duk yana zabure ne kuma yasa ta, watsa masa harara tare da cewa.

“Are you okay?”

“Yea I’m okay, mekika shigoyi dakina?”

Riyyam din ya tambayeta yana me hade fuska, tare dayin rau rau da idanunsa.
Alamun dai rashin gaskiya.

“Oho mezanzo nayi ad’akin dan rawan TIKTOK? Mammy ne tace nazo nakiraka.”

Zaitoon din ta fada tana me hararansa, batare kuma da tajira maizaice ba, ta juya tayi tafiyarta.

